# TAKAICIN MATA A FINA-FINAN HAUSA

**NA**

**BINTA MUSA HASSAN**
**M.A /ARTS/ 07307/2008-2009**

**SASHEN HARSUNAN AFIRKA DA AL'ADU**

**JAMI'AR AHMADU BELLO, ZARIYA.**

# TAKAICIN MATA A FINA-FINAN HAUSA

**BY**

**BINTA MUSA HASSAN**
**M. A /ARTS/ 07307/2008-2009**

**THESIS SUBMITTED TO THE POSTGRADUATE SCHOOL**
**AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA NIGERIA**
**IN PARTIAL FULFILMENT FOR THE AWARD OF MASTER**
**OF**
**ARTS AFRICAN LANGUAGES (HAUSA)**
**DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES,**
**AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA, NIGERIA**

## DECLARATION

**I hereby declare that the work in the thesis entitled 'TAKAICIN MATA A FINA-FINAN HAUSA' has been written by me in the Department of African Languages and Cultures under the supervision of Dr. Muhammad Lawal Amin and Dr. Ramlatu Jibir Daura. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. This thesis has not been presented for a higher degree or diploma at any university.**

**------------------------- --------------------- -------------------**

**Binta Musa Hassan Signature Date**

## CERTIFICATION

**This thesis** entitled 'TAKAICIN MATA A FINA-FINAN HAUSA' written by Binta Musa Hassan, meets the regulations governing the award of the degree of Master of Arts (African Languages) Hausa, Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria and is approved for its contribution to knowledge and literary ~~presentation.~~---------------------

Dr. Muhammad Lawal Amin
Chairman, Supervisory Committee

--------------------------------------

Dr. Ramlatu Jibir Daura
Member, Supervisory Committee

-------------------------------------

Dr. Balarabe Abdullahi
Head of Department

----------------------------------

Prof.A.A.Joshua
Dean, Postgraduate School

## SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan kundi ga mahaifiyata marigayiya Zainab Sharif Abdu da kuma mahaifina marigayi Sharif Abdu Abubakar. Da fatan Allah (S.W.T.) Ya yi musu rahama, Ya sa su a Aljannar Firdausi, Amin.

**GODIYA**

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah maxaukakin sarki, wanda Ya halicce ni ya kuma qaddaro rayuwata har na sami kaina a wannan matsayi na kammala wannan kundi na neman digiri na biyu a fannin da ya shafi rayuwar mata a jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Ina fara miqa godiyata ga iyayena Alhaji Sharif Abdu Abubakar da Hajiya Zainab da suka tarbiyyantar da ni da saka ni makaranta da kulawa da karatuna, har na kawo zuwa wannan matsayi, Allah Ya jiqansu, Ya biya su da Aljannar Firdausi, Amin. Sai kuma babban yayana Salihu Zangina wanda shi ma ya ba da gudummawa mai yawa wajen karatuna, shi ma Allah Ya yi masa rahama.

Godiya ta musamman ga Dr. Muhammad Lawal Amin da Dr. Ramlatu Jibir Daura waxanda su ne suka xauki xawainiyar dubawa da kuma yin gyare-gyare a farkon wannan aiki. Sannan sun taimaka da shawarwari da suka sa aka sami sukunin kammala wannan aiki, na godewar hadaga taskiya misaltuwa ba gare ni ga mai duba wannan aiki na cikin gida, wato Dr. Balarabe Abdullahi wanda ya taimaka da bayanai da shawarwari masu amfani, Allah Ya saka masa da alkhairi, Amin.

Ina kuma miqa kyakkyawar godiyata ga maigidana Malam Musa Hassan Aikawa bisa ga qwarin gwiwa da taimako da fahimta da ya ba ni tun daga farkon karatuna har zuwa yau. Allah Ya saka masa da alkhairi, ya kuma bar mu tare, Amin.

Haka kuma ina miqa godiyata da addu'a ga marigayi Dr. Abdullahi Garba Wurma wanda shi ne ya yi sanadiyar zuwa na karatu wannan jami'a. Allah Ya gafarta masa, Amin.

Bayan haka akwai ximbin jama'a da suka taimaka yayin gudanar da wannan aiki ta hanyoyi daban-dabam kamar su marigayiya Malama Rabi Garba, Allah Ya yi mata rahama; da Malama Hauwa Muhammad Bugaje da dukkan malaman Sashen Harsuna da Al'adun Afirka na wannan jami'ar. Da kuma dukkan abokan aikina na Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso. Kano.

Haka kuma ba zan manta da 'ya'yana ba da suka jure wa barin su da nake yi a gida na tsawon lokuta, don yawon karatu da bincike na wannan aiki, Allah Ya yi musu albarka, Ya ba su ilimi mai amfani, Amin.Ba zan kammala ba sai na miqa godiyata ga Isma'ila Bello Bature da Muhammad da dukkan ma'aikatan Gidan Mambayya, saboda irin taimakon da suka ba ni a kan wannan aiki.

Daga qarshe ina miqa godiya ga dukkan yayyena da qannena da ‘yan’uwana da abokan arziki, Allah Ya saka wa kowa da alheri, amin. Allah kuma Ya sa aikin ya zama mai amfani ga al’umma gaba xaya, amin.

# TSAKURE

Tun zamani mai tsawon gaske, an sami mata da suka yi rubuce-rubuce, suka bayyana yadda matsayin mace yake tun a wancan lokaci. Ire-iren waxannan mata sun dubi matsayin mace ta fuskar al'ada da addini da siyasa da ilimi da tattalin arziki da zamantakewa da sauransu vangarorin rayuwa, inda bayanansu suka fito da cewa duk a waxannan vangarori na rayuwa mace ta kasance qasqantacciya kuma rarrauna, har wasu ma ke xaukar ta ba 'yar'Adam ba ce. Ganin wannan bincike ya faxo cikin wannan fage na irin takaicin da mata ke fama da shi a rayuwa ya sa aka shiga cikin duniya[illegible] da niyyar fito da abubuwan da ke sa mata  shiga halin quncin rayuwa da xauki fina-finan Hausa a matsayin madubi da suka hasko waxannan abubuwa. An yi haka ne saboda an hangi wani givi da ke akwai a bincike-bincike da nazarce-nazarcen  ayyukan da suka shafi mata da fina-finan Hausa. Mafi yawan manazarta sun fi bai wa ayyukan da maza da sauran sassan adabi muhimmanci, duk kuwa da cewa su akwai abin da ya kamata a binciko a kansu. Sannan su ma fina-finai

matsayinsu na wani vangare na adabin Hausa xauke suke da abin da rayuwar al'umma musamman mata.

Domin daidaita binciken an dubi yadda addinai da al'adu daban-dabam ke kallon matsayin mata a zamanin jahiliyya har zuwa wannan qarni. Haka kuma an kawo matsayin mata da irin gudummawar da suke bayarwa a vangaren shirya fina-finan Hausa.

Domin fito da fasalin binciken fili an kawo bayanai game da samuwar fina-finan Hausa. Sannan aka kawo bayanai dangane da kalmar takaici da nau'o'insa. Haka kuma an kawo abubuwan da ke jefa mata cikin takaici da suka haxa da zamantakewa tsakanin miji da mata da kishi tsakanin kishiyoyi da kishi tsakanin faccaloli (kishiyoyin sauri) da kuma tsakanin da suruka da sarakuwa, sai kuma rashin haihuwa da haihuwar 'ya'ya mata . Sannan kuma an kawo yadda fina-finan Hausa suka nuna yadda yara mata kan shiga qunci da takaici a sauran al'amuran rayuwa, kamar a sanadiyyar auren dole da irin yadda matar uba ke quntata wa 'ya'yan miji, da kwaxayi da son abin duniya da kuma yadda maza kan yaudari matan su saka su cikin takaici

## Abstract

For a long time there have been women who have written a lot about the situation of women. Some of these women writers used many dimensions in looking into the problems of women, some look into the problem from cultural, religious, political, educational, economic, social and other aspects of life. Using the above factors, the position of women is at the lowest ebb, in fact in certain areas women are even considered as sub-human. Consequently, since the research is gender oriented towards understanding the vexation of women in Hausa films, it is vital to delve into history so as to place the research on its proper base.

Feminist's views are taken into consideration in order to find out the factors that push women into these difficult conditions. In this research Hausa films are taken as a case study. These films have portrayed the difficult conditions into which women have found themselves. Hausa films were taken as a case study, because of the gap into research in the position of women in Hausa films. Most of the researchers have concentrated on male and other literary genres despite the fact that researches on women are needed. Even Hausa films as literary genres deal with some social problems especially those dealing with women.

To make the research balanced, the work probes into so many areas like feminist's views and historical situation of women's rights from the ignorant (jahiliyya) period to the present century. Furthermore, the role and contribution of women to the development of Hausa films are taken into consideration.

To achieve the set goal, the research looks at how Hausa films emerged. Then information is provided on the meaning of vexation and its genres. Moreover, the factors that throw women into difficulties such as the co-existance among married couples (husband and wife) and rivalry between co-wives, among mother-in-law and daughter in-law and between sisters-in-law.

Finally, information is provided from the Hausa films on how girls fall into trouble or difficult conditions in their lives.

## Qunshiya

Taken Bincike------------------------------------------------------------------I

Declaration------------------------------------------------------------------ II

Certification-----------------------------------------------------------------III

Sadaukarwa-----------------------------------------------------------------IV

Godiya---------------------------------------------------------------------- V

Tsakure----------------------------------------------------------------------VIII

Abstract-------------------------------------------------------------------- X

### Babi Na Farko: Shimfixa

1.0.Gabatarwa--------------------------------------------------------------1

1.1.Tarihin Samuwar Fina-Finan Hausa-------------------------------7

1.2. Dalilin Bincike------------------------------------------------------ 13

1.3. Manufar Bincike-------------------------------- ----------------------14

1.4. Muhimmancin Bincike-------------------------------------------- 15

1.5. Iyakar Bincike------------------------------------------------------16

1.6. Hanyoyin Gudanar da Bincike--------------------------------------17

1.7.Naxewa-----------------------------------------------------------------22

### Babi Na Biyu: Ayyukan Da Suka Gabata

2.0. Gabatarwa------------------------------------------------------------24

2.1.1 Matsayin Mace Kafin Bayyanar Musulunci-------------------- 25

2.1.2. Matsayin Mace Bayan Zuwan Musulunci--------------------- 30

2.1.3. Matsayin Mace A Zamanin Yau (2012)------------------------33

2.1.4. Matsayin Mata Da Gudummawarsu A Fina-Finan Hausa---35

2.2. Nazarce-Nazarce A Kan Fina-Finan Hausa-------------------- 38

2.2.1. Littattafai------------------------------------------------------------ 38

2.2.2. Kundayen Bincike---------------------------------------------------39

2.2.3. Maqaloli/ Mujallu-------------------------------------------------- 45

2.3. Nazarce-Nazarce Dangane Da Mata-----------------------------50

2.3.1 Littattafai-------------------------------------------------------------- 50

2.3.2 Kundaye-----------------------------------------------------------------55

2.3.3. Muqaloli/ Mujallu---------------------------------------------------61

2.4. Kammalawa-------------------------------------------------------------64

**Babi Na Uku: Takaicin Mata A Zamantakewar Iyali**

3.0. Gabatarwa------------------------------------------------------------66

3.1. Ma’anar Takaici------------------------------------------------------- 66

3.2. Nau’o’in Takaici-------------------------------------------------------67

3.2.1. Fushi-------------------------------------------------------------------67

3.2.2. Haushi---------------------------------------------------------------- 69

3.2.3. Qunci---------------------------------------------------------------- 69

3.2.4. Wulaqanci----------------------------------------------------------- 70

3.3. Takaicin Mata A Zamantakewar Iyali------------------------------ 71

3.3.1 Yanayin Zamantakewa Tsakanin Miji Da Mata---------------- 72

3.3.2 Kishi------------------------------------------------------------------- 81

3.3.2.1 Kishi Tsakanin Kishiyoyi---------------------------------------- 84

3.3.2.2 Kishin Uwar Miji----------------------------------------------- 92

3.3.2.3 Kishin Sauri/Faccala---------------------------------------------- 101

3.4. Rashin Haihuwa------------------------------------------------------106

3.5. Haihuwar 'Ya'ya Mata---------------------------------------------- 112

3.6. Kammalawa----------------------------------------------------------- 118

**Babi Na Huxu: Takaicin Yaran Mata**

4.0.Gabatarwa----------------------------------------------------------120

4.1. Kwaxayi Da Son Abin Duniya---------------------------------------120

4.2. Quntatawar Matar Uba Ga 'Ya'yan Miji-------------------------- 125

4.3. Auren Dole---------------------------------------------------------------130

4.4. Yaudarar Samari Ga 'Yammata---------------------------------------137

4.5. Kammalawa----------------------------------------------------------- 142

**Babi Na Biyar: Naxewa**

5.0 Gabatarwa---------------------------------------------------------------143

5.1. Kammalawa------------------------------------ --------------------- 143

5.2. Shawarwari-------------------------------------------------------------150

Manazarta------------------------------------------------------------ 152

Rataye------------------------------------------------------------------ 164

## BABI NA FARKO : SHIMFIXA

### 1.0 Gabatarwa

Masana adabin Hausa sun yarda kalmar adabi ta samo asali ne daga harshen Larabci (Yahaya 1973 da Xangambo 1985 da Gusau 1991 da sauransu). Daga Larabci kalmar ita ce adab ko adb (tilo) ko d'ab (jam'i) wasu kuma suna ganin daga addaba (tilo) ko adab (jam'i) aka sami asali na kalmar. A Larabce, ta hanyar lugga, kalmar na iya zama: fasaha, qwarewa, halaye kyawawa, shirya liyafa da sauransu (Gusau, 2011). A wajen Hausawa, manazarta adabin Hausa sun bayyana ma'anar adabi ta fannin ilimi ta hanyoyi daban-dabam, misali, Yahaya (1973) ya ce adabi:

> "Adabi wata babbar hanya ce da xan'Adam yake yin amfani da ita don ya sadar da abubuwan da suka shafi rayuwarsa da ta 'yan'uwansa (iyali ko dangi ko qasarsa) ga su 'yan'uwan ko wasu dabam. Abubuwan da yakan bi ya sadar xin nan kuwa sukan shafi wani abu ne da ya daxaxa masa zuciya ko wanda ya sosa masa rai ko wanda ya shafi siyasa ko addini ko wayar da kai wato ilimi".

Adabi abu ne qagagge, tsararre a kan wani tunani na musamman da gabatar da shi da harshe mai zalaqa. Ashe shi adabi zubi ne mai jan

mai daxi, wani lokaci kuma mai xaci, mai bayyana farin ciki ko ban ko ban takaici. Abu ne mai jefa jin daxi ko tsoro, ko sanya nadama ko ko gamsuwa ko girsuwa. Haka kuma yakan qunshi kwaikwayo a sauwara tunani ta yadda za a tsara aukuwar wani abu ko a yi faruwarsa. Matanonin adabi suna yi wa rayuwa hannunka-mai-sanda koyar da darussa iri-iri da yin ishara da nuni cikin nishaxi ta yadda za mutane bisa rayuwa tagari kuma a shiryar da su zuwa ga tafarkin (Gusau, 2011: 5-6). Adabin Hausa ya yi ta samun qare-qare waxanda nashewa su haxe su zama xaya. Waxannan qare-qare da adabi ya same su ne a dalilin shigowar manyan al'ummun nan guda biyu, wato Larabawa a wajen qarni na 13 zuwa na 14 da kuma Turawa a wajen 19.

Daga cikin abubuwan da adabin Hausa ya qaru da su ya kuma gaba a kai, sun haxa da fim. Shi kuwa fim ya samu ne a sanadiyyar ci da wasan kwaikwayo. Bisa al'ada, duk wani abin da za a gudanar, musamman abin da ya shafi adabi, ko na waqa, ko zube ko wasan kwaikwayo, ya dace a ce yana da dalili ko sanadin yin sa. Domin su bayyana halayyar al'ummarsu ta hanyar lura da abubuwan da ke cikinta, su kuma yi qoqarin faxakar da sauran jama'a. Fina-finan

Hausa ba wai hakanan kara-zube ake yin su ba, akwai manufa da kuma hujja da

ta sa ake yin su. Halayyar da al'umma suka kasance ciki ita ke yin tasiri a cikin fina-finansu. Wato masu shirya fina-finai za su xauki wani hali da al'umma ta sami kanta ciki idan mai kyau ne su nuna hakan, idan ma aka sami akasin haka, haka za su bayyana, don yin kira ga al'umma da a yi gyara.

Kowace al'umma ta duniya tana da wasu tanade-tanade da tsarabe-tsarabe da ta yi domin tafiyar da rayuwarta ta yau da kullum, waxannan tanade-tanade su ke jagorancin yadda rayuwa baki xaya za ta kasance tun daga haihuwa har tsufa zuwa mutuwa. Waxannan abubuwan sun shafi xabi'u da al'adu da tarbiyya da zamantakewa da kuma al'amarin ci gaban al'umma, kamar neman ilimi da sha'anin siyasa da aure da haihuwa da sauran al'amauran rayuwa na yau da kullum.Waxannan al'amuran zamantakewa da na ci gaban al'umma dogara ne bisa irin matsayin da al'umma ta ba mace. Saboda Allah shirya cewa rayuwa ta duniya da lahira ba ta namiji ne shi kaxai ba, mace da namiji ce su biyu. Hasali ma dai ita rayuwa ba ta yiwuwa sai haxuwar biyun, domin rayuwar duniya kamar tsuntsu ce, da mace da

su ne fuka-fukansa guda biyu. Don haka idan al'umma ta ba mace kula da ita, ta kuma mutunta ta, to sai al'ummar ta ci gaba, kuma yi daxi, domin idan mata suka sami natsuwa, tarbiyya za ta inganta, mata su ne tushen tarbiyya. Idan kuwa aka sami akasin haka, to sai ta ci baya kuma a sami tavarvarewar tarbiyya.

Tun a da can har zuwa yanzu mata ba su da ta cewa, wai varawo a hannun mata. Matan sun daxe suna cikin quncin rayuwa da matsi da takura da shiga halin qaqa-nika-yi. Duk da cewa su ne iyayen al'umma kuma mataimakan mazan a fannonin rayuwa daba-dabam, amma kuma ana xaukar su kamar qananan yara, wani lokacin ma ana xaukar su kamar bayi, suke fuskantar azaba iri-iri da wahalhalu, daga qarshe kuma, a yi watsi da su (Badamasiy, 1998 : 1). Tsawon lokuta mata sun sha gwagwarmaya domin yunqurin fitar da kansu daga cikin quncin rayuwa. A qasashen yamma, kamar Faransa da Birtaniya an yi ta samun mata 'yan gwagwarmaya, waxanda suka fi mai da hankali wurin ganin mata sun sami 'yanci, musamman daidaito ga haqqinsu, da ba wa mata 'yancin mallakar dukiya da ba su damar samun albashi daidai da maza da 'yancin jefa quri'a da sauransu.

A qasashen Hausa ma, an xauki mata a matsayin raunana, ba a cika ba su ilimi ba . Kuma al'umma sun amince maza su ne ke jagorancin komai, domin Musulunci ma maza ya ba shugabanci. Kamar yadda ya zo a cikin Al-qur'ani mai girma:

> "Maza masu tsayuwa ne a kan mata, saboda abin da Allah Ya fifita sashensu da shi a kan sashe, kuma saboda abin da suka ciyar daga dukiyoyinsu……."(suratu Nisa'i aya ta 34)

A vangaren gida maigida shi ne da iko a kan kowa da komai na gidan, duk yadda ya ce, haka za a yi. A fagen sana'a ma, maza ne suka mamaye, domin suke yin mafi yawancin sana'o'i. A fagen mulki da sauran abubuwan rayuwa maza ne kan gaba, su mata na kulle a gida, suna bautar aure. Wannan matsayi na mata ya taimaka wajen barin su a baya, da kuma xaukar su a matsayin raunana a cikin al'umma. Har ma ana ganin mace ba ta iya fitar da kanta daga matsala balle ta fitar da wani, duk kuwa da cewa ba dole ne hakan ya kasance ba, shi ya sa wasu ke cewa sai mace ta kai shekara arba'in sannan qwaqwalwarta ke kai matsayin ta tunkiya, wanda wannan an san irin takun saqar nan ne da ke aukuwa tsakanin jinsuna, ba wai don haka tabbas ba ne (Ibrahim, 2009 : 19).

Akwai nau'o'in zamantakewar al'umma daban-dabam da suka haxa da zamantakewar miji da mata da zamantakewa tsakanin kishiyoyi da ta tsakanin suruka da sarakuwa da tsakanin faccaloli da makamantansu. A irin wannan zamantakewa wani lokaci akan sami 'yan rigingimu da hatsaniya da kan faru tsakanin mutanen da ke zaune da juna. A sanadiyyar haka, wani lokacin akan jefa matar da abin ya [illegible] suna da yawa, kaxan daga ciki su ne, yanayin zamantakewa tsakaninsu da mazaje, da kishi da rashin haihuwa da haihuwar 'ya'ya mata da auren dole da quntatawar matar uba da kwaxayi da yaudara. Waxannan abubuwan takaici su za a duba a wannan aiki.

Abubuwan da ke jefa mata cikin takaici.

Ganin cewa akwai bambancin da kan wanzu tsakanin jinsin namiji da jinsin mace ta vangaren matsaloli ko abubuwan da kan sa su takaici, binciken ya ga ya dace a fara da fahimtar yadda wannan taqaddama ta jinsi ta samo asali, da yadda take taimakawa wajen gina rayuwar mata.

Kalmar jinsi ta samo asali daga harshen Larabci. Daga kalmar ita ce jinsu ko al-jinsu (tilo), ajnas ko junus (jam'i). A Larabce, kalmar na nufin dangin wani abu, wato kalmar jinsun ta fi kalmar Nau'i kaxan ne daga jinsun. Haka kuma, ana cewa mujanasa wato,

kamanceceniya ko dangantaka, sannan ana cewa tanjiinsun wato dangantakar wani abu da wani ko kuma a kamanta su (Ar-razi :101). wasu malamai kamar na falsafa idan suka ce jinsi suna nufin tarin masu nau'i daban-dabam, misali dabbobi, jinsi guda ne, a cikin jinsin kuma za a iya ware wani nau'i, misali, jinsin mutum ( Al-Wasid :140).

A harshen Hausa kuwa jinsi shi ne fanni ko iri ko bambancin halitta (Bargery, 1934: 506). Ko bambancin mace da namiji ko kuma bambancin mace da namiji na kalmomi a Nahawu (Qamusun Hausa, 2006).Maganar jinsi ta wuce bambancin halitta kawai, ta haxa da bambance-bambancen da ake samu ta vangaren abubuwan da al'umma ke shatawa a al'adance a kan yadda ya kamata mata ko maza su kasance. Haka kuma, waxannan qa'idojin sun shafi kowane vangare na rayuwa, kamar yanayin zamantakewa na yau da kullum da makamantansu. Har wa yau, waxannan tsare-tsare na al'ada su ne suke haifar da matsalar xaukakar wani jinsi a kan wani ko danniyar da ake yi wa jinsin mata a cikin wata al'umma. Haka kuma ana bayyana jinsi a matsayin tsare-tsaren al'umma a kan xabi'u da ayyuka da matsayin da ake ganin ya dace da maza da waxanda suka fi dacewa da mata (Riley, 1997 : 2-6).

Jinsi abu ne wanda mutum kan iya zava wa kansa (De Beauvair, 1949). Wato irin rayuwar da mutum ya zavar wa kansa ita ce ke nuna jinsinsa, ba yadda aka halicce shi ba.

Duk idan aka haxa ra’ayoyin masana dangane da ma’anar jinsi, wannan bincike zai iya cewa, jinsi na nufin bambancin da ke akwai tsakanin namiji da mace ta fuskar halitta da kuma bambancin rawar da kowane vangare yake takawa ta fuskar al’ada da xabi’a da wasu vangaren rayuwa.

Wariyar jinsi kuwa, ta wanzu ne a sanadiyyar ra’ayi ko aqidar cewa, akwai bambanci ko fifiko tsakanin namiji da mace a cikin (Jennifer, 1985: 6). Daidaiton jinsi kuwa, bai wuce bai wa mata damar kamace su ba, domin su sami ‘yancin kai a fagen ilimi da kiwon lafiya siyasa da sha’anin gudanar da rayuwa na yau da kullum, da kuma faxa a ji (Ibrahim, 2009 : 2). Alal haqiqa, jinsin mata na da matuqar muhimmanci a tsakanin al’umma waxanda kusan ma iya cewa, mutum ba ta yiwuwa sai da mace. Kuma sai da macen al’amuran sukan tafi yadda yake buqata. Ya zama dole sai da mace gida yakan gida, sannan namiji yakan cika namiji. Don haka ne ma ake yi wa kirari da ‘mata iyayen giji, in ba ku ba gida, in kun yi yawa gida ya suka fi bayar da gudummawa ga al’umma musamman ta vangaren

yara. Su suka fi xaukar kaso mafi yawa wajen xawainiya da sadaukar tare da yin qoqari wajen tarbiyya. Shi ya sa ma aka ce idan an mace xaya, tamkar an ilimantar da al'umma ne.

Saboda la'akari da irin muhimmancin da mata ke da shi a wajen shekarar 1960 zuwa 1975 Majalisar  Xinkin Duniya ta vullo da wani shiri mai taken 'shekarar mata'. Sannan aka yi wani babban taro wanda yake shi ne irinsa na huxu da aka tava yi a kan mata duk duniya, a birnin Beijing na qasar Sin, wanda aka yi masa laqabi da 'Taron Beijing' a shekarar 1995, wanda ya sami mahalarta daga ko'ina cikin duniya, ya kuma yanke shawara a kan sha'anin daidaita jinsi na in-ba-ka-yi-ba-ni-wuri. Tun daga wannan taro ne maganar daidaiton jinsi take a bakin kowa; 'yan jarida ne ko masana ko manazarta ko ma-duba (Ibrahim, 2009: 41).

Wannan kace-na-ce da ake yi kan wariyar jinsi, shi ya sa wannan bincike ya xauki wani fanni daga cikin abubuwan da suka shafi mata don gudanar da bincike a kansa, ta yadda binciken kan iya bayar da gudummawa a kan abin da ya shafi rayuwar matan Hausawa.

## 1.1 Tarihin Samuwar Fina-Finan Hausa

Fim tantagaryar kimiyya da fasaha ce kuma rayuwar xan'Adam ce ake nunawa. Fim yana xauke da tarihi da xabi'un jama'a da muhallinsu da abincinsu da kuma suturarsu musamman bisa harshensu da tsarinsu na rayuwa da hanyoyin tunaninsa da kuma falsafar rayuwar mutanen da ake yin fim xin don su. Har ila yau, fim hanya ce ta sanarwa da ilimantarwa da jan hankali da nishaxantarwa da faxakarwa da yaxa manufa da tallatawa (Gidan Dabino da wani, 2004: 332).

Babu shakka, za a iya cewa fina-finan Hausa 'yan bana-bakwai ne, idan aka kwatanta su da sauran fina-finan, musamman na Turanci da na Canis. Domin farkon samuwar fina-finan Hausa abu ne da ya faru a qarshen qarni na 20. Amma tun farkon abin da ya xora tubalin samuwar fina-finai shi ne wasan kwaikwayo. Shi kuwa wasan kwaikwayo ya samu ne bayan Turawan mulkin mallaka sun zo, sun kafu, sun kuma yi nisa wajen shimfixa tsare-tsarensu da suka shafi mulki da ilimi da sauransu (Hausawa, 2009).

Tun kafin zuwan Turawa, Hausawa suna da nasu hanyoyin da na gargajiya da suke aiwatarwa ta fuskoki daban-dabam. Haka kuma wasannin gargajiya masu tarin yawa da suke qunshe da kwaikwayon halayyar rayuwar Hausawa da xabi'unsu. Ire-iren waxannan wasanni

haxa da wasan tashe da wasan gauta da wasan kalankuwa da da kuma wasan bori (Adamu, 2002).

Bayan wasannin kwaikwayo na gargajiya, an sami rubuce-rubuce na zube da waqoqi bayan zuwan Turawa a qarni na 20. Wasan kwaikwayo shi ne ya zo a makare, amma bincike ya nuna an sami rubutaccen wasan kwaikwayo na farko a cikin tsohuwar hanyar rubutun Hausa na Muhammadu Agigi na Haji Ahmad Muskwani, Kano a shekarar 1902 (Abbas, 2008 : 44).

Majigi shi ne hoton farko da Hausawa suka fara cin karo da shi kafin sauran hotuna da ake nunawa. An fara nuna majigi ta hanyar sanya allon kallo a saman mota (Bargery, 1934). Hotuna ne masu motsi da ake nunawa a farin bango ta hanyar harba su da wata na'ura ta wutar lantarki mai hasken gaske (Qamusun Hausa, 2006).

Hoton majigi na farko da aka fara nuna wa Hausawa shi ne na *Larai*, wanda ma'aikatar yaxa labarai ta Arewa ta shirya a shekarar domin wayar da kan Hausawa a kan noman zamani, musamman da gwamnatin wancan lokaci take so a noma, kamar gyaxa da cikin shirin aka nuna Baban Larai ya yi amfani da shawarwarin gona ya noma gyaxa kuma ta yi kyau sosai inda ya sayar ya sami

kuxi masu yawa. Kuma mutanen qauyensu suka yi koyi da shi (Inuwa, 2009).

Daga nan sai Ma'aikatar Yaxa Labarai ta Arewa ta ci gaba da nuna wa jama'a majigi, inda aka nuna majigin *Xan'arewa a London*. Wannan majigi an shirya shi ne domin wayar wa da 'yan Arewa kansu, kan yadda za su zauna a London, idan sun je kwas ko karatu. A cikin majigin an nuna yadda za su gudanar da rayuwarsu da kuma yadda za su yi hulxa da wasu mutane da ba su saba da su ba, sannan aka nuna musu yadda za su zauna da waxannan mutane cikin kwanciyar hankali da lumana.

Sai kuma majigin *Shaihu Umar* wanda Ma'aikatar Yaxa Labarai ta shirya a shekarar 1976 domin nuna wa mutanen Afirka a bikin nuna al'adun baqaqen fata, wasan asalinsa rubutun zube ne aka mayar da shi majigi kuma shi ne majigi na farko da aka tava yi mai tsawo da ya xauki sama da awa xaya, sannan ya qayatar da gaske (Chamo, 2005: 36).

Daga nan kuma sai majigin *Kulva Na Varna* da Umar Xanjuma rubuta, sai kuma majigin *Magana Jari Ce* da Abubakar Imam ya Duk su ma rubutun zube ne aka mayar da su majigi. Ire-iren hotunan majigi su suka ja hankalin sarakuna da talakawan gari suka

sha'awarsu ta kallon hoton majigi domin koyon kiwon lafiya da noma sauran al'amuran duniya.

Kamar yadda bayani ya gabata, duk waxancan fina-finai an nuna su ne ta hanyar majigi. Daga 1980 zuwa 1990 an sami bunqasar qungiyoyin wasannin kwaikwayo na dave a manyan birane suna nuna wasan kwaikwayo ana xauka ana nunawa a gidajen talabijin na tarayya da ke jihohin Arewa kafin a sami gidajen talabijin na jihohi. Misali an yi su *Tambari* da *Karambana* waxanda qungiyar su Qasimu Yero take shiryawa da *Samanja Mazan Fama* wanda su Usman Baba Pategi (Samanja) da *Idon Matambayi* daga Sakkwato da *Qarquzu na Bodara* daga Jos da *Gaskiya Dokin Qarfe* daga Maiduguri da *Taskira* da *Karo da Goma* da *Ba'are duk* daga Kano, dukkan waxannan shirye-shirye ne a NTA da suka sami karvuwa sosai a wajen Hausawa musamman saboda faxakarwa da nishaxantarwa da suke yi wa al'umma.

A wajen qarshen shekarar 1990 aka fara nuna wasannin waxanda suka shafi zamananci. A CTV 67 Kano an nuna *Bakan Gizo Hadarin Qasa* da *Farin Wata* waxanda ma'aikatan talabijin ne suka su. Vullar waxannan wasanni da karvuwarsu a wurin jama'a a Kano

tunanin mayar da wasan kwaikwayo sana'a. Kuma, daga nan ne aka shirya wasanni a kaset-kaset na bidiyo ana sayarwa, kuma daga lokaci ne aka fara amfani da kalmar fim.

Daga nan, sai qungiyoyin marubuta littattafai da na wasan kwaikwayo na dandali da na motsa jiki (kareti) suka yi hovvasa, inda suka fara jarraba shirya fim ba tare da wasu ma'aikata qwararru ba. Irin waxannan qungiyoyi sun haxa da qungiyar wasan kwaikwayo ta **Gyaranya** da **Black Eagle** da **Dynamic Fighters** da **Tumbin Giwa** da sauransu. Qungiyar Tumbin Giwa ta gudanar da fina-finai guda biyu a Kano. Xaya an yi shi ne da sigar fim xin qasar Sin wato China, wato ta faxace-faxace, xayan kuma an yi shi kamar na Indiya wato yadda suke rawa da waqa amma dukkansu an yi su da Hausa ne (Inuwa, 2009).Sannan an sami kamfanonin shirya fina-finai irin su qungiyar Giwa ta shirya fim mai suna *Turmin Danya*. Kamfanin Kwabon Masoyi suka shirya fim mai suna *Kwabon Masoyi* a 1993, sannan a shekarar suka sake shirya *Gimbiya Fatima*. Daga nan sai kamfanin Gidan suka shirya *In da so da qauna* a shekarar 1994. Haka kuma akwai qungiya a Birnin Kudu wadda ta shirya wani fim mai suna *Wata Rana* shekarar 1995, sannan sai qungiyar jigon Hausa ta shirya fim xin

Duk a shekarar ne Yakasai Drama Association ta shirya fim xin *Danja* da sauransu. Samar da waxannan fina-finai da wasunsu shi ne ginshiqin da ya kawo ci gaba har aka riqa yin fim xin haxin gwuiwa. baya ma sai mutum xaya ya xauki nauyin yin fim ba tare da wani ba. ( Garba, 2009).

A cikin shekarar 1998 ne masu shirya fina-finai suka yunquro, suka kafa qungiya ta masu wannan harkar domin su yi magana da murya daya. Tun daga wannan lokaci sana'ar shirya fim ta bunqasa, kuma ga shi qofar shiga wannan sana'ar a buxe take, sai aka dinga tururuwa cikinta, maza da mata, saboda amfanin da ake ganin masu wannan sana'a sun fara samu. Gaskiya ne, wannan sana'a ta samar wa matasa da dama aiki, maza da mata sun zama 'yan wasa da masu shiryawa da masu ba da umarni da masu xaukan nauyi, masu waqoqi da masu kwalliya da masu xaukan hoto da 'yan kasuwa da sauransu. Wannan sana'a ta haxa mutane iri-iri, kuma kowa yana da tasa wadda ta shigo da shi wannan sana'a. Da wannan sana'a ta suka yi mata rijista suka sa mata suna Kanywood Industry, wato masu shirya fina-finan Hausa. A qarqashin wannan industiri akwai kamfanonin da suke shirya fina-finai kuma cibiyar wannan qungiya

Kano. Kamfanoni sun haxa da na Kaduna da Abuja da Sakkwato da Maiduguri da sauran wurare. Akwai dalilai masu yawa da suka wajen samun nasarar gudanar da fina-finan Hausa da suka haxa da aikin yi ga matasa da yawaitar ‘yan sakandare ko masu ilimi da talabijin da bidiyo ‘yan Kwatano(kwance) da sha’awar son kallon fina-Hausa a wajen matan aure.

## 1. 2. Dalilin Bincike

Babu shakka, daga cikin dalilan gudanar da wannan bincike, shi ne an fahimci cewa akwai ayyuka muhimmai waxanda ke da alaqa da wannan bincike. Sai dai kamar yadda binciken ya nuna, duk ayyukan da aka yi ba su dubi irin waxannan matsaloli na mata ba, ba su kuma dubi fina-finan Hausa ba. Maimakon haka sun fi karkata kan sauran sassan adabin Hausa da sauran vangarorin rayuwa. Wani dalilin da ya qara qarfafa gwiwar a yi wannan bincike shi ne don qara fito da martaba da muhimmancin mata ga al’umma, wanda shi ya jawo hankalin masu shirya fina-finan Hausa har suke tavo abin da ya shafi mata.

Har wa yau, an haqiqance cewa, ba a cika ba halin da mata ke ciki muhimmanci ba a fagen bincike, duk kuwa da cewa matan na fama da abubuwan takaici irin na zamantakewar iyali da rashin haihuwa da rashin abinci da kishi da rikice-rikice da 'yan'uwan miji da auren dole, da sauransu.

Haqiqa, babu kon tantama, a cikin fina-finan Hausa akwai abubuwan da suke qoqarin faxakar da al'umma dangane da abubuwan takaicin mata. Tsoma takaicin da mata ke fama da shi a fina-finan Hausa da masu shirya fina-finan ke yi a cikin fina–finansu ya ba da dama a yi bincike don gano ire-iren takaicin da suka qunsa.

## 1. 3. Manufar Bincike

Masu shirya fina-finan Hausa ba a bar su a baya ba wajen jejjefa ire-iren abubuwan takaicin da mata ke fama da su cikin ayyukansu. Qudurin wannan aiki ne ya bi diddigin waxannan fina-finai waxanda aka yi tun daga shekarar 1995 zuwa wannan lokaci, domin nuna wa duniya cewa, masu shirya fina-finan Hausa na yin hovvasa wajen samar da kuma raya wani vangare na adabin Hausa.

Kamar yadda masana adabi suke cewa, ‘adabi madubin rayuwar al’umma’, don haka duk wani aiki da aka yi na adabi, zai zama wani tsani na binciko wani abu na wannan al’ummar da aka yi aikin a kanta. Don haka, yana xaya daga cikin manufar wannan aiki, ya bayyana waxannan abubuwa ga al’umma domin a magance wahalhalun da mata ke fama da

su. Jawo hankalin masana da manazarta don a gudanar da bincike a kan abin da ya shafi al’umma, musamman al’amarin da ya shafi mata.

**1. 4. Muhimmancin Bincike**

Wannnan bincike da ya shafi takaicin mata na da muhimmanci qwarai, kasancewarsa wani yanki daga cikin katafaren fagen adabi wanda ke tafiya da wannan zamani, saboda haka aikin zai amfanar da masu aikace-aikace a kan harkokin mata a fannonin ilimi daban-daban. Binciken har wayau na da muhimmanci domin zai zaburar da mata kan su zage dantse wajen guje wa duk wani abu da zai iya kawo vatanci ga rayuwarsu a idon jama’a.

Haka kuma maza waxanda ba su xauki mata da kima ba za su amfana da wannan nazari domin zai sa su dawo kan hanya su ba mata kima da daraja, su kuma tausaya musu.

Al'umma ko manazarta adabi za su san gudummawar da fina-finan Hausa ke bayarwa ga al'umma. Sannan su ma masu shirya fina-finan zai ba su qwarin gwiwa wajen qara fito da sababbin fina-finai waxanda al'umma za su amfana da su.

Sannan zai amfanar da malamai na sashen nazarin harsuna wajen ba xalibai da masu yin nazari, musamman a kan abin da ya shafi mata da kuma fina-finan Hausa qarin manazarta.

**1. 5. Iyakar Bincike**

Wannan nazari zai dubi fina-finan Hausa ne waxanda aka kan abin da ya shafi rayuwar matan Hausawa. Fina –finan Hausa da shirya don nuna hoton rayuwar mata, ba duka binciken zai iya an taqaita a kan fina-finai guda talatin kawai kamar yadda za a ga a cikin aikin, da kuma manazarta. Binciken ya qunshi shekarar 1995 2012. Dalili kuwa shi ne, daga shekarar 1995 ne fina-finan Hausa yin yawa. Har zuwa yau xin nan kuwa ana ta yin fina-finai waxanda kalle su, za a ga akwai abubuwan da za a nazarta a cikinsu. don

binciken zai taqaita a iya wannan lokaci. Sai dai za a yi qoqari wajen an biya buqatar manufar wannan bincike ta fuskar zaqulo muhimman finan da suka yi fice, kuma suka sami karvuwa ga jama'a.

Sannan fina-finan da za a duba, ba na kamfani xaya ba ne, ko furodusa xaya ba, fina-finai ne na kamfanoni da furodusoshi mabambamta, da suka fito daga garuruwan Hausawa daban-dabam kamar Kano, da Kaduna, da Jos da sauransu.

**1. 6. Hanyoyin Gudanar Da Bincike**

Wannan bincike ya zavi nagartattun hanyoyin da zai yi amfani da su domin samun ingantattun bayanai game da wannan aiki. Waxannan hanyoyi sun haxa da:

Ziyartar xakunan karatu na manyan jami'o'in Arewacin Nijeriya, domin binciko ayyukan da masana da manazarta suka gabatar a kan mata da kuma fina-finan Hausa.

Har ila yau, an ziyarci shagunan sayar da fina-finan Hausa da kuma wurin masu shirya fina-finan Hausa, domin nemo fina-finai da za a yi aiki da su.

Daga qarshe an zauna an kalli duk fina-finan da aka kalato, aka kuma tsettsefe abin da aka kalla domin a samu damar fito da bayanai.

An gina wannan bincike a kan ra’in matantaka. Wannan ra’in wani yunquri ne na wasu tsirarun mutane, da ke qoqarin ganin an daidaita matsayin maza da mata ta fuskar siyasa da tattalin arziki da zamantakewa da sauran fannoni rayuwa.

Tsawon tarihi mata sun sha gwagwarmaya a qasashe da lokuta daban-dabam  domin yunqurin fitar da kansu daga cikin quncin rayuwa da matsi da takura da shiga halin qaqa-nika-yi. A qasashen Faransa da Birtaniya , an yi ta samun mata ‘yan gwagwarmaya, waxanda suka fi mai da hankali wurin ganin mata sun sami ‘yanci musamman daidaito ga haqqinsu, bai wa mata ‘yancin mallakar dukiya da ba su damar samun albashi daidai da maza da ‘yancin jefa quri’a. Ire-iren waxannan ‘yan gwagwarmaya  su ake kira masu kare ‘yancin mata. Bayan ra’in Markisanci wanxanda ke fafutar ganin an sami tsakanin mutane a cikin al’umma ta fuskar tattalin arziki, wani sharhin aka samu na zamani shi ne na waxanda ke fafutukar kare ’yancin Fafutukar kare ‘yancin mata na da dogon tarihi wato dai tun tsohuwar Daular Girka, musamman idan aka yi la’akari da aikin fitattun mata na Daular Girka kamar  wata mata mai suna Sappho da kuma wasan kwaikwayon da Aristophanes ta rubuta nai suna *Lysistrata*  a inda aka

mata sun karve ragamar babbar fadar Girka mai suna Acropolis. A wasa an nuna mata sun fi maza qwarancewa sun kuma yi amfani da matancinsu wurin kawo qarshen wani gagarumin yaqi da ya mamaye wato yaqin da aka yi wa laqabi da yaqin Peloponesiya (De Beauvoir,

De Beauvoir ta ci gaba da bayyana cewa, gwagwarmayar neman ‘yancin mata ta kanno kai a qasar Faransa a cikin littafin marubuci Chaucer mai suna *Wife of Bath* wanda aka nuna qwarewar da ta fi ta dukkan mazaje biyar da jarumar littafin ta aura.

Haka kuma a lokacin farfaxo da ilimi a nahiyar Turai akwai mata da suka rubuta rubutattun waqoqi, kamar su Catherine Des Roches da suka fito daga qasashen Faransa da Ingila.

Tsakanin qarni na biyar zuwa na goma sha biyar wato, tsaka-zamani an sami mata da suka fafata da mazaje wurin neman kamar dai su Christine De Pisan. A qarni na goma sha bakwai rubutattun waqoqi irin su Alphra Behn da Anne Bradstreet suka yi fice wurin sana’ar rubuce-rubuce waxanda maza suka yi wa katutu. juya-hali na Faransa, Mary Wollstonecraft ta yi kira da a samar wa ‘yancin da juyin-juya- hali ya samar cikin Faransa. Akwai jerin mata dama da suka bayyana a Turai da Amurka kamar su Madam De

Brontes da Jane Austen da George Elliot da Elizabath Barret Magaret Muller da kuma Emily Dickinso, inda har aka sami **Virginia da Simon De Bauvoir suka** rubuta muqala, 'Mata Masu Abin Al'ajabi' a shekarar 1963. Wannan ya jawo kafuwar babbar qungiyar mata ta Amurka a shekarar 1966 (Woolf,1929:50).

A watan Mayu na shekarar 1968 aka sami babbar gwagwarmayar neman 'yancin mata, a qasar Faransa wadda ta haifar da zanga-zanga da qone-qone, a sakamakon tunzura da ma'aikata da xalibai mata suka yi. Hakan ya haifar da abubuwa da dama wanda ya jawo gagarumin canji dangane da al'amuran da ke faruwa kan mata. 'Yan gwagwarmaya irin su Jack**ques Derida, Jackques Lacan, Annie Leckevit da kuma Helenine Cixons** sun ba da gudummawa sosai wajen fito da assasa rubuce-rubuce a kan 'yancin mata a qasar Faransa.

A duk tsawon waxannan lokuta da suka shuxe, an hana mata ilimi da kuma mallakar dukiya musamman kuxi. Haka kuma matan sun sha fama da gwagwarmaya bisa danniyar maza da dogaro da mazan. Kai har da maza marubuta da suka xauki duk wani rubutu na 'ya mace a matsayin shashasha.

A galibin rubuce-rubucen maza a qasar Birtaniya, ana bai wa matsayi qasqantacce ko kuma a bayyana su a matsayin sakarkaru

tunani, misali, maqalar Michelet mai suna *Woman, the Relative Being*. dai abin ya ci gaba da kasancewa har zuwa qarni na ishirin lokacin suka fara gwagwarmaya a dunqule kuma a tsare. Mata sun yi a fannoni da dama da suka haxa da sake rubuta tarihin marubuta haxa da marubuta mata, da bambance-bambance tsakanin maza da gudummawar mata wurin rubutu.

Mata dai sun sami kansu a halin qaqa-nika-yi ganin yadda maza suka mamaye fannin rubutu. Don haka, sai mata marubuta a qasar ta Birtaniya, suka shiga tunanin shin za su ci gaba da rubuce-rubuce kan jigon da maza ke yi? Wato littattafansu su qunshi labaran yaqe-yaqe da jaruntaka da tafiye-tafiye masu cike da hatsari. Ko kuwa za su qirqiri nasu jigon ne kamar soyayya da qauna da kishi da sauransu?

Wasu matan ‘yan gwagwarmaya na ganin a ci gaba da rubutu tamkar maza, wasu kuma na ganin matan su mayar da hankali kan abin da ya shafi rayuwarsu.

Haka dai abin ya ci gaba da kasancewa, inda za a bayyana nasarorin ‘yan gwagwarmayar samar wa mata ‘yanci har da cewa sun yi rubutu bisa rayuwarsu da qwarancewarsu da kuma abin da ya shafi ‘ya’ya mata da matsalolinsu.

Abin fahimta a nan shi ne ‘yan gwagwarmayar mata na da alaqa da aqidar Markisanci, kamar irin su Hegel da Schopenhuer da Bergson da sauransu.

Gwagwarmayar samar wa mata ‘yanci ta qunshi qasashe da al’ummomi daban-daban. Alal misali, mata marubuta daga qasashen Larabawa kamar Fatima Mernissi da Laila Ahmad sun fi mai da hankali ne ga al’adun qasashensu wajen neman ‘yancin mata. Haka ma mata baqaqen fata ‘yan Amirka kamar Alice Parker. Na yankin Asiya ma kamar su Gayatri Spiraka su ma dai sun mayar da kai ne ga al’adun qasashensu. Kodayake akwai irin waxannan ‘yan gwagwarmaya a qasar Hausa, amma har yanzu gwagwarmayarsu ba ta kankama ba.

Amma, binciken na ganin ba wai daidaiton jinsi tsakanin maza irin na mata ‘yan gwagwarmayar Turai ake magana ba, illa dai abin ne a kyautata wa mata. Sannan a kiyaye dukkan haqqoqin da Allah Ya ce a ba su daidai gwargwado, wato mata su sami kulawa daga wajen mazaje. Su sami ilimi da kiwon lafiya, da abinci sami sana’ar yi don rage fatara. Sannan a ba su damar zavin mijin Al’umma kuma ko dangin miji su daina addabar mata kan wasu

ba su suke da ikon yi ba. Waxannan abubuwa su ne suke damun Hausawa ba wai ba su dama su yi gogayya da maza ba.

Tasirin abubuwan da aka yi bayani su suke taimakawa wajen bai wa masu shirya fina-finan Hausa haske wajen shirya fina-finansu. Duk da cewa akasarin masu shirya fina-finan Hausa sukan qirqiro fim ne, amma ana samun nason wani al’amari da ya shafi rayuwar mai shirya fim xin ko wasu na kusa da shi ko kuma ya shafi rayuwar al’umma baki xaya. An sami tabbacin wannan zance a yayin gudanar da wannan bincike, da aka zanta da masu shirya fina-finan Hausa. Sun bayyana cewa, wasu fina-finan Hausa suna shirya su ne saboda wani abu da ya faru gare su ko kuma ya faru ga wani, sai su shirya fim a kansa don su faxakar kamar fim xin *kishiyata*.

**1.7. Naxewa**

A wannan Babi, bayanan da suka gabata sun nuna yadda fina-Hausa ke da manufa da kuma hujja da ta sa ake aiwatar da su. Daga manufar tasu har da qoqarin fito da martabar mace ga al’umma. Sai aka dubi tarihin samuwar fina-finan Hausa. Sannan aka xan yi tsokaci jinsi, wariyar jinsi da kuma daidaiton jinsi wanda fage ne mai wuyar iyakancewa, mai kuma nauyi, ba ma ga al’ummar Hausawa ba kaxai, ga sauran al’ummu. Saboda tun farko an riga an ba mata wani

masu rauni a kowane irin al'amari kamar yadda bayanai suka gabata wajen mata ‘yan gwagwarmayar neman ‘yanci a faxin duniya. Bayan babin ya zo da dalilin da ya haddasa wannan bincike da kuma manufar da ake so a cim ma idan an kammala binciken, sai da binciken ya bi har ya cim ma manufarsa.

## BABI NA BIYU: BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

### 1. 0. Gabatarwa

A babin da ya gabata, an yi tsokaci ne kan ra’in matantaka waxanda ke fafutukar ganin an sami daidaito tsakanin jinsin maza da mata a dukkannin vangarorin rayuwa. A wannan babin kuma za a waiwayi ayyukan da suka gabata masu alaqa da wannan aiki.

An yi nazarce-nazarce da dama a fagen adabin Hausa. Daga cikin irin nazarce-nazarcen da aka yi akwai littattafai da kundayen bincike da mujallu da maqaloli, ire-iren waxannan ayyuka ne za a duba don sanin makamar wannan nazari. Za a kwatanta waxannan ayyuka da wanda za a yi don tabbatar da cewa kowane akwai fuskar da ya duba.

### 2. 1. Nazarce-Nazarce A Kan Fina-Finan Hausa

Daga cikin nazarce- nazarcen da aka yi game da fina-finan Hausa, akwai littattafai da kundayen bincike da muqaloli waxanda za a kawo su don kwatanta su da wannan aiki.

#### 2. 1. 1. Littattafai

Wasu littattafan sun dubi abin da ya shafi al'ada ne a fina-finai, wasu kuwa fina-finan kai tsaye suka duba.

Alfred da Opular (1977), tsokaci suka yi dangane da yadda kamfanonin samar da fina-finai suke tafiyar da ayyukansu a Nijeriya, littafin ya bayar da haske dangane da tarihin samuwar fim da havakarsa a Nijeriya.

Adamu (2004), littafin ya yi bayani kan yadda kafafen sadarwa suka yi tasiri wajen miqa saqon wata al'umma zuwa ga wata. A nan ne aka yi nazarin yadda ake baddala wasu fina-finan wala Allah daga Hindu zuwa na Hausa ba tare da la'akari da bambancin al'ada ba.

Larkin (1995) littafin ya yi tsokaci ne kan dangantakar littattafan soyayya da fina-finai. Ya bayyana cewa littattafan labaran soyayya ba wai sun damu da al'adun Hausar ba ne wajen rubutun, domin ba salon rayuwar Hausawa kawai ta qunsa ba, saqon nasu da suke so a fahimta guda xaya ne, wato *soyayya* sai dai amfani da harshen Hausar da suke yi wurin rubuta labaran za a gane cewa ga Hausawa saqon yake. To haka ma fina-finan Hausa na zamani, domin juya akalar littattafan labaran soyayya suka yi zuwa fina-finai, su sana'a ce a wurinsu na neman kuxi, duk guda biyun xanjuma ne da xanjumai.

### 2.1.2. Kundayen Bincike

Bayan littattafan da suka yi magana kan fina-finan Hausa, sai kundayen bincike da manazarta suka yi a matakan ilimi daban-dabam.

Manazarta sun bi hanyoyi mabambanta don gudanar da nazarce-nazarce a kan fina-finan, sun dube su ta fuskoki daban-dabam, waxansu sun duba jigo ne a fina-finan Hausa, wasu kuma al'ada da xabi'a suka duba. Yayin da wasu suka duba waqa a fina-finan Hausa.

Umma (2000) da Abdullahi (2002) da Chamo (2005) da Yakubu (2006), sun dubi abin da ya shafi jigo ne a fina-finan Hausa.

Su kuwa Habiba (2003) da Ahmad (2003) da Gandu (2006) da Umma (2009) sun dubi abin da ya shafi al'ada ne a fina-finan na Hausa.

Yayin da Umma (2008) ta dubi adon harshe a waqoqin Fina-finan Hausa, shi kuwa Mungadi ya dubi yadda ake mayar da tatsuniyoyi zuwa fina-finan Hausa ne. Su kuma Umar (2002) da Ahmad (2003) gudummwa da matsalolin fina-finan Hausa ga jama'a suka duba.

Umma (2000), ta yi bayani kan yanayin tarbiyya da sigoginta a wasan kwaikwayo da kuma jigogin wasanin kwaikwayon Hausa. duba wasu abubuwa da suka shafi harkokin addini cikin wasannin

kwaikwayo, kamar yadda ake ganin tasirinsu cikin fina-finan Hausa. kuma yi bayanin yadda yanayin zamantakewar jama'a yake a kwaikwayo, musamman abin da ya danganci miji da mata, iyaye da da magabata da yara da malamai da xalibai da sarki da talaka da da kuma yadda ake bayyana wannan mu'amalar a cikin fina-finan kwaikwayo na Hausa.

A qarshe aka yi tsokaci kan munanan halaye, kamar rashin xa'a da karuwanci da kwaxayi da qarya. Sai kuma kyawawan xabi'u ta fuskar wasan kwaikwayon fim, kamar ladabi da biyayya da gaskiya da haquri da riqon amana da sauransu.

Abdullahi (2002), ma ya fito da bambance-bambancen da ke tsakanin wasan kwaikwayo da fina-finan zamani, an fara da bayanin samuwar wasan kwaikwayo da ma'anarsa da ire-irensa da muhimmancinsa da kuma bayanin samuwar fina-finan zamani da yaxuwarsu da kuma muhimmancinsu, sannan aka kawo bambancin jigon wasan kwaikwayo da fina-finan zamani da kuma bambancin salo da tsarin wasan kwaikwayo da fina-finan zamani.

Ghari (2005), shi ma binciken da ya yi kan fina-finan Hausa. ya yi bayanin tarihi da yanaye-yanayen fina-finan Hausa da rabe-kuma yadda ake tsara su da kuma bayanin kamfanonin da suke

kuma yi bayani kan Hukumar Tace Fina-finai da kuma rubutu a fina-Hausa da kuma qungiyar marubuta fina-finai. Aikin ya yi bayani kan fina-finai da nau'o'insa da hanyoyin isar da saqo da tubalan gina qarshe aikin ya yi nasarar gano jigogi huxu a fina-finan Hausa haxa da siyasa da soyayya da faxakarwa da kuma ban dariya.

Wani binciken shi ne na Yakubu (2006), wanda ya yi game da kalmomin soyayya a cikin fina-finan Hausa, ya yi sharar fage inda ya bayar da ma'anar fim, da kuma asalin wasan kwaikwayo da samuwar fina-finan Hausa. Sai kuma aka yi bayanin fina-finan Hausa masu jigon soyayya, sannan ya fito da kalmomin kwarkwasa da saye, da aka yi amfani da su a waxannan fina-finai.

Shi kuwa Chamo (2001), gwada kawo yadda al'adun Turawa suka yi tasiri a fina-finan Hausa ya yi. An yi bayani kan ma'anar fim da samuwar fina-finan Hausa. A qarshe ya bayyana dalilin cakuxuwar al'adu da yadda za a magancesu.

Ita ma Habiba (2003) ta dubi yadda fina-finan Hausa suka al'adun auren Hausawa. Ta fara da kawo ma'anar aure da dalilan yin yadda Musulunci ya shimfixa yin aure da kuma albarkar da ke tattare da yadda kimar ma'aurata take a idanuwan jama'a da irin sakamakon

alherin da aure kan haifar. Sannan ta qara da cewa, fina-finan Hausa qara wa al'adun Hausawa komai ba wurin ci gaba ko buqasa, sai dai gurvata rayuwar matasa maza da mata kai har ma da matan aure da sha'awar irin xabi'un da suke nuna wa a cikin fina-finan.

Shi ma Ahmad (2003), tsokaci ya yi kan muhimmancin fina-finan Hausa wajen bunqasa tattalin arziki da samar da aikin yi ga jama'a. An kuma kawo bayanin matsaloli da ke cikin fina-finan Hausa na zamani waxanda suka haxa da matsala ta fuskar al'ada da addini da kuma bayanin yadda mata suka jahilci fina-finan. A qarshe ya kawo shawarar yadda za a magance matsalolin ta fuskar shari'a da kyawawan al'adun Hausawa da xabi'u da kuma yanayin zamantakewa.

Hakika ma Umma (2009) ta yi tsokaci kan yadda al'adun Larabawa da na Turawa da na Indiyawa suka yi jirwaye cikin fina-finan Hausa. Da yadda na maqwabtan Hausawa kamar Yarbawa da Igbo da Kanuri da Fulani suka yi naso a cikin fina-finan Hausa. An kuma duba yadda Hausawa suka cuxanya da wasu al'ummu, kamar Turawa da Larabawa da kuma mutanen Asiya, sannan da irin sakamakon da aka samu a sanadiyyar wannan cuxexeniya ta fuskar zamantakewa da ladabi da biyayya da kunya da sutura dea abinci da gaskiya da qawa da sauransu.

Haka shi ma Gandu (2006), nuna yadda ake mayar da fina-finan Hindu kai-tsaye zuwa na Hausa ya yi, ba tare da la'akari da bambancin al'adu ba. Wannan ya qunshi mayar da waqoqinsu (Hindu) zuwa na Hausa da amfani da karin muryar Hindu a waqoqin Hausa. Da kuma raye-rayen al'adar Hindu da rayuwar aurensu da ire-iren tufafinsu, kai har ma da rayuwarsu ta yau da kullum.

Mungadi ya yi tsokaci a kan yadda ake mayar da tatsuniyoyin Hausa a cikin wasannin kwaikwayo na bidiyo. Ya faro ne ta duba adabin baka cikin wasan kwaikwayo na Hausa da duba sassan adabin bakan. A qarshe ya nazarci tatsuniyar *Daskin da Rixi da ta Kogin Bagaja* Ita ma. Umma (2008) kamar Mungadi (2000) duban dabarar sakaxa waqa cikin fina-finan Hausa ta yi. An bayyana yadda waqoqi suke a fina-finan Hausa tare da bayanin lokacin da fina-finai suka fara wanzuwa da kuma havaka. An kuma kawo wasu daga cikin waqoqin da ake samu a fina-finan Hausa da bayyanin abubuwan da suka haifar da sakaxa waqa a cikin fim, tare da yin tsokaci kan jigogin waqoqin fina-finan tare da kawo misalan waqoqin Hausa da kuma samuwar kixan zamani a fina-finan Hausa. Sannan ta yi bayanin yadda adon harshe ya warwatsu cikin adabin waqoqin fina-finan Hausa.

Shi kuwa Umar (2002), ya dubi gudummawar da fina-fnan Hausa suka bayar a vangaren adabi. Aikin ya qunshi bayani kan adabi da rabe-rabensa da kuma tarihin samuwar wasan kwaikwayo na Hausa. Sannan ya duba adabin zube da wasannin gargajiya da waqe-waqe duk a fina-finan Hausa.

### 2. 1. 3. Maqaloli/ Mujalla

Bayan kundayen binciken da suka duba fina-finan Hausa, sai kuma maqaloli da mujallu da masana suka gabatar a tarurruka daban-daban, waxanda suka yi magana kan fina-finan na Hausa.

Louise (1996) da Yakasai (2002) Al-Kanawy (2004) da Umma (2008) da Rabi (2009) sun dubi abin da ya shafi jigo ne a fina-finan Hausa. Yayin da Bunza (2002) Adamu (2004) da Larkin (2004) da Krings (2005) suka duba al'ada, Mandawari (2004) da Galadima (2001) suka duba waqa a fina-finan Hausa.

Louise (1996), ya yi bayani kan tarihin gidan talabijin na CTV yadda suke gudanar da wasan kwaikwayo a gidan talabijin da kuma

rawar da kowa yake takawa a cikinsu. Sannan an nuna irin basirar da nunawa da darasin da suke koyarwa ga jama'a. A qarshe an kawo da wasannin kwaikwayon na talabijin suke takawa wajen faxakar da al'umma.

Shi ma Yakasai (2002) ya bayyana cewa, shekarun 1997 zuwa 1999 ne aka samu bunqasar fasahar bidiyo da kuma kwaxayin yi da kuma samarwa da gabatar da salon Hindu a bidiyon Hausa ( jigo da waqa da tsari), wanana ne ya taimaka wajen samun bunqasar fina-finan Hausa daga kimanin kaso hamsin a shekara bakwai zuwa kaso xari a shekara takwas. Ya ci gaba da cewa, halin yanzu kasuwa ta buxe kuma soyayya ita ce qashin bayan waxannan fina-finai na bidiyo, kuma a nan ne ake sarrafa waqoqi, (galibi na soyayya) cikin waxannan, baya da qaruwar masu shirya fina-finai sai kuma ma'aunin mawaqan ya tashi suka yi yawan da ba a san adadinsu ba, har kuma ya kasance waqoqin sun ginshi mutane domin babu daxi, babu tsari balle ma'ana.

Haka shima Al-Kanawy (2004) ya bayyana cewa mutanen da harkar fim a farko suna da tunanin yaxa al'adar Hausa, kuma suna da tunanin gobe, inda ya ba da misalin wasu fina-finai. Ya ci gaba da cikin fina-finan da ake yi daga baya ma akwai masu ma'ana duk da

a rasa 'yar kaucewa ba a cikinsu. Amma a wata fuskar akwai shiririta a cikinsu. A qarshe ya bayyana cewa in dai faxakarwa suke yi shagaltarwa ba to daraktoci da forudusoshi kamata ya yi su xauko mata manya ba qanana ba su saka su cikin shirin fim.

Ita ma Umma (2008), kamar waxanda suka gabata jigon tarbiyya ta duba, inda ta bayyana cewa, tarbiyya muhimmiyar aba ce mai girma a rayuwar kowace al'umma, musamman dangane da zamantakewar mutanen wannan al'umma. Ta kuma duba tarbiyyar Bahaushe ne a fina-finan Hausa, sannan ta fito da matsayin tarbiyya da dangoginta kamar yadda suka yi naso a fina-finan Hausa, da kuma yadda wasannin kwaikwayo suke koyar da kyawawan xabi'u da kuma yadda suke kore tare da dakushe munanan halaye a al'ummar a Hausawa.

Haka ma Rabi (2009) ta yi tsokaci kan yadda ake fito da halayen mata a fina-finan Hausa, inda ta bayyana cewa an yi abin da Hausawa ke cewa, 'an bugi jaki kuma an bugi taiki'. A wasu fina-finan an nuna mata a matsayin masu kunya da haquri da ladabi da biyayya. A wasu fina-finan kuma aka fito da matan a matsayin masu kishi da bin bokaye da kuma saka sutura wacce ba ta dac da al'adun Hausawa ba.

Yayin da waxanda suka gabata suka dubi alqibla xaya, shi ma Bunza (2002) ya dubi yadda littattafan Hausa na soyayyya suka gurvata al'adun Hausawa, inda ya bayyana cewa fina-finan Hausa sun fi su muni, domin littattafai sai mai iya karatu, amma su fina-finai ko wanda bai iya karatu ba zai kalla ya gani. Haka nan kuma yara qanana da ba su kai mizanin karatu ba, a nan ake vata musu qwaqwalwa. Lahkin (2004), shi ma ya yi bayanin sinima da yadda Hausawa suke kallanta a matsayin dandali na 'yan iska, ya kuma nuna yadda gwamnati ta yi amfani da talabijin wajen tallata aikace-aikacenta. Ya yi bayanin dangantakar da ke tsakanin littattafan soyayya da fina-finan Hausa, inda ya bayyana su da cewa, 'xanjuma ne da xanjumai, ba wai al'adun Hausawa suke isar wa ba, domin ba salon rayuwar Hausawa kawai suka qunsa ba, saqon nasu da suke son a fahimta guda xaya ne wato 'soyayya'. Kaiyage (2005) ya dubi al'adun fina-finai ne a Arewacin Nigeriya, sannan ya kasa fina-finan gida biyu akwai, fina-finai waxanda suke da ra'ayin a sanya abubuwan addini da kuma masu ra'ayin ba lalle a cusa sha'anin addini a irin waxannan fina-finai ba. Sai kuma aka duba dangantakar da ke tsakanin fina-finai da kuma wasu al'adu, da kuma siysar 'yanwasa da yadda ta danganci 'yan wasa.

Galadima (2001) ya nuna alaqar  waqa da fim wato yadda ake cusa waqa cikin fim, inda ya ce baquwar al'ada ce cikin tsarin shirin fina-finan Hausa, ya bayyana cewa waqa tana taimakawa wajen sayar da fina-finai, amma a matsayinsu na alqalai a wannan fanni waqoqi ba su zama dole ba a wajen shiri, su ba su xauki waqoqi a bakin Shirin ba.

Kumai Mandawari (2004), ya fara da bayyana bambancin da tsakanin waqe da waqa, inda ya bayyana waqa da cewa ita ce wadda mawaqa ke rerawa da nufin nishaxantar da mai saurare tare da kixa kamar kalangu ko gurmi ko kuge da sauransu. Waqe kuwa ita rubutacciyar waqa, ta kasance tsararriyar hanya ce ta karya waqa qa'idoji da kuma manufa. Sannan ya bayyana cewa waqoqin fina-Hausa sun samo asali ne daga marubuta waqoqin bege na Annabi amincin Allah su tabbata a gare shi). Ya kuma bayyana cewa fim xin da aka fara da waqa shi ne *Dausayin Soyayya* na gidan talabijin na Kano da aka yi a 1986. Sannan a 1994 aka sake rera waqa a fim xin Ya xora da cewa waqa ta yi tasiri matuqa a fina-finan Hausa domin  a tsakanin 1999 zuwa yau duk fim xin da ya yi tashe a wannan tsakanin iske waqarsa ce ta taimaka wajen sai da shi. Sannan sai ya yi tsokaci

tasirin waqe a siyasa da kuma tasirin waqe a addini da sauran rayuwa.

Kamar yadda aka ga aikace-aikacen da masana da manazarta suka yi, za a iya fahimtar cewa ayyukan sun shafi fina-finan Hausa ne, amma ba su tavo abin da ya shafi mata ba. Kamar Umma (2000) da Abdullahi (2002) da Chamo (2005) da Yakubu (2006) da Louise (1996) da Yakasai (2002) da Al-Kanawy (2004) Umma (2008) da Rabi (2009) sun yi bayanin abin da ya shafi jigo ne a fina-finan Hausa. Amma kamar aikin Chamo (2001) da Habiba (2003) da Ahmad (2003) da Gandu (2006) da Umma (2009) da Bunza (2002) da Adamu (2004) Larkin (2004) da Krings (2005) sun yi tsokaci ne kan abin da ya shafi al'ada a fina-finan Hausa. Umma (2008) da Mandawari (2004) da Galadima (2001) waqa suka duba a fina-finan Hausa. Ba su nazarci takaicin mata a fina-finan Hausa ba kamar yadda wannan aiki ya yi ba.

## 2. 2. Nazarce- Nazarce Dangane Da Mata

Bayan nazarce-nazarcen da aka yi kan fina-finan Hausa, sai waxanda suka dubi al'amaran da suka shafi mata. Wasu sun yi aiki a

abin da ya shafi halayyar mata, wasu kuwa matsayin mata suka yayin da wasu suka duba gudummawar da mata suka bayar a adabin

**2. 2.1. Littattafai**

Kamar yadda a baya aka sami littattafai da suka yi magana kan fina-finan Hausa, a nan ma akwai littattafai da suka yi bayani kan al'amuran mata.

Aliyu (1982), ya yi bayani kan aure da kuma haqqin ma'aurata a Musulunci. Ya kuma bayyana matsayin mace tun lokacin jahiliyya da kuma matsayinta a wasu al'ummu kamar al'ummar Hindu da Romawa da Girkawa da sauransu, har zuwa matsayinta a addinin Musulunci da kuma irin 'yancin da Musulunci ya ba wa mata.

Yayin da ita kuma Hauwa (2006) ta nuna yadda Shehu Usman Xan-fodio ya bayar da muhimmanci kan ilimin mace na addinin Musulunci da kuma yadda Turawan mulkin mallaka suka qasqantar da matsayin mata a qasar Hausa.

Mack da Jean (2004) sun rubuta littafi a kan Nana Asma'u 'yar Shehu Usman Xanfodiyo. Sun yi bayanin rayuwarta da irin muhimmiyar rawar da ta taka wajen gyara xabi'u da halayyar al'umma. Da waqoqin da ta rubuta masu jawo hankalin jama'a kan al'amuran duniya.

Sai kuma ita Mack (2004) ta kuma rubuta wani littafin wanda shi ma ta yi magana kan gudummawar mata a adabin Hausa. Ta nuna irin yadda matan Hausawa Musulmai ke yin waqoqi, waxanda suka haxa da waqoqin bikin aure da kuma na bikin suna, waxanda duk suna xauke da karin magana da yabo da kuma kirari. Sannan ta kawo misalan wasu mawaqan Hausawa mata, kamar su Hajiya Hauwa Gwaram da Hajiya 'Yar Shehu da Hajiya Maizargadi da Hajiya Fati da Hauwa Mai Duala da Hajiya Barmani Coge da kuma Binta Zabaya Woolf (1929) ta fi mai da hankali ne bisa yanayin da mata samun kansu ciki, musamman ga fannin zamantakewa da tattalin samar wa mata nasu gurbin a harkar rubuce-rubuce. Manufofinta sun wasu bayanai guda biyu da ta gabatar a Kwalejin 'Yan Mata ta Cambridge a shekarar 1928 wadda aka buga a littafinta mai suna *A One's Own* a da kuma xaya jawabin da ta yi wa laqabi da *Three* waxannan jawabai ta yi magana kan 'yancin mata a matsayinsu na Wannan ta sa aka xauke ta a matsayin wadda ta fi duk sauran mata gwagwarmayar 'yanci fice a qasashen da ke magana da harshen Wannan 'yar gwagwarmaya ta yi rubuce-rubuce da dama wasu daga littattafanta da suka yi fice sun haxa da *Mrs. Dallowayi* wanda aka

shekarar 1925 da *To The Lighthouse* wanda aka a rubuta a shekarar *Orlando* wanda aka rubuta a shekarar 1928.

De Beauvoir (1949) ita ma a cikin littafinta mai suna *Introduction Woman As Other* ta yi nazari sosai bisa gwagwarmayar da kuma halin da mata suka sami kansu ciki. Ta yi nuni da cewa irin qunci da halin qaqa-nika-yi da mata suka kasance ciki ba ya rasa nasaba da cewar, dama tun fil azal, mace mai dogaro ga namiji ce, idan ma ba a kwatanta da baiwar namiji ba. Mata dai ba dai-dai suke da maza ba. Ta qara da cewa hatta a qasashen da suke bisa doron shari'a, da ake cewa mata daidai da maza, a zahiri ba haka abin yake ba, domin matan ba za su iya fafutar qwatarwa kansu 'yanci ba.

Duk da yake ba tana magana kan al'ummar Hausawa ba ne, amma ta bayyana cewa, idan aka duba matsayin maza da mata bisa ga al'amuran da suka shafi tattalin arziki, za a tarar bambancin a bayyane yake. Alal misali maza ke riqe da ayyuka mafiya girma da albashi mai tsoka. Su suka mallaki kamfanoni da masana'anta, su suke da ajiya mafi girma a bankuna da sauransu. Duk waxannan abubuwan [illegible] mata, ta nuna cewa, A fannin ilimi kuma, maza sun yi wa mata tazara. sun fi mata yawa da kuma zurfafawa wurin samun ilimi, wato ci gaba

ilimi har zuwa jami'a. Ballantana kuma a zo fannin mulki da siyasa, a ma maza su suka yi fice domin suke da manyan muqamai, suke da tsayawa matakan mulki. Daxin daxawa, maza ke xaukar nauyin mata, samar musu da gida da sutura da abinci. Kai har ma duk abin da ya 'ya mace ta yi ta fannin addini da kyawawan xabi'u, duka maza ke Alal misali, wacce irin sutura mace ta kamata ta saka. Duk waxannan abubuwan rayuwar mata ta dogara kacokan bisa maza.

Wollstonecraft (1792) ta yi yunqurin jawo hankalin al'ummar duniya a kan yadda ake tauye 'yanci da danne haqqin mata a duniya. Ta bayyana cewa, ya zama dole a san cewa mata kamar maza suna da irin rawar da suke takawa wajen ci gaban al'umma, don haka ya dace a ba su damar su taka rawar da kyau. Sannan ta yi kira kan daidaito tsakanin mata da maza a wasu vangarorin rayuwa daban-dabam, da suka haxa da siyasa da zamantakewa da ilimi da sauransu. Amma ba wai tana faxin cewa, maza da mata xaya suke ba. Abin da take nufi shi ne a wajen Ubangiji da mace da namiji xaya suke.

Sannan ta yi bayani kan wajen da ya shafi ilimi, inda ta ce, kamata a kai yara makaranta, kuma a ba su tarbiyya a gida, wannan ma ilimi ne.

Da alama ayyukan waxannan mata 'yan gwagwarmayar su ne taimaka wajen gina tunanin al'umma game da harkar nazarin

Domin tun daga wannan lokaci sai aka *aza* harsashin nazarin ake ta rubuce-rubuce game da mata.

### 2. 2. 2. Kundayen Bincike

Bayan littattafan da suka yi magana kan mata, sai kuma kundayen bincike. Daga cikin kundayen da suka duba halayyar mata, akwai Talle (1972) da Zilai (1972) da Zilai (1994) da Bakura (2003)Sai kuma waxanda suka dubi matsayin mace da suka haxa da, Laraba (1984) da Salamatu (1995) da Rabi (1998) . Yayin da su Hajara (1986) da Maryam (2001) Nafisa (2002) da Mainasara (2008) da Balbasatu (2009) da Hauwa (2011) da Bilkisu (2012) da suka dubi gudummawar mata a fagen adabi.

Talle (1972) da Zilai (1972) sun bayyana a nazarinsu cewa, yawancin wasannin kwaikwayon wancan zamani cike suke da tsofaffin al'adun Bahaushe, waxanda suka sava wa addinin Musulunci, duk kuwa da cewa addinin Musulunci shi ne hanyar rayuwa gaba kaya.

Zilai (1972) ta nuna littafin *Zamanin nan Namu* da cewa, yana nuni ne a kan rikici ko kuma takun saqar da ake yi tsakanin tsofaffin al'adu da sababbi a zamantakewar aure.

Dukkansu sun fito da halayyar wasu iyaye mata marasa xabi'un kirki, da yadda suke cusa wa 'ya'yansu xabi'un banza irin su son abin duniya ta hanyar tallace-tallace. Da halin tsofaffin mata na kinibibi da gulma da yaudara, kamar yadda Uwar Gulma ta zuga Halima Iler (1972). Talle ta yi yaji ba ta tsaya nan ba, sai da ta kawo maganar sakacin da maza ke yi wajen nuna halin ko-in-kula dangane da hakkin kula da iyalansu. A qarshe ta qarqare da cewa al'ummar Hausawa, al'umma ce da ke da son abin duniya da kuma rashin ba ilimin mata muhimmanci kamar yadda aka nuna a halayyar 'yan wasa.Kamar yadda waxanda suka gabata suka dubi halayyar mata ta kinibibi da gulma da kuma yaudara. Haka ma Zilai (1994) da Bakura (2003) suka dubi halayyar mata ta kishi.

Zilai (1994) ta bayyana ma'anar kishi da cewa, hali ne da mutum yake tsananin son abu ba tare da tarayya da wani ba. Sannan ta bayyana dalilin yin kishi tare da sigoginsa. Ta nuna cewa ana gabatar da kishi ta magana, ko zungura wani abu inda kishiya take, tare da nuna cewa mata su suka fi nunawa da aiwatar da shi.

A yayin da shi kuma Bakura (2003) ya bayyana yadda kishi ya kasance a tarihin Musulunci. Ya bayyana cewa Mala'iku da Iblis sun

bayyana kishinsu, da yadda ‘yan uwan Annabi Yusuf suka bayyana a kansa. Ya kuma kawo irin kishin da ya gudana a tsakanin matan Muhammadu (S.A.W.) da kuma yadda Aljanu ke kishin xan Adam. ya bayyana yadda Hausawa ke nuna kishinsu kafin bayyanar kuma irin sauyin da aka samu bayan zuwan Musulunci qasar Hausa, yadda zuwan Turawa ya yi tasiri a kan kishin Hausawa. Ya ci gaba ire-iren kishi a qasar Hausa tare da tavo kishi a adabin baka, inda ya kishi a tatsuniya, da kishi a qissa, da kishi a almara, da kishi a hikaya, kishi a waqoqin baka na makaxa, da kishi a waqoqi na musamman.

Kamar yadda waxanda suka gabata suka dubi halayyar mata, ita kuma Laraba (1984) ta dubi muhimmancin mata ga tarbiyyar yara. Ta bayyana mace a matsayin malamar farko ga yara, tare da bayyana irin wahalhalun da mata ke sha, tun daga xaukar ciki da naquda da kuma haihuwa. Ba ta tsaya nan ba sai da ta kawo ire-iren tarbiyyar da Bahaushe ke yi wa ‘ya’yansu wadda ta haxa da girmama na gaba, da tsabta da ladubban cin abinci da kuma koyar da shi harshensu yayen.

Suyaye Salamatu (1995) da Rabi (1998) bayyana matsayin mace suka yi a rubutattun wasannin kwaikwayon Hausa.

Salamatu (1995) ta yi tsokaci kan hakkin mace a zamantakewar aure da ma wadda ba auren take ba.Ta kuma kawo ra'ayoyin marubuta wasannin kwaikwayon Hausa ta hanyar amfani da littafansu.

Ita ma Rabi (1998) ta yi tsokaci kan halayen mata a zaman Hausawa. Ta duba halaye masu kyau da marasa kyau, waxanda aka alaqanta su da mata musamman Hausawa.

Salamatu (1995) da Rabi (1998) duk sun nuna cewa, sakamakon da 'yan wasa mata ke samu a rubutattun wasannin kwaikwayo bai dace da halayyarsu ba. Rabi (1998) ta qara da cewa, hakan ba ya rasa nasaba da yadda mafi yawan marubuta wasannin kwaikwayon Hausa mazaje.

Salamatu (1995) ta qara da nuna cewa, mafi yawan mazaje sun xauki mata a matsayin masu rauni da qasqanci da rashin basira da nuna kishi, ga su kuma mamugunta da magulmata ga su kuma karuwai, sannan ba a xauki ilimantar da su a matsayin abu mai muhimmanci ba.

Hajara (1986) ita ma ta bi sahun 'yan uwanta wajen yin nazari a kan abin da ya shafi mata, amma fa a kan  salon maganar matan yankin Katsina. Ta bayyana cewa, salon maganar mata ya bambanta da na maza, a tsakanin matan ma a kan sami bambanci na ilimi da shekaru da matsayin mutum da muhallin maganar da kuma abin da ake magana a kai.

Haka ita ma Maryam (2001), ta yi nazarin yadda mata suke sarrafa lafuzansu a cikin rubutattun qagaggun labarai a inda ta haxa littafin *Sirrin Voye* na 1 da na 2 wanda Bilkisu Funtuwa ta rubuta. Ta fito da salon lafuzzan da kan ja hankalin mai karatu, waxanda da zarar an ji su an san daga bakin mata suka fito. A cikn ta kawo misalun irin waxannan lafuzzan da suka haxa da 'Na shiga uku' da 'Ahayye dar yarda' da irin kamantansu.

Kamar Ayuba Hajara (1986) ta yi bayanin salon maganar matan yankin Katsina, su kuwa Nafisa (2002) da Mainasara (2008) da Balbasatu (2009) duk sun duba irin gudummawar da mata suka bayar a fagen adabi ne.

Nafisa (2002) ta duba irin rawar da mata suke takawa a kan shirin fim da kuma matsalolin da suke fuskanta. Ta yi nazarin mata uku da ke fitowa a fina-finan Hausa da suka haxa da Hauwa Ali Dodo da Halima Adamu da Amina Garba.

Shi ma Mainasara (2008) ya dubi karin magana a bakin mata. Ya kawo ma'anar karin magana daga masana daban-daban. Sannan ya fito da dalilan da ke sa mata yin karin magana, waxanda suka qunshi nuna soyayya da qaunar juna, ko domin mayar da martani, ko kuma domin qwato wa kansu martaba a idon 'yan uwansu mata. A qarshe ya kawo misalan karin maganar da suka shafi kishiyoyi da matan aure da kuma 'yammata.

Ita ma Balbasatu (2009) ta fara da kawo tarihin rubuce-rubucen mata a cikin adabin Hausa, tare da yin taqaitaccen tsokaci kan matsayin mata a zamanin jahiliyya, wato matsayinsu na marasa ‘yanci. A wancan lokacin mace ba ta kai mutum (namiji) ba, amma ta fi dabba. A addinin Musulunci kuwa mace na da ‘yanci amma a wannan zamanin, ta nuna mata a baya suke musamman a fagen ilmi. Ta dubi mace a adabin baka da kuma rubutaccen adabin Hausa. Ba ta tsaya nan ba, har sai da ta nuna cewa kafin zuwan baqi qasar Hausa, matan Hausawa sun kasance masu taka muhimmiyar rawa wajen ciyar da qasa da al’umma gaba. Irin wannan gudummawa ta shafi bangaren tattalin arziki da siyasa da tarbiyya da fasaha da kuma ciyar da harshen Hausa gaba. Mata na yin hakan ne ta hanyar tatsuniyoyi da labarai da kacici-kacici da waqoqi [illegible] da sauransu.

Hauwa (2011) ta nazarci jigogin waqoqin mata na wa’azi a qarni na ashirin. An duba waqoqi guda takwas daga mata marubuta daban-daban, masu jigon ilimi da riqon amana da zamani da lulluvi ga mata da kuma illar kishi ga mata. Kafin ta yi wannan said a ta kalli matsayin mata a qasar Hausa da kuma nazarin irin gudummawarsu a fagen rubutattun waqoqin wa’azi a qasar Hausa.Sannan aka kawo tarihin marubuta waqoqin wa’azi a qasra Hausa.

Ita kuwa Bilkisu (2012) kwatanta rubutun Bilkisu Ahmad Funtuwa da Bilkisu Yusif Ali a ma'aunin harshe, wato yadda suke gina kalmominsu da yadda suke gina jimlolinsu da yawan sakan layi a shafukansu. Haka kuma ta fito da yadda suka yi amfani da rukunana nahawu da suka haxa da; suna da aikatau da bayanau da siffata da shuratasu. A qarshe ta duba salon nahawun tsirau da kuma nahawun tsirau mai rikixa da marubutan suka yi amfani da shi.

### 2. 2. 3. Maqaloli/Mujalla

Waxanda suka dubi matsayin mata sun haxa da, Abdulmumini (1993) da Maryam (2010). Waxanda kuma suka dubi halayyar mata, sun haxa da, Kwantagora (1999) da Magaji (1999). Sai kuma Abdulganiy (2008) wanda ya dubi gudummawar mata a fagen adabi.

Abdulmumin (1993) da Maryam (2009) duk sun yi magana a matsayin mace. Abdulmumini (1993) ya fito da irin matsayin da ake mata ta hanyar nazarin rubutattun wasannin kwaikwayo, wato yadda tauye wa mata haqqinsu na yi musu auren dole da kuma rashin ba su wadataccen ilmi, bayan kuma an yi musu auren mazajen na

da su da nuna musu rashin kula. Daga qarshe hakan na yin rabuwar auren ko da kuwa ba su daxe ba, kamar yadda ya faru ga ta zama qaramar bazawara a cikin *Ai Ga Irinta Nan*. Ko kuma ma ya sanadiyyar rabuwarsu da duniya, kamar yadda ya faru ga Halima a *Uwar Gulma*, inda ta rasa ranta a sakamakon vacin rai.

Kamar yadda Abdulmumini (1993) ya dubi matsayin mace a rubutattun wasannin kwaikwayo, haka ita ma Maryam (2010) ta dubi matsayin mace a yau. Ta dubi 'yancin mata a gargajiyance kafin zuwan Musulunci da kuma'yancinsu bayan zuwan Musulunci, sannan da 'yancin mace bayan zuwan Turawa da kafuwar qungiyoyi. Ta kuma yi bayani a kan irin yadda Turawa suka wulaqantar da mata suka kuma tozarta su, duk wai a matsayin ba su 'yanci, ta hanyar kakkafa qungiyoyi masu xauke da munanan manufofi.

Shi kuwa Kwantagora (1999) duba halayyar mata ya yi na yi junansu sammu. Ya fara ne da bayani a kan kalmar sammu da dalilan da ke sa a yi sammu waxanda suka haxa da qiyayya da jaruntaka da kishi da sauransu. Ya yi bayanin cewa mata kan yi kishiyoyinsu don son jin daxin zama da miji ko kuma don mijin ya

kishiyarta. Ya kuma nuna cewa maza ma na yin sammu idan aka neman aure, don raba matar da mijin da ta aura.

Shi ma Magaji (1999) duba wata halayyar ta mata ya yi ta kunya. Ya yi bayanin ire-iren mutanen da kunya da mutuntawa kan shiga tsakaninsu. Kamar tsakanin iyaye da 'ya'ya da mata da miji da yayye da qanne da surukai da malamai da almajirai da sarakuna da talakawa da maqwabta da kuma tsakanin mai gida da baransa. Ya kuma nuna cewa mata kan ji kunyar faxin sunan xansu na fari da yadda suke kunya da mutunta mazajensu.

Abdulganiy (2008) ya yi nazari kan gudummawar mata a fagen adabin baka, muqalar ta yi bayanin yadda mace Musulma za ta iya bayar da gudummawa wajen gyara al'umma. Ya kawo matsayin mace kafin zuwan Musulunci, wanda ya kasance abin kunya mutum ya haifi mace, inda suke binne ta da rai. Haka kuma ana iya auren mata masu yawa ba tare da sharaxi ba. Ya bayyana cewa zuwan Musulunci ya sa mace ta samu 'yanci, har ya kasance tana da gado, ana kuma ba ta sadaki a lokacin aure. Sannan kuma Musulunci ya hana auren mata fiye da huxu. A qarshe ya kawo hanyoyin da mace Musulma za ta bi don gyara al'umma.

Nazarce-nazarcen da aka kawo a nan dangane da mata, wasu suna nuni ne da matsayin mata a cikin al'umma, wasu kuma suna bayani ne kan halayen mata, wasu kuma sun kalli irin gudummawar da mata suka bayar a fagen adabi ne. Aikin Nafisa (2002) shi ne za a iya fahimtar suna da makusanciyar alaqa da wannan bincike, domin kuwa ta kalli mata ne a fina-finan Hausa, sai dai akwai bambanci a tsakaninsu, domin ita ta dubi rawar da mata ke takawa da kuma irin matsalolin da suke fuskanta a cikin shirin fim, sannan ta yi nazarin mata uku waxanda suke fitowa a fina-finan Hausa, waxanda suka haxa da Hauwa Ali Dodo da Halima Adamu da Amina Garba, a nan kuwa za a nazarci ire-iren takaicin da mata ke fama da shi ne waxanda aka fito da su a fina-finan Hausa.

## 2 . 3. KAMMALAWA

Wannan babin ya yi nazarin kundayen binciken da aka daga kan digiri na xaya zuwa na uku da kuma na babbar difloma ta digiri na xaya, waxanda suke da alaqa da wannan nazari. An kuma yi bugaggun littattafai da aka rubuta da muqaloli da mujallu waxanda da manazarta suka gabatar a tarurrukan qara wa juna ilimi waxannan littattafai da aka duba, sun zama suna da dangantaka da nazari a vangarori mabambanta, don haka sun zama matashiya ko

wannan aiki. Domin Kwantagora (1999) da Magaji (1999) da Talle da Zilai (1972) da Zilai (1994) da Bakura (2003) sun dubi halayyar Su kuwa Laraba (1984) da Salamatu (1995) da Rabi (1998) da (1993) da Maryam (2010) da Aliyu (1982) matsayin mace suka duba. (1986) da Maryam (2001) da Nafisa (2002) da Mainasara (2008) da Balbasatu (2009) da Hauwa (20011) da Bilkisu (2012) da Abdulganiy (2008) da Mack (2004) kuwa gudummawar mata a fagen adabi suka A yayin da kowa ya xauki vangaren da yake so ya tavo, sai ya cikashe wannan gurbi da ake fatan a cike ba. Wato dai babu nazari da ya yi daidai da wanda za a yi a nan. Sai dai waxanda ke da alaqa, wasu kuma alaqar ta nesa ce.

## BABI NA UKU: TAKAICIN MATA A ZAMANTAKEWAR IYALI

### 3. 0. Gabatarwa

A babin da ya gabata an waiwayi ayyukan da suka gabata masu alaqa da wannan aikin. A wannan babi kuma, za a dubi matsayin mace a wajen wasu al'ummu da addinai kafin zuwan Musulunci da bayan zuwan Musulunci da kuma matsayinta a yau. Sai kuma ma'anar kalmar takaici da nau'o'insa, daga nan ne kuma za a tsunduma cikin aikin don fito da abubuwan takaicin mata.

### 3.1. Wace Ce Mace

### 3. 2. 1. Matsayin Mace Kafin Bayyanar Musulunci

Kafin bayyanar Musulunci, mutanen da suka fi kowanne shan wahala tsakanin sauran 'yan'uwansu mutane su ne mata. A wannan lokaci an xauka mace jaraba ce, masifa ce, kuma haihuwar ta bala'i ne, ba abin so ba ne. Don haka a wancan lokaci mutane ba sa son haihuwar 'ya'ya mata. Al'ummu da yawa sun xauka cewa duk wanda ya haifi mace to babu shakka ya gamu da lalacewa sai neman tsari, kamar yadda yake a cikin Suratu Nahl, aya ta 58-59:

> “Kuma idan aka yi wa xayansu bushara da mace sai fuskarsa ta wuni baqa qirin, alhali kuwa yana mai cike da baqin ciki”.
>
> “Yana voyewa daga mutane domin munin abin da aka yi masa bushara da shi. Shin zai riqe shi a kan wulaqanci, ko zai turbuxe shi a cikin turvaya? To, abin da suke hukuntawa ya munana”.

Kuma kowace al’umma da addini akwai irin matsayin da ta ba mace. tsohuwar al’ummar Indiyawa mace baiwa ce, tana yin duk abin da umarce ta da yi, ba tare da musu ba. Hasali ma mijinta shi ne wato abin bautarta. Ta kasance kamar inuwa, idan mijinta ya mutu a qona su, alhali ita tana da rai. Har zuwa yau mata mabiya addinin suna shiga halin qunci, idan mazansu suka mutu suka bar su, domin ana yi musu kallon gawa, wato sun mace a duniya, ba su da sauran jin daxin duniya. Ba su yin kwalliya, ba su kuma cin abinci mai daxi. Ba a hulxa da su, balle a aure su. Sai dai su zauna gidan miji, dangin mijin su rinqa yi musu fyaxe, idan kuma suka qi a kore su daga gidan. Haka kuma a wancan lokacin a al’ummar Hindu akan yi matar iyali, idan da maza goma a gidan, sai su xauki mace xaya a matsayin matarsu su duka (Ibrahim, 2009 : 45). Haka abin yake ko a wajen

al'ummar Rumawa, mace ba ta da muhimmanci ba za ta iya tafiyar da al'amuranta ba, mace ba ta yin shaida, ba a alqawari da ita, ba a kuma ba ta wasiya, haka kuma ba ta yin gado. Don haka duk al'amuranta na qarqashin mahaifinta ko xan'uwanta, idan kuma mai abar mulka ce a wajen mijinta domin zai iya sarrafa ta yadda yake iya kashe ta idan ba ya son ta, ko idan ya kama ta da wani laifi. Har wani taro da aka yi a Daular Rumawa domin a gane ko mace na da kuma ana iya sanar da ita addini (Al-Sheha, 1997: 22).

A wajen Yahudawa kuwa, mace ba ta yin gado kuma idan matansu suna yin jinin al'ada, sai su kevance su daga cikinsu domin sun zama najasa, sai su yi musu rumfa a wajen gida suna tura musu abinci kamar dabbobi.

Nasara kuwa, sun xauki mace a matsayin uwar zunubi, wadda ta yi dalilin fitar Annabi Adam daga Aljanna. Lokacin da Annabi Adamu (A.S.) yana cikin Aljanna ya ci ganyen bishiyar da Allah (S.W.T.) ya hana shi, to sai suka ce Hauwa'u ta ruxe shi har ya ci saboda haka suka xauke ta (mace) a matsayin shaixaniya. A wani taro na Kiristoci da aka tava yi a shekarar 1856 domin gano mace 'yar'Adam ce ko dabba, bayan an tattauna sosai, an yarda cewa, mace 'yar'Adam ce, amma wadda aka halitta domin ta bauta wa namiji.

A al'ummar Girkawa ma ba ta sake zani ba, domin kuwa mata ba su da wata kima, ba a ba su ilimi. Kuma al'ummar gaba xaya ta xauki mace a matsayin mafi qasqantacciyar halitta. Ba su da wani amfani sai dai su haifo 'ya'ya, su kuma kula da aikace-aikacen gida. Idan kuwa aka haifa wa mutum 'ya mummuna ko nakasasshiya, to yana iya kashe ta. Haka ma idan mace na haihuwar 'ya'ya mata zalla, shi ma mijin na iya yanka ta, idan kuwa 'ya'ya maza zalla take haifa, to sai a rinqa kai ta baye wajen baraden qasar, kamar yadda ake yi wa dabba wai don ta haifo 'ya'ya a sami jarumai da za su yi wa qasa yaqi.

A qasar Sin ma haka abin yake, mace ita ce qasa da kowa wajen kima. Sannan ita ake ba aiki wulaqantacce. Sun fi murna da haihuwar 'ya'ya maza, inda suke cewa haihuwar 'ya'ya maza kyauta ce daga Allah. Amma 'ya'ya mata babu wanda yake son su don haka gara mutuwarsu ma da rayuwarsu. Inda har suke yin wata karin magana cewa, 'ku saurari matanku, amma kar ku yarda da abin da suke faxa'.

Wannan matsayi ya yi kama da wanda Larabawa suka ba mace a zamanin jahiliyya. Sun kasa halitta gaba xaya gida uku, kaso na xaya mutane, kashi na biyu kuwa su ba su kai matsayin mutune ba, amma

sun xara dabba, na uku kuwa, su ne dabbobi. Halittar da aka xauka ba ta kai mutum ba, amma ta xara dabba ita ce mace. Mace a jahiliyyar Larabawa ba ta gadon mijinta, ko iyayenta ko 'yan'uwanta, hasali ma ita kanta ma kayan gado ce, domin idan mijinta ya mutu babban xansa wanda ba xanta ba, na iya gadonta. Sannan an haramta wa mata sake yin aure idan mazansu sun sake su. Haka kuma ba su da damar zaven mijin aure, sai dai a aurar da su yadda aka ga dama. Namiji kuwa yana da damar ya auri mata ko nawa ya ga dama, ba tare da yin adalci a tsakaninsu ba. Har ma ta kai suna 'ya'ya mata da ransu a rami don gudun abin kunya, ko kuma duk ta tsira daga binnewa da rai, idan har ta rayu to ba ta da rabo a cikin 'yan'uwanta komai yawan dukiyar da aka bari (Hausawa, 2010 :129).

A wajen Yunanawa kuwa, mace ba ta da wani muhimmanci kamar haja take, za a iya sayar da ita kuma za a iya sayo ta.

A Afirka ta Yamma, kafin bayyanar Musulunci, matan wannan vangare, tun ma ba a ce qasashen Hausa ba, suna cikin duhun jahilci bauta da qangi na maza. Mata sun kasance kamar dabbobi ko nawa so yana iya tarawa. Wasu sarakuna na ajiye mace kusun dubu xaya. Kuma mata ba sa lulluve jikinsu, suna takure ne a gida ba ilimi

(Talata-Mafara, 1999). Rayuwar mace a al’ada irin ta Bahaushe ita kanta tana ganin ba a halicce ta don komai ba, sai don bautar aure, da yi wa namiji biyayya da yi masa hidima. Mace Bahaushiya a tsakanin waxannan lokuta ba ta da haqqin mallaka kamar sadakinta da gadonta. Sarakuna ko Hakimai ne suke qwace wa mace sadakinta (Mohammed, 2011:15).

Mata sun kasance kamar shanu  ba a kullensu, a sake suke kanigbai wa matansa wurin noma a cikin gonakinsa da ake kira Bayan noma su suke xauko ruwa daga rijiya ko rafi domin sha da gida da kuma bai wa dabbobi.  Ita ce kuma za ta yi sussukar hatsi da daka da kuma dafa abinci.  Sannan ita za ta  je  daji ta samo wa wankan jego,idan an sami rabo. Ban da ayyukan gida matan yi sana’o’i da yawa. Sukan yi kiwon awaki da kaji, sukan je  kuma cin kasuwa. Duk da wannan wahala da matan Hausawa ke wa maza, ciyar da su, ko shayar da su, ko yi musu sutura bai zama dole a kan mazajen ba. Da damina ne kawai namiji yake ci da matarsa dole don za ta yi masa noma. Amma a lokacin bazara mace za ta yi qoqarin ci da kanta da ‘ya’yanta ta hanyar sana’o’inta ko kuma amfanin gonar da ta samu a gayaunarta. Haka ma sutura daga ta aure da miji ya yi,

idan matar ta zo gidansa babu ruwansa da suturarta, sai dai ita ta yi wa kanta. A wancan zamani idan Bamaguje zai yi aure, shi mijin tsangaya kawai zai kafa ya kawo kan xaki ya xora, amma shafen xakin da davensa da sa masa qyaure wannan duk aikin matar ne, wadda ba za ta iya yi ita kaxai ba, sai ta yi wo gayyar 'yan'uwanta su Idan kuma budurwa ce iyayenta ne za su yi gayya a yi (Ibrahim, 1982

Haka mata suka sha fama da wahalhalu, da azaba iri-iri a wajen al'ummun duniya daban-daban, kafin bayyanar addinin Musulunci. Musulunci shi ya xaga darajar mace, ya ba ta 'yancinta kamar yadda za mu gani a gaba.

### 3. 2. 2. Matsayin Mace Bayan Zuwan Musulunci

Addinin Musulunci ya 'yantar da mata daga halin bautar da suka samu kansu ciki. Musulunci ya daidaita mata da maza a wasu al'amura. A wajen bauta Alqur'ani ya nuna cewa, da namiji da mace duk xaya ne. A wajen rabon lada ko zunubi Allah (S.W.T.) Yana saka wa mace, yana saka wa namiji, gwargwadon abin da suka aikata. Kamar yadda Ya faxa a cikin suratu Nisa'i aya ta 124:

> “Kuma wanda ya yi aiki daga ayyukan qwarai, namiji ne ko kuwa mace, alhali kuwa yana mumini, to waxannan suna shiga Aljanna kuma ba za a zalunce su da gwargwadon hancin gurtsun dabino ba”.

Sannan Musulunci ya ba mace wasu haqqoqi nata da aka danne mata a zamanin jahiliyya. Misali gado, inda Maxaukakin Sarki Ya faxa:

> “ Maza suna da rabo daga abin da iyaye biyu da mafi kusantar dangi suka bari, kuma mata suna da rabo daga abin da iyaye biyu da mafi kusantar dangi suka bari, daga abin da ya qaranta daga gare shi ko kuwa ya yi yawa, rabo yankakke” (Nisa’i : 7).

Sannan aka ceto rayuwarta daga binne ta da rai, aka kuma ba ta damar neman ilimi kamar yadda aka ba maza. Sannan aka hana mata fita da rana, Musulunci ya yi umarni da su zauna a cikin xakunansu, sai dai duk da haka idan wani qwaqqwaran dalili ya samu mata suna iya fita da rana, amma lalle su lulluve dukkan jikinsu in ban da fuskarsu da tafukansu, kamar yadda Allah (S.W.T.) Ya faxa a cikin Suratu **Nur, aya ta 31:**

> “Kuma ka ce wa muminai mata su runtse daga gannansu, su tsare farjojinsu, kuma kada su bayyana qawarsu face

ya bayyana daga gare ta, kuma su doka da mayafansu a kan wuyan rigunansu, kuma kada su nuna qawarsu face ga mazansu ko ubanninsu…………..”

Addinin Musulunci ya kuma xora wa miji ciyar da matan da yake aure da kuma qananan yara a kowane lokaci, shi zai ba su abinci, kamar yadda yake a suratu Baqara aya ta 23:

> “ Kuma nauyin ciyar da su da tufatar da su yana kan wanda aka yi wa haihuwa”.

Haka ma kuma akwai Hadisan Manzon (S.A.W.) da dama da suka bayyana falalar ciyar da iyali.

> Daga Abu- Huraira (R.A.) ya ce, Manzon Allah (S. A. W.) Ya ce: “Dinaren da ka ciyar saboda Allah da dinaren da ka ciyar wajen ‘yanta wuyaye, da dinaren da ka yi sadaka da shi ga miskini, da dinaren da ka ciyar da iyalinka babu wanda ya fi girman lada sai wanda ka ciyar da iyalinka” Muslimu ne ya ruwaito shi (An-nawawi, 1993:202).

Bayyanar Shehu Usman Xanfodiyo a qarni na sha tara, ya qara waxannan haqqoqi na addinin Musulunci, shi ne Allah Ya ba shi ikon tsaye don faxakarwa da jaddada addinin Musulunci. Shehu ya yi

wadai da yadda ake tauye mace ta fuskar danne haqqinta, da hana mata ilimi da takura su a gida suna aikacen-aikacen da bai wajaba su yi ba, ya yi gwagwarmaya da sarakuna da malamai na wannan lokaci, ya jaddada addini, ya qwatar wa mata 'yancinsu na qangin da suke ciki, ya xaukaka darajarsu. Ya fara wannan gwagwarmaya ne ga himmatawa wajen ilimantar da matan ta fuskar nuna musu haqqoqinsu da abin da ya rataya a wajensu. Bayan gwagwarmaya ya kuma yi rubuce-rubuce da dama kan a bai wa mata darajar da Allah Ya ba su, ga irin abin da yake faxa a cikin littafinsa mai suna Nur-al-albab:

> "Yawancin maza masu ilimi sukan bar matansu da mata da bayi a wulaqance kamar wulaqatattar dabba, ba koya musu abin da Allah Ya yi umarnin a koya musu ba, ba tare da sanar da su dokokin Allah da suka shafe su bar su da jahilcin yadda alwala da sallah suke, azumi da harkokin ciniki da sauran ayyuka waxanda za su yi, waxanda kuma Allah Ya yi umarnin a koya musu. Maza sun xauki waxannan halitta (mata) kamar kayan gida waxanda suka kararraye bayan an daxe ana amfani da

> su. Waxanda sai zubarwa kawai a juji. Wannnan gaftareren laifi ne. A'a, yaya za su bar bayi a baqin jahilci, alhali kullum suna ilimantar da xalibansu" ( Fafunwa, 1974: 49-50).

Shehu Usman ya kafa misali da kansa ta hayar ilimantar da da 'ya'yansa, kuma ya sa su suka zama malamai ga sauran mata ganin an magance matsalar jahilci da ke damun al'umma. Ya kuma buqatar da ke akwai ta ilimantar da mata kan sauran al'amuran da rayuwa kamar harkokin kiwon lafiya da ciniki da sauransu (Bugaje, 2011:11). A Arewacin Nigeriya an sami mata muzakkarai tun wancan na Shehu Usman, waxanda suka yi wa mata da mutane aiki na gari ilimi da wayar da kai. Babban misali a nan shi ne irin gudummawar Asma'u 'yar Shehu Usman ta bayar wajen ilimatar da mata don su ilimi na addini da sana'a. Ta yi rubuce-rubuce da dama, ta yi wa'azi kashi-kashi. Ta rubuta waqoqi irin waxanda suka dace da mata. haxu da wasu matan sun kafa qungiya don ba da gudummawarsu gaban al'umma gaba xaya. Bayan Nana Asma'u akwai wasu matan daban-dabam waxanda duk sun sami yin abin da suka yi ne

sakamakon gwagwarmayar tabbatar da mutuncin mata da Shehu Usman da almajiransa suka yi.

### 3. 2. 3. Matsayin Mace A Zamanin Yau

Har zuwa yau, al'adar nan ta xaukar mace a matsayin 'yan baya ga dangi na nan a zukatan wasu al'ummu. Ko a qasashen da suka ci gaba, masu gwagwarmayar qwato wa mata 'yanci, matsayin mace har yanzu na da rauni a dukkan vangarorin rayuwa da suka haxa da ilimi da siyasa da aure da aikin gwamnati da tattalin arziki da sauransu. A qasar Amirka daga farkon qarni na sha 18 zuwa na 19 an mata 'yanci ta fuskar mayar da su saniyar ware a fagen siyasa. Ta shata wani tsari aka yi wanda yake tabbatar da cewa, matan da suke gwamnati ko na manyan kamfanoni ba su riqe manyan muqamai ba. Albashin namiji kuwa ya fi na mace yawa ko da kuwa aikinsu iri xaya Wannan bambancin kuma ya kasance har a qasashen Ingila da kuma Siriya ( Riley, 1997). Ta ci gaba da bayyana cewa, qasar Ingila marubuciya mai suna Anne Evans ta yi rubutu a kan matsalar mata, ta "mace ba ta da zavi, sai dai ta dogara ga duk abin da ta samu ko ya same ta. Ta kuma tsaya iya xan matsayinta". Babban abin takaicin a

nan shi ne ita wannan mata sai da ta liqa wa kanta sunan namiji wato ‘George Elliant’ kafin rubutunta ya sami karvuwa ga al’umma (Riley, 1997).

Haka kuma idan muka juya muka kalli tarihi, za mu ga cewa, daga cikin shahararrun marubuta da suka yi suna a duniya, waxanda aka yi ta nazarce-nazarce a kan ayyukansu, da qyar ne idan za a sami mace. Misali mun ga an yayata su Plato da Aristotle da Shakespare da Milton da Chaucer da Samuel Johnson da T. S. Elliot da sauransu. Amma ba a damu da shahararrun marubuta mata ‘yan gwagwarmaya ba irin su Jane Austen da Bronte, Woolf da Horston Wallstonecraft da De Beauvoir da sauransu a duniyar Turai da Amirka ba domin komai ba sai don suna mata (Remi, 2005).

A fagen ilimi ma mata ne a baya wajen samun ilimi. A wata qididdigar yawan jama’a da aka gabatar, an gano cewa, a qasashen Sin da Bangaladash yawan mazan da ke da ilimi ya rivanya na mata sau uku. Duk da cewa mata na bakin qoqarinsu ta vangaren tattalin amma wannan bai sa sun sami canji daga matsayin da suke da shi farko ba. Mata na yin ayyuka da dama waxanda ke taimaka wa wajen havaka tattalin arzikin al’umma, wato suna noma da kiwo da kuma

sana'o'in hannu irin su saqa, har ma da fatauci, suna kuma yin ayyukan gayya. Riley (1997) ta yi bayanin cewa, a qasar Sin 'ya'ya mata ne, ake turawa gona ko wajen ga-aiki, domin su nemo wa iyaye da sauran 'yan'uwansu da suka haxa da maza abin masarufi. Sannan a qasar Hindu mace ke neman kuxin biyan sadakin aurenta har zuwa, ko a 'yan kwanakin nan sai da aka sami wani magidanci ya kashe matarsa, kan sun xau tsawon lokaci ba tare da ta ba shi kuxin sadaki ba.

Ko a nahiyar Afirka, ciki har da qasar Hausa, matan sun kasance saniyar ware a vangarorin rayuwa da dama. A fagen siyasa, matan Arewa ba su fara jefa quri'a ba sai a shekarar 1976, ballantana su shiga takara a zave su(Ibrahim, 2009).

A vangaren aikin gwamnati ma, mata tsiraru ne ke aiki, sannan akwai muqamai da ake ganin mata ba su isa su riqe su ba sai dai mazaA harkar ilimi kuwa matan da ke da ilimi qalilan ne, kuma mafi yawan ilimin nasu ba mai zurfi ba ne. Har wa yau qididdiga ta Unesco ta qarshen qarni na ashirin ta nuna cewa, daga cikin yaran da suka shiga makaranta a Nijeriya, kashi talatin da uku ne mata, sauran duk maza ne (Ibrahim, 2009 : 49).

Idan muka gangaro kan yanayin zamantakewa na yau da kullum, mata suna xanxana wahalhalu da dama, da fuskantar vacin rai da takaici, daga wajen mazaje, sannan wani lokacin a sami maza su yaudare su, su yi musu ciki, ko kuma fyaxe. Haka kuma batun auren dole shi ma har yanzu na nan daram a al'adar Hausawa, inda za a yi wa yarinya auren dole ba tare da an nemi yardar ta ba, kamar yadda addini Musulunci ya tanada, kuma a nemi ta zauna da miji ta yi masa ladabi da biyayya.

**3. 2. 4. Matsayin Mace Da Gudummawarta A Fina-Finan Hausa**

Ko a fagen shirya fina-finan Hausa matsayin da ake ba mata bai wuce wanda aka yi bayani a baya ba. Wato raunana. Ramat (2004) ta fito da matsayin mata a fina-finan tun daga tushe, ta yi hakan ne ta hanyar kasa shirin fim zuwa zango biyu.

A zango na farko, ta bayyana cewa fina-finan wancan lokaci na labari ne kawai na aikace-aikacen da hukuma takan yi daban-dabam. vangaren mata kuwa, ana nuna irin ayyukan da suke yi kamar noma da itace da xaukar ruwa da sauransu. Kusan duk a fina-finan wannan abin da kawai za ka dinga gani ke nan, ba za ka ga ana nuna

ba. Yawanci hukuma ce kan sa a yi waxannan fina-finai, don ta nuna ake aiwatar da xaya daga cikin waxannan sana'o'i.

Haka kuma, idan nuna tarihin shugabannin wancan lokaci ne, in an ga mace a ciki, to tana ayarin masu rawar kalangu ne, ko masu rawar bori, don su yi wa manyan baqi rawa, ko kuma ta xaga tutar Nijeriya don ta yi maraba da wannan shugaba da ake yin fim xin dominsa. Ba su da wani matsayi a shirin kuma ba biyansu ladan fitowa ake yi ba. Wasu ma ba za su tava ganin kansu a cikin fim xin ba. Ta qara bayyana cewa, an sami shirin fim na 'yan qananan labarai da tatsuniyoyi, waxanda ake saka mata ciki, a nan ma yawancin matsayin da suke takawa, ba ya wuce na magajiyar karuwai ko uwar varayi ko su zama karuwan masu shirya wannan fim xin. Zango na biyu kuma, shi ne lokacin da talabijin ta kunno kai, dole ana son mace a cikin talabajin ko wasan kwaikwayo, a lokacin aka canja aqidar, sai aka ba mata dama su fito a shirin, amma da wata irin siga don rawar da suke takawa vatacciya ce, idan kuwa aka ba su matsayi mai kyau, to hukuma ce take son a yi farfagandar aikin da take yi, sai a tsara shirin aikin jiyya ko malamar makaranta ko ma'aikaciyar ofis. Ban da waxannan duk matsayin da mace kan fito a fim zai zama rarraunan ne a wannan lokaci.

Duk da wannan qasqantaccen matsayi da ake ba mata a cikin shirin fim a wancan lokacin, a wannan zamanin mata na taka muhimmiyar rawa wajen shirin fim. Domin matan ne suke samar da kashi tamanin cikin xari (80%) na cim ma manufofin shirya fina-finan Hausa (Adamu, 2002 : 53). Domin su suke fito da matsalolin da al'umma take fama da su, kuma ta muryoyinsu ne ake iya magance matsalolin 'ya'ya da kuma zama da su, da na aure da matsala ta 'yan'uwan miji da kishiya da uwar miji da mace da 'ya'yan miji, sannan da matsalar shiga kasuwa miji.

Mata kan fito a matsayi daban-dabam a fina-finai. A mafi yawan fina-finai matan kan fito a matsayin iyaye, kuma sukan kasance masu matuqar muhimmmanci ga rayuwar jarumi. Wani lokacin kuma sukan fito a matsayin jaruman shirin wato su mamaye fim xin gaba xaya. Kuma su ne suke isar da ainihin saqon da ake son isarwa a cikin fim xin. Haka kuma idan ka xauki na matan uba waxanda sukan taimaka ko dai a gallaza wa 'ya'yan gida ko kuma su su yi qoqarin gusar da maigida daga hanya madaidaiciya. Kazalika sukan xauki matsayin kakanni ko iyaye masu tauye haqqin matan 'ya'yansu. Haka sukan xauki matsayin 'ya'yan gida masu nusar da al'umma halayen irin yaran nan marasa kamun kai da sauransu. Ko kuma matsayin matan aure da sauransu.

Duk da wannan gudummawa da matan ke bayarwa wajen shirin fim, hakan bai hana a fito da su a matsayi irin na kishi da qasqanci ko da wata halayya mara kyau ba, ko dai a fito da su a matsayin masu bin bokaye da nuna soyayya da kinibibi da kissa ga mazajen.

**3. 3. Ma’anar Takaici**

Takaici shi ne jin haushi, wanda vacin rai yakan kawo (Qamusun Hausa 2006:199). Vacin zuciya, hasala, fushi ko haushi (Bargery, 1934).

A hirar da na yi da Xangambo ranar 15/6/2012 ya bayar da ma’anar kalmar takaici da cewa, wani tunani ne da yake zuwar wa mutum da zai ji haushin yadda wani abu ya faru ba a san ransa ba, wato bai sa a ransa abun zai faru ba. Ma’ana dai ka ji haushin yadda abu ya faru ba yadda kake so ba, kuma ka ga baiken wanda ya yi abin wato da kai ne ba za ka bari hakan ta faru ba.

Umma ma a hirar da muka yi ranar 15/6/2012 cewa ta yi, abin da ya cusguna wa mutum har ta kai mutum ya yi da-na-sanin aikata abin. Hakan kuma na iya kasancewa mutum ya aikata abin da kansa ko kuma wani ya aikata masa, wanda zai aikata masa yakan kasance na gida ko na waje. Ko kuma wani abu wanda ba ka ji daxinsa ba.

Haka shi ma Raxxa a hirar da muka yi da shi ta ranar 16/6/2012 cewa ya yi, takaici shi ne mutum ya rinqa tafasa a cikin zuciyarsa da kuma damuwa a cikin rai.

Dangane da wannan nazari kuwa, takaici shi ne zama cikin damuwa da quncin zuciya tare da rashin samun kwanciyar hankali.

## 3. 4. Nau'o'in Takaici

Abubuwa da dama kan haifar tare da bayyana takaici a cikin zuciyar mutum, wato dai duk wani abu akasin jin daxi takaici ne. Daga ciki kuwa akwai;

### 3. 4. 1. Fushi

Fushi na nufin vacin rai ko jin haushi ko kufula (Qamusun Hausa 2006:145)., yayin da (Bargery, 1934 : 331) ya bayyana fushi da ciccika ko fusata, ko harzuqa ko hasala ko kumbura ko kuma murtuka. Mutum ya dugunzuma ya shiga wani yanayi daban da wanda shi da shi. Fushi ba abu ne mai kyau ba, domin Allah (S.W.T.) Ya yi

yin fushi, Ya kuma bayyana cewa, Yana tare da masu haquri. Allah (S.W.T.) a cikin Al-qur'ani Yana cewa:

> "Su ne masu ciyar da dukiyoyinsu a cikin yalwa da qunci (masu voye fushi kuma masu yin rangwame ga mutane). Ubangiji Yana son masu kyautatawa" (Suratu Ali-Imran ayata 111).

Haka ma a cikin Hadisi na sha-shida na An-nawawi,

> "Wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, "Ka yi min nasiha", sai Manzon Allah (S.A.W.) ya ce, "Kada ka yi fushi". Mutumin ya yi ta maimaita buqatarsa, amma Manzo Allah (S.A.W.) yana cewa, "Kada ka yi fushi". Bukhari ya ruwaito (Lemu, A. 2007).

Likita Isa a hira da muka yi da shi ranar 3/7/2012 ya bayyana cewa, idan mutum ya yi fushi jininsa yana zagawa da sauri, haka ma zuciyarsa ita ma tana bugawa da sauri, sannan fatar cikin mutum idan da za a buxe ta a lokacin da yake a cikin fushi za a tarar ta yi ja-ja-wur. Daga nan ne kuma sai fushin ya bayyana a fuskarsa wadda ita za ta nuna halin da ya shiga. Wannan ba zai rasa nasaba da karin maganar nan da Hausawa ke cewa, 'labarin zuciya a tambayi fuska '. Idan mutum ya yi fushi ana ganewa ko dai ta fuskarsa ko ta lafazinsa.

### 3.4.2. Haushi

Haushi na nufin vacin rai ko qullatar mutum a zuci ko kumburi (Qamusun Hausa , 2006 : 199). Bargery (1934) kuwa bayyana kalmar haushi ya yi da hassada ko kishi. Ita kuwa hassada wata cuta ce ta voye da kan faru a sanadiyyar ganin qyashi da rashin son ji ko ganin wani ya ci gaba ko kuma wani alheri ya same shi. Wannan cuta ta hassada ana danganta ta da zuciya, sannan duk mai wannan cuta shi kaxai ya san abin da yake ji a zuciyarsa. Kuma duk inda mutum ya kai da fasaha ba zai iya yin bayanin haqiqanin yadda yake ji a cikin zuciyarsa ba. Irin wannan cuta ba ta da magani kai tsaye da za a iya [illegible] da ba haka yake so a yi ba. Mutum kan iya jin haushi a sakamakon abubuwa daban-daban ko saboda wani abu da wani ya yi masa.

Haushi kan zo wa mutum sabida (Adamu, 1998: 6).

### 3. 4. 3. Qunci

Qunci shi ne matsatsi (Qamusun Hausa 2006). Ma'ana dai takura ransa wuri xaya. Mata kan iya shiga halin qunci ta vangarorin da dama. Kamar ta hanyar zamantakewa da jama'a, a wasu lokutan kan sami kansu cikin qunci ta zamantakewar iyali, wato abin da kan

cikin quncin kan fito ne ko dai daga wajen miji ko kishiya ko uwar miji dangin miji ko ma faccala da sauransu. Wani lokacin kuma ta hanyar mu'amala da sauran mutane daga waje.

Wani lokacin kuma mata kan shiga qunci ne ta fuskar tattalin arziki, wato rashin samun abin hannu ko kuxin da za a yi amfani da su wajen sayen kayayyakin masarufi na amfanin yau da kullum, kamar kayan abinci ko sabulun wanki da na wanka da man shafawa da sauran 'yan tsarabe-tsarabe. Yawanci wannan kan faru ne idan ya kasance mace ba ta da sana'a, ko kuma idan mijinta ba mai sakin hannu ba ne.

**3. 4. 4. Wulaqanci**

Wulaqanci shi ne rashin darajanta mutum ko ka yi wa mutum abin da bai kamata ba, ko abu marar daxi. (Qamusun Hausa, 2006 ). Ko kuma nuna tsana ga wani, kamar yadda Bargery, (1934) ya bayyana. Duk wani nau'i na cin mutunci wulaqanci ne. Ta hanyar wulaqanci mutum yake gamuwa da muzgunawa, wato wani abu da mutum zai yi wa wani don ya jefa shi cikin takaici.

Akan iya aiwatar da wulaqanci a aikace ko kuma ta hanyar Wani lokacin akan sami maigida ya rinqa wulaqanta matarsa babu

hanyoyi daban-dabam kamar hana ta abinci ko yi mata duka ko gaya wasu kalamai marasa daxi, ko dai aikata wani abu da zai sa ta cikin

Sannan a tsakanin matan ma akan sami wata matar ta wulaqanta wata kamar tsakanin kishiyoyi ko dangin miji, ko faccaloli, ko matar uba da sauransu. Sukan yi hakan ne mafi yawan lokata ta hanyar habaici ko baqar magana ko ba'a ko zambo ko karin magana da sauransu.

### 3. 5. TAKAICIN MATA A ZAMANTAKEWAR IYALI

Iyali kan xauki fuskoki guda biyu, wato zai iya kasancewa zama na mutum da matarsa, ko matansa, da 'ya'yansa. Amma a tsarin zaman Hausawa na gargajiya iyali sun wuce matarsa ko matansa da 'ya'yansa. A qasar Hausa magidanta suna bin tsarin zaman gandu ne wanda yakan kasance zaman babban gida wanda ya qunshi sashen maigida, da sassan qannensa da 'ya'yansa su ma wasu daga cikinsu magidanta ne, wato suna da nasu iyalin. A irin wannan tsari ba a rasa 'yan guna-gunin maganganu, marasa daxi, ko 'yan faxace-faxace da gori da kan faru tsakanin matan gidan.

Bayan wannan kuma, saboda yanayin rayuwa ta yau da kullum, kowace mace ba ta rasa abin da yake damun ta a rayuwa. Wata

haihuwa ke damun ta, wata rashin wadataccen abinci, da cin wajen maigida shi ne damuwarta. Wasu matan kuwa yadda mutane tsangwame su kan abin da ba su da ikon yi, wato rashin haihuwa ko yawan haihuwar 'ya'ya mata shi ne ke sa su takaici.

Wasu matan kan yi qoqarin bayyana matsalolin da ke damun su musamman ga qawayensu ko 'yan'uwansu domin samun sauqi a zukatansu, wasu kuwa ba sa fitowa fili su faxi matsalolinsu ga kowa, sukan bar abin a cikinsu ya yi ta damun su, har ya jefa su cikin baqin ciki da takaici a wasu lokutan ma ya haddasa musu cututtuka.

Ganin irin waxannan matsaloli a cikin al'umma na neman zama ruwan dare game duniya, ya sa fina-finan Hausa ke qoqarin faxakar da al'umma muhimmancin mata a wannan rayuwa, ta hanyar fito da ire-iren waxannan matsaloli da ke jefa mata cikin takaici .

### 3. 5. 1. Yanayin Zamantakewa Tsakanin Miji Da Mata

A gargajiyance dangantakar miji da mata abu ne mai qarfi suna xaukar mazansu tamkar iyayensu, suna yi musu ladabi da duk abin da suka san zai faranta wa mazan rai. Sannan duk wasu gida da tarbiyyar yara, su ke yi. Wato dai duk irin tarbiyyar da namiji

xora mace a kai tun farko, haka za ta tashi da ita. Ko da kuwa an haqqinta ne.

Bayan bayyanar addinin Musulunci ne aka bayyana haqqin miji a kan matarsa da kuma haqqin mace a kan mijinta. Haqqin miji a kan matarsa shi ne, ci da sha da tufatarwa da kuma kare mutuncin juna. Kyautatawa ce ga miji ya sami lokaci ya zauna da iyalinsa ya tattauna matsalolin yaransu, kansu da kuma sauran harkokin gida, kamar yadda aka ruwaito.

Daga Abu Huraira (R.A.) ya ce, Manzon Allah (S.A. W.) ya ce:

> “Ku kyautata wa mata, domin ita mace an halicce ta ne daga qashin haqarqari, kuma mafi tanqwarar qashin haqarqarin shi ne samansa, idan ka ce za ka miqar da shi sai ka karya shi, idan kuma ka bar shi sai ya zama a tanqwarensa don haka, ku kyautata mu’amalarku da mata”. Buhari ne ya ruwaito shi (An-nawawi, 1993 : 195).

Ita kuma mace, ladabi da biyayya ga miji dole ne a kanta, wajibi ne mace ta yi tattalin mijinta wurin kula da cinsa da shansa da tarbiyyar yara da kuma tsabtace gida.

Amma ga wasu magidantan abin ba haka yake ba, domin kuwa yawa daga cikin mazaje sun yi biris da waxannan haqqoqi da

xora musu, suna wulaqanta matansu ta hanyar hana su abinci da sutura. Akwai magidantan da ke sa matansu cikin qunci ta hanyar abinci da sauran abubuwan masarufi. Ba sa wadata gidansu da su za su fita su ci mai kyau su sha mai kyau. Sau da yawa wasu za su fita su bar gidansu babu abinci, idan kuwa an sami abincin, sai yana auna musu da gwangwani. Har ila yau, za a ga abincin lami ne nama, ko kuma shinkafa fara da mai, idan kuwa miya ce sai 'tafashi-Ranar da kuwa ya yi sha'awa aka girka masa abin daxi ko abin gidan, matar ba ta da rabo a ciki, don ko kaxan ba zai amince ta ci ballantana ta sami nata kason. Maganar sutura kuwa daga Sallah sai idan an yi sa'a, don ko haihuwa ta yi ba lallai ya yi zanen goyo ba, ballantana ta sami kayan shafe-shafe da na kwalliyar mata. Maganar gida a tattauna abin da ya shafi iyali kuwa ba su yi, sai tsakiyar dare namijin zai shigo gida ya shige xaki ya yi kwanciyarsa. Matar da ta kanta cikin wannan hali na qunci takan kasance cikin takura da zama qazanta da rashin gyara. Sannan tarbiyyar yaranta ma kan raunana.

An fito da irin wannan halayya ta wulaqanta mata ta hanyar abinci a fim xin *Aure Dodon Mata* (2009, na Sky Entertainment, Kano), Samar yake quntata wa matarsa Zara da rashin wadataccen abinci,

ya fita ya je otel ya ci mai kyau ya kora da lemon kwalba. Ko da girki sai Samar ya qayyade mintunan da zai yi, idan mintunan suka dai a sauke abincin ko da bai dahu ba.

Samar : *Zan fita kada a kunnan risho sama da mintuna goma,*

*Abinci kuwa za a kawo'yar tsakuwa, don ba zan yarda a yi min almubazzaranci da kaya ba.*

Sau da yawa haka zai fice bai bar wa Zara ko da tsaba xaya ta abinci ba, ballantana ma har ta yi almubazzaranci. Sai dai idan yunwa ta ishe ta ta xauko kwano ta sa a gaba tana hamma har barci ya xauke ta, idan kuwa ya tashi shigowa sai ya kawo mata biredi gaya ya ce ta ci, idan ta yi masa magana sai ya ce:

Zara: *Yanzu ka yi adalci ke nan, ka xauko biredi gaya ka kawo min?*

Samar: *Biredin kike rainawa, ni fa wannan surutun ke ta shafa to idan ban je na ci na qoshi ba, ya zan kawo miki, kuma na kawo miki kina rainawa, ina jin ki, yi min wa'azi.*

Zara: *Ba wai wa'azi zan yi maka ba, amma gaskiya zan gaya maka, ka dinga yin adalci, ya kamata ka dinga yin adalci, Allah Yana cewa ku yi adalci, ni fa matarka ce.*

Sai ranar da Samar ba zai je cin abinci otel ba, a ranar za a yi girki da nama, amma duk da haka Zara ba ta da rabo a ciki, ga irin abin da Samar ke faxa wa Zara:

Samar: *A sayi nama na naira saba'in, a xebi shinkafa kofi xaya a dafa, don yau ba zan je wajen cin abinci ba. Ke kuwa ki xebi garin kwaki ki jiqa ki sha.*

Zara: *Ka ji tsoron Allah, na dafa abincin ka yi min haramiya.*

Samar: *Ki bi umarnina, idan kuma ba za ki bi umarnina ba to, aljannarki na qarqashin qafar mijinki.*

Da wannan Samar ya dogara yake wulaqanta matarsa da azabtar ita da yunwa. Duk ta rame ta fita daga kamanninta, saboda yunwa kullum kuwa cikin qunci take babu walwala ko fara'a a tare da ita, sai dai ta zauna ta takure wuri xaya tana tunani.

Kowane namiji da irin nasa halin, wasu mazan kuwa a waje faranza ka gansu, zaune a majalisarsu ana ta hira, ana qyalqyala dariya, amma da zarar lokacin komawarsu gida ya yi sai ya murza gashin baki ya sha-kunu. Wasu kuwa haka ma za su shiga gidan ko sallama babu, suna ture duk abin da suka samu a tsakar gida, suna tsaki. Nan da nan kowa zai shiga taitayinsa.

Shi ma fim xin *Jan Hali* (2011, Fasaha Media Concept, Kano), nuna yadda Malam Iro ke quntata wa matarsa Jummai. Malam Iro ya kasance mutum mai tsanani ga matarsa, domin kullum cikin yi mata masifa da bala'i yake na rashin dalili, a waje kuwa ba haka yake ba, hirarsa da abokai ya sha dariya har da tafawa. Har wani lokacin ya tutiyar cewa, shi matarsa Jummai tsoron sa take ji, domin ko kara ya ba ta iya tsallakawa. Yana shigowa gida idan ya yi gyaran murya, Jummai zai kama rawa, ta rasa inda za ta sa ranta saboda tsoron Idan kuwa ya shigo ya tarar da takalma a qofar xaki sai ko ya kama zage-zage. Don haka kullum Jummai cikin taka-tsan-tsan take, kar ya ga wani abu ba daidai ba. Amma da yake mai neman bala'i ne, ba abin da zai yi faxa akai. Akwai ranar da ya zo xaukar buta ya tarar ruwa ciki, nan fa ya kama zagin Jummai ta uwa ta uba. Ban da kuma, unguwa ko qofar gida ba ya barin ta fita. Wata rana aka aiko mahaifiyarta ba lafiya ba yadda take, amma ya hana ta zuwa dubiya, je ba, ita bai bar ta ta je ba. Da takaici ya ishe ta sai ta fashe da kuka baqin ciki. Duk irin wannan abu da Malam Iro ke yi wa Jummai, bai shi idan ya ga ta tara kuxi ya lallava ta ya qwace ba. Haka yake yi

hana ta tara ko sisi. Al'amarin Malam Iro ga Jummai abin sai wanda domin abin ba sakainar xiba.

Bayan wannan kuma, wasu mazan suna wulaqanta matansu na sunna, su bar su su fita wajen matan banza a waje, don haka matan nasu ba su da kima da daraja a idonsu, za su ci mutuncinsu su zagi iyayensu, su doke su, su yi musu duk abin da suka ga dama. Wani lokacin ma wani namijin a gaban matarsa za su rinqa waya da wata matar, yin hakan kuma kan qona wa matan rai, ina laifin ma a je waje a yi, domin Hausawa na cewa, 'qazantar da idonka bai gani ba tsabta ce', duk da dai ba haka aka so ba wai qanin miji ya fi miji kyau!

Irin haka ta faru ga Abida cikin fim xin *Adabiyya* (2010, Nasara Global Concept Ltd, Kano), Abida mata ce ga Sammani, amma bai da kima da daraja ba, kullum cikin wulaqanta ta yake da gaya mata maganganu. Ba ya dawowa gida sai tsakiyar dare, yana can da banza, kuma bai damu da ya ba ta haqqinta na aure ba, a gabanta rinqa yi wa matan banza waya. Dubi irin baqin cikin da takaicin da ya mata, lokacin da take kwance kan gado, amma shi yana zaune yana matar banza, tana kuma jin irin kalaman da yake faxa mata, waxanda

mafarki ba zai gaya mata su ba, don haka da takaici ya ishe ta sai ta shi:

Abida: *Allah Ya sawaqe, Allah Ya shirye ka, wallahi ba ka san darajar aure ba, don kuwa da ka san darajar aure, ba za ka bar kan gadonka na sunna, kan shimfixarka ta lada, ka je kana buga wa wata waya ba, kana yi mata 'kiss' a gabana ba.*

Sammani: *Kin san kin ci darajar mai daraja, amma ba don haka ba sai na mai da ke a bar yin kwatanci, sa'ar ki xaya, na yi magana da wadda zuciyata take mararinta, na yi magana da wadda idan ina magana da ita, vargon jikina yake motsi, kuma mizaninmu ya zo xaya, in ban da haka yau sai kin gane kuskurenki. Burinki dai in zo in kwanta a gadonki, in yi tarayya da ke, to na fi qarfinki, kuma mizanina ya fi qarfin naki, ai ni na gama da ke , da ma kwanturagi na xauke ki na shekara xaya.*

Amfanin Abida a wajen Sammani shi ne ta dafa masa abinci, idan kuwa ta kuskure ta vata lokaci za ta sha zagi har da duka, kamar yadda yake faxa mata.

Sammani: *Bauta kika zo yi, abinci! Don kina qarqashina, na ba ki minti uku ki dafa min 'fried rice'.*

Zama tsakanin Sammani da Abida babu daxi kamar ba ma'aurata ba. Babu wani abu da Abida za ta buqata gun Sammani ta samu, ko fita zai yi sai dai ta ga ya rufe qofa ya fice, ko ta yi magana, sai ya ga dama zai ba ta amsa. Idan kuwa ya ba ta amsa, to fa kalaman ba masu daxi zai gaya mata ba. Dubi irin abin da ya gaya mata:

Abida: *Fita za ka yi?*

Sammani: *To da ma mun yi da ke, idan zan fita sai na gaya miki?*

Abida: *To da ma ba ni da lafiya, idan direba ya kai ka, sai ya dawo ya kai ni asibiti.*

Sammani: *Allah Sarki ba ki da lafiya (cikin tsokani), kuma shi direban aikinki ya zo yi, to ba zai kai ki ba, don ba aikinki ya zo ba.*

Abida: *To ka ba ni kuxi na shiga mota.*

Sammani: *Kuxin mota kike so ko? (ya yi mata ambola), to gidanku, idan na dawo ki kawo min canji.*

Duk irin wannan abu da Sammani ke yi wa Abida, sai dai idan abin ya ishe ta ta saka kuka a xaki ita kaxai, tana faxin:

Abida: *Allah ya ganar da mijina ya san ni matarsa ce ta sunna. Allah ya dawo da hankalinsa cikin gidansa.*

Mata da yawa kan jure aikace-aikacen gidan miji da dama kamar sharar gida, wanke-wanke da wankin kayan miji, wasu matan ko hula miji zai sa, ita za ta yi masa karinta, ta goge takalma, sun zama kamar bayi ko 'yan aiki, amma duk wannan xawainiya ba ta burge wasu mazan, maimakon su yaba, sai ma su kama faxa, da zagi na wulaqanci. Ko 'yar aiki ce dai ai a yaba mata ta ji daxi.

Dubi irin faxa da wulaqancin da Suwaiba ke sha wajen Ibrahim a cikin fim xin *Aure Dodon Mata* (2009, Sky Entertainment, Kano), lokacin da ta yi masa karin hula.

Ibrahim : *Suwaiba! wannan wane irin abu ne? Wa ya ce ki karyan hulata, me ya sa kike yi min shisshigi ga al'amurana? Haka ake yi, ko an gaya miki wannan hular tana buqatar kanki ne? Ko ko an ce dole ne? Yau na ga Allah qaqai.*

Amma duk da haka Suwaiba ba ta daina qoqarin kyautata wa Ibrahim ba, duk da cewa faxan ba zai bar ta ba. Idan zai shigo gidan ba sallama sai dai kawai ya sa kai, da faxansa da zage-zage zai shigo. Irin hakan ce ta kuma faruwa:

Ibrahim : *Sau nawa ina gaya miki, ki daina wanke min kaya, wannan wane irin dabbanci ne, mutum sai ka ce kifi na dinga gaya*

*miki magana ba kya ji, don iskancin banza, iskancin wofi.*

Duk irin wannan abu Suwaiba ba ta cewa komai sai dai ta ce:

Suwaiba: *Allah Ya ba ka haquri, ni dai ba zan fasa ba, ba komai, ni dai addu'ata Allah Ya qara min juriya.*

Idan ya dawo tun daga zaure zai fara qwalla mata kira,

Ibrahim: *Suwaiba! Suwaiba!! Wannan wane irin xanyen kai ne, yaya kayana da na yi musu wankin sikari ki tsoma min su a wannan ruwa omon, wane irin shashanci ne? Haka sudan da kin ga dama sai ki xebi kayana ki tsoma a cikin ruwa.*

Don Allah dubi irin wannan aiki, wasu ma neman mai wanke musu kayan suke yi, amma shi an yi masa wankin maimakon ya gode kuma sai zagi. Allah Ya kyauta! Babu shakka da yawa matan aure a gidajen mazansu abin da suke fuskanta ke nan. Matan aure da yawa na fama da takaici da haqurin zama da mazajensu a zamantakewar aure.

### 3. 5. 2. KISHI

Masu iya magana sun ce:

"Kishi kumallon mata, in ya taso sai sun amayar".

Kishi abu ne daxaxxe kuma mai ximbin tarihi domin kuwa tun fil

azal Allah Ya halicci xan’Adam da kishi, kuma kowa da irin nasa. Wani za a same shi mai zafin kishi wani kuwa kishinsa mai sauqi ne . Kishi ya samo asali tun zamanin Annabawa. Misali kishi tsakanin Habila da Qabila ‘ya’yan Annabi Adam, kamar yadda Allah (S.W.T.) Ya faxa a cikin suratu Ma’ida aya ta 27:

> “Kuma karanta musu labarin xiya biyu na Adamu, da gaskiya a lokacin da suka bayar da baiko, sai aka karva daga xayansu kuma ba a karva daga xayan ba, ya ce: “Lalle ne zan kashe ka” (Xayan kuma) ya ce: “Abin sani dai, Allah Yana karva daga masu taqawa ne”.

Aya ta 30 ta wannan sura ta fito da kishin qarara, inda Allah (S.W.T.) Ya ce:

> “Sai ransa ta qawatar masa kashewar xan’uwansa, sai kuwa ya kashe shi, sa’an nan ya wayi gari daga masu hasarai”.

Wani misalin kishin shi ne wanda ya faru tsakanin Annabi Yusif da ‘yan uwansa (‘ya’yan Annabi Yakubu). Annabi Yusif ya yi baqin jini a wajen ‘yan’uwansa da suke uba xaya saboda son da mahaifinsa yake masa fiye da su. Saboda tsananin kishin hakan ya sa suka yi tunanin su raba shi da mahaifinsa, kamar yadda yake a cikin suratu Yusuf aya ta 8-10

"A lokacin da suka ce, lalle ne Yusufu da xan'uwansa ne mafiya soyuwa ga ubanmu daga gare mu, alhali kuwa mu jama'a guda ne. Lalle ubanmu, haqiqa yana cikin vata bayyananniya".

"Ku kashe Yusufu, ko kuwa ku jefa shi a wata qasa, fuskar ubanku ta wofinta saboda ku, kuma ku kasance a bayansa mutane salihai".

"Wani mai magana daga cikinsu ya ce, "Kada ku kashe Yusufu. Ku jefa shi a cikin duhun rijiya, wasu matafiya su tsince shi, idan kun kasance masu aikatawa ne".

Qamusun Hausa (2006:247) ya bayyana kalmar kishi da cewa, rashin jituwa ne da nuna qyashi irin wanda matan da ke auren mutum xaya suke yi wa juna. Ko kuma nuna gaba ga wani a kan wani ra'ayi ko sana'a ko kuma dagewa da nuna qwazo a kan wani abu na kirki da mutum ya sa a gaba don cimma buri. Shi kuwa Bakura (2003) bayyana kishi ya yi da cewa wata hanya ce ta gwagwarmaya da ke tattare da zargi da tuhuma da savani da rashin jituwa da husuma da mugun nufi, domin qoqarin kare kevantacciyar qauna ga abin so, ba tare da yin tarayya da wani ba.

Ita kuwa Rabi (1998), ta nuna kishi da cewa, hali ne da mutum yake tsananin son abu ba tare da tarayya da wani ba. Akan gabatar da kishi ba tare da wata kangiya ba, domin gaba gaxi mai kishi zai nuna. Rabi (2011), cewa ta yi kishi wata hanya ce da masoya kan bi domin su nuna so da qauna ga abin qaunarsu da kuma kare shi daga kuvuce musu. Kishi halitta ce da ke cikin kowace halitta a doron qasa. Amma al'adar al'umma ce ke jagorancin yadda ake gudanar da shi Dangane da wannan nazari kuwa kishi na iya zama tsana ko qiyayya da hassada da xan'Adam yake nunawa a kan wani ko wata da ke tarayya da abin da mutum yake so. Rashin samun damar mallakar abin da mutum yake so shi kaxai, shi ke haifar da kishi.

Kishi cikin jikin mutum yake sai dai kuma mata sun fi nuna shi da aiwatar da shi. Mata na da hanyoyin nuna kishi kamar ta magana, da habaici da karin magana da lugude da waqa, ko ta shantu ko ta niqa ko zungurar wani abu inda kishiya take, yadda za ta farga da ita ake, ko wata shewa, ko dai wani abu makamancin waxannan (Garba, 1998: 33-34) Kishi kan iya zama kyakkyawa ko mummuna, kuma dukkansu ana iya gane su ta irin yanayin da aka bayyanar da su.

Kyakkyawan kishi ana aiwatar da shi ne don amfanin kai ba tare da cutar da abokin kishi ba. A nan ne akan sami irin kishin da ake kira ‘kishin zuci’. Misali ta fuskar neman ilimi, a tsakanin masu qoqarin neman sa, kowane daga ciki yakan yi qoqarin ya ga ya fi kowa qoqari, ba tare da cutar da kowa ba. Haka ko ta fuskar sana’a ne za a ga kamfanoni masu yin abubuwa iri xaya, kamar sabulu ko magi ko katifa ko gadaje da sauransu, za a ga kowane kamfani da irin ingancin abin da ya samar, saboda haka sukan yi kishi a tsakaninsu ta yadda za su sami karvuwa ga jama’a wanda duk ya fi kishi, to za a ga kullum yana daxa inganta sana’ar tasa ne ba tare da ya cutar da abokin kishi ba. Mummunan kishi kuwa daga jin sunan, ba abin so ba ne. Kishi ne da ake bayyana shi ta hanyar cutar da abokin yi, ko a nuna masa ba a qaunar sa. Irin wannan kishi shi ne aka fi samun sa a tsakanin mata. Ana samun kishi a tsakanin mata biyu waxanda suke mijinsu xaya. Sannan ana samun kishi a tsakanin matar wa da matar qani wato faccala. Haka ma kuma ana samun kishi tsakanin uwar miji da matar xa. Akwai kuma kishin da ke shiga tsakanin yayye ko qannen miji da matar xan’uwansu (Mohammed, 2011:105-106). Irin waxannan kishi su ne suka fi fice, kuma su ne waxanda alqiblar da wannan nazari zai fuskanta.

### 3. 5. 2. 1. Kishi Tsakanin Kishiyoyi

Masu iya magana na cewa;

> 'Kishiya ba haushi ta mata, ana ganin ki kan zagi miji'.

Wannan nau'i na kishi ya zama ruwan dare game duniya a zamani wannan. Kishiya ita ce matar da maigida ya auro domin ta zama abokiyar zama ga ta gidan. Qarin aure ga maigida wani lokacin akan yi dace ya zama mai sauqi, amma wani lokacin yakan zamo matsala ga dukkansu. A mafi lokuta tsananin son kai ne ke haifar da kishi, wato idan mace na tsananin son mijinta, ba ta son ta yi tarayya da wata wajen son sa, sai dai ta so shi ita kaxai.

Tun zamanin Maguzanci, namiji na da damar auren mata ko guda nawa ya ga zai iya ba tare da qayyadewa ba. Wannan ya dogara ne da halin da yake da shi. A wurin Hausawa auren mata da yawa wata hanya ce da mutum zai qara tattalin arzikinsa cikin sauqi a wancan lokaci, domin su taya shi aikin gona da na gida da kuma Haifa masa 'ya'ya da yawa don a sami qarin masu aikin gona. Da addinin Musulunci ya zo, sai ya halatta wa maza auren mace xaya zuwa huxu, matuqar za su yi adalci. Kamar yadda yake a cikin suratu Nisa'i aya ta 3,

> "Kuma idan kun ji tsoron ba za ku yi adalci ba a cikin marayu to, (akwai yadda za a yi) ku auri abin da ya yi muku daxi daga mata; biyu-biyu, da uku-uku, da huxu-huxu. Sa'an nan idan kun ji tsoron ba za ku yi adalci ba, to, ( ku auri) guda ko kuwa abin da hannayenku na dama suka mallaka. Wannan shi ne mafi kusantar zama ba ku wuce haddi ba".

Sannan ya yi umarrni da yin kulle ga mata, wato kada su fita sai da lalura, kamar yadda Allah (S.W.T.) Ya faxa a cikin suratu Nur aya ta 31,

> "Kuma ka ce wa muminai mata su runtse daga gannansu, kuma su tsare farjojinsu, kuma kada su bayyana qawarsu face abin da ya bayyana daga gare ta, kuma su doka da mayafansu a kan wuyan rigunansu, kuma kada su nuna qawarsu face ga mazansu ko ubanninsu……".

Hakan ya sa matan Hausawa suka riqa zama a gida, kodayaushe, sai aka riqa samun yawan qorafe-qorafe a tsakaninsu, musamman su da wani ishasshen ilimin addinin Musulunci, balle su san haqqoqin suke rataye a kansu na juna da kuma na iyalin baki xaya. Wannan ya da hamayya da hassada da kushe tsakanin kishiyoyi, ya zama kamar

kwalliya matsalar da ba a ga qarshenta ba har zuwa yau. A duk lokacin da maigida ya yi aniyar qara aure mace kan nuna damuwarta, wannan xabi’a ce ta mata domin mafi yawan mata ba su son kishiya, sai dai dole. Kuma duk yadda namiji ya kai da son matarsa, ita ma ta kai ga son sa, in dai al’amarin kishiya ya shigo tsakani, to fa lamari yakan wargaje. A wannan lokaci ne wasu mata ke aukawa bala’i na shiga bokaye da malaman tsibbu don dai su ga kishiya ba ta yi tasiri a gidan ba, wasu ma har su sa mata ciwo ko ma su raba ta da duniyar gaba xaya.

Fim xin *Kishiyata* (2011, 3SP International Ltd, Jos), fim ne da ya dace da sunansa domin kuwa an nuna tsantsar kishi, tun daga farkonsa har qarshe an yi ta samun zaman hamayya da hassada da qyashi da makirce-makirce da tsibbace-tsibbace.

Fatima da Talatu, mata ne ga Malam Lawal, saboda tsananin makircin Talatu zama tsakaninsu ya qi daxi. Kullum cikin tashin faxace-faxace suke. Wannan dalili ya sa Malam Lawal ya qara auro wai ko sa rage abin da suke yi, amma maimakon abin ya yi sauqi, sai fi na da, musamman ga Talatu, wadda da ma laifin daga gare ta ne, kuma fito da sabon babi na kishi. Don kuwa,  sai da ta yi qoqarin da

Hafsa cikin quncin rayuwa, domin ta yi asirin da ta sa ta ciwo, daga ma ta hallaka ta gaba xaya ta hanyar makirci da kisisina da nuna duk cikin gidan ita kaxai take qaunar ta, ashe son xan miciji take yi

Domin duk ranar girkin Hafsa, sai Talatu ta lallava ta kwashe naman miya, ta cinye. Idan Malam Lawan ya zo cin abinci Hafsa ta rasa abin faxa. Amma da yake Hausawa na cewa, 'amarya ba ta laifi ko da ta kashe xan masu gida', har ya gama cin abincin ba zai ce komai ba. Amma ko da ta fahimci Hafsa za ta gane ta sai ta yi mata dabara da cewa:

Talatu: *Hafsa kwana biyu na ga kin canja.*

Hafsa: *Ai ni abin gidan nan ne ya fara isa ta duk abin da na ajiye ba na ganin sa a gun.*

Talatu: *Ai yaya babba ce, (wato Fatima), ki yi hankali da ita, idan ba haka ba wata rana har ke ma za ta haxa.*

Idan kuwa maigida ya shiga xakin Hafsa sai Talatu ta je taga ta lave ta ji abin da suke faxa. Ko kuma idan ya shigo da leda a hannunsa, Talatu ta tarasai shi ta zava, sannan ya kai wa sauran matan. Tun daga wannan lokaci abubuwa suka fara yi wa Hafsa zafi a ranta.

Duk da Talatu ta ga hakan bai yi mata ba, sai ta tafi wajen ta laya ta binne a qofar xakin Hafsa da kuma magani ta shafa wa

jiki. Bayan kwanaki kaxan kuwa,  Hafsa ta fara ciwo bajibagani, kuma zarar Malam Lawal ya shigo inda take sai ta fasa ihu, ta faxi a sume.

Ga shi ana magani amma kullum maimakon ciwo ya yi baya, sai gaba yake yi.  Hafsa ta xau tsawon lokaci tana fama da ciwo, amma duk Talatu ba ta fasa karvo magani wajen boka ba tana xura mata. Akwai ranar ma da  ta shiga xakin Hafsa wadda ba ta ma san inda kanta yake ba, ta sa matashi ta danne mata kai tana faxin:

Talatu: *Ni ce ajalinki, sai na raba ki da duniya, tun da kin zavi zama da mijina.*

Burin Talatu bai cika ba a wannan karon, domin tana cikin haka Fatima ta yi sallama ta shiga xakin, sai ta yi sauri ta xaga ta. Ranar nan Talatu ta tafi karvo magani wajen boka kamar yadda ta saba, Hafsa rai ya yi halinsa. Da Talatu ta dawo ta ga taron jama'a a qofar gida,  saboda kisisina irin tata tun daga waje ta yada zane fara kuka, tana ihu, tana tumami, ana ba ta haquri. Da yake mutuwar dare ce, Talatu ta ce ita za ta kwana da gawa, mutane na faxin ba za ta iya ba, amma ta ce za ta iya:

Talatu: *Zan iya, ai 'yar'uwa ce idan ban yi mata ba wa zan yi wa, mun yi zaman lafiya da Hafsa.*

Da aka bar Talatu da gawa da dare ta tashi ta buxe bakin gawa ta saka

laya a ciki. Ashe wannan laya kuma asiri ne ta yi don ta haukatar da Fatima, tun da ta gama da Hafsa. Ai kuwa tana saka layar nan bakin Gawa, Fatima ta miqe ta sava xanta Ahmad a baya ta fice ta bar shiga duniya da, tana hauka, ko labarinta ba a ji.

Haka Talatu ta yi ta muzguna wa kishiyoyi, don kawai sun haxa mijin aure. Ta kashe wannan, ta haukatar da waccan. Gida yanzu daga ita sai ‘yarta sai mijinta, abin da take so ta samu. Nan fa Talatu ta miqe qafa, dangin miji ma masifarta ta hana kowa zuwa gidan. ‘Duk kishin kishiya ba ya hana miji aure’, in ji Hausawa, haka kuwa aka yi domin kuwa Malam Lawal ya kuma yin aure, haka Talatu ta kuma azabtar da ita da jefa  ta cikin takaici. Amarya ta koma ‘yar aiki, kullum sai dai ta yi wa Talatu shara da wanke-wanke da girki, Talatu ce ke da miji. Ita kuwa amarya tsakaninta da miji sai dai kallon-kallo, ko da magana sai dai idan Talatu ba ta wajen ya yi mata, idan kuwa tana wajen bai isa ba, ballantana kuma ya shiga xakinta. Haka dai Talatu ta yi ta qunsa wa amarya baqin ciki da takaici. Daga qarshe ma  ta  kuma yin qoqarin kashe amarya, ta hanyar zuba mata magani a abinci, amma Allah Ya sa ba ta ci abincin ba Talatu ta ci, magani ya koma kanta ta kuturce.

A fim xin *Mata Ko Baiwa* (2011, Royal Film Production, Kano) nan ma mun ga yadda Aisha ta shiga halin qunci da muzgunawa daga wajen mijinta Rabi'u da kuma kishiyarta Hajara. Aisha ta kasance tamkar baiwa a cikin gida. Ita take yin duk wani aiki na wahala a gidan. Ita take yin girkin abinci kullum, ta yi shara, ta yi wanke-wanke, ta kuma wanke kayan Hajara da na Rabi'u. Ba ta da hutu kwata-kwata. Ita kuwa Hajara na zaune ta miqe qafa, suna hira da miji, amma idan Aisha ta kawo abinci sai su shige xaki su cinye, su ce ta je ta kankari qanzo ta zuba mai da yaji ta ci. Aisha ba ta da kwana a gidan, domin tun da aka kai ta Rabi'u bai tava ko da shiga xakinta ba, ko da magana ba ta da ikon yi da mijinta, don idan ta yi masa magana ran Hajara zai vaci, shi kuwa da ran Hajara ya vaci gara ya rasa komai. Ko da zance suke yi da Hajara idan Aisha ta fito ta tsaya sai ya kama ta da faxa. Idan kishin Hajara ya motsa kuwa sai ta ce, ita kwata-kwata ba ta son ganin Aisha a gidan, don haka lallai Rabi'u ba zai shiga xakinta ba, idan har bai saki Aisha ba, da qyar zai sami yi shawo kanta, sannan hankalinsa ya kwanta. Dubi irin abin da ya faru:

Hajara *Wallahi yau ko za ka shiga cikin xakina ba, tun da na ce ka saki Aisha ka qi.*

Rabi'u *Allah ba ki haquri, ki yi haquri zan sake ta.*

Don haka kullum Aisha tana aiki tana zubar da hawaye na baqin-ciki, tana kuma roqon Allah ya yanke mata wannan zama na takaici da vacin rai. Ga irin abin da take faxa:

Aisha: *Allah ka fitar da ni daga cikin wannan gida, Allah Ka zava min mafi alkhairi.*

Amma duk da haka idan kishin Hajara ya kuma motsawa, sai ta ce:

Hajara: *Lallai Rabi'u ka zava ko ni ko ita.*

Rabi'u: *Ki yi haquri, Aisha lallai ki yi mata biyayya, ki yi mata duk abin da take so, ki kuma bi ta a hankali, duk abin da ta ce haka za a yi.*

Shi ma fim xin *Mace Ta Gari (*1991, Kamfanin Tumbin Giwa*)* ya fito tsantsar kishi, ya nuna yadda kishiya ke qoqarin quntata wa halin qaqa. Jamila ta kasance tana zaune da mijinta cikin kwanciyar da fahimtar juna. Don haka ma da ya ce zai yi mata kishiya ba ta ta hankalinta ba, sai ma ta ce, "Allah tabbatar da alkhairi, Allah sa arziki ce, Allah kuma Ya haxa kawunanmu". Don haka ko da amarya sai Jamila ta yi qoqarin yadda za ta ja ta a jiki su zauna lafiya, amma amarya Tsaiba abin ba haka yake ba. Domin kuwa ita, Tsaiba burinta uwargida Jamila da ta zo ta tarar. Don haka ta yi ta qulle-qullen

za ta raba Jamila da gidan. Akwai lokacin da Jamila ta haxu da madafi , don haka sai ta yi qoqarin ta kauce ta ba ta hanya, domin ta halin Tsaiba. Ai kuwa sai da Tsaiba ta taho da sauri ta ture Jamila da tsiya har qashinta na hannu ya tsage. Haka kuma ko unguwa Jamila sai Tsaiba ta shiga xakinta ta vata mata duk kayan amfaninta, don A wajen maigida ma haka kullum cikin shirya mata makirci take. lokacin da Jamila ta kama Tsaiba a cikin xakinta tana zuba mata don ta kore ta daga gidan, amma da Alhaji ya dawo, sai Tsaiba ta kuka take faxin:

Tsaiba: *Ni wallahi na gaji da zaman gidan nan kullum idan ba ka nan, sai su haxu ita da 'ya'yanta su yi min duka, kuma su ce idan na faxa maka gobe ma haka za su yi min, to yau har xakina aka je ana zuba min magani wai in haukace.*

Sannan duk ranar girkin Jamila, sai Tsaiba ta tsiri ciwo, ta hana su barci.

Idan kuwa ranar girkinta ne sai a tsiri murna da habaice-habaice da kissa iri-iri, ita dai Jamila ba ta cewa komai. Sai dai tana shan baqin ciki da vacin rai. Akwai ranar da Alhaji ya tafi zai kwanta kawai sai qarai ya ji ana cewa:

Tsaiba: *Wayyo! Wayyo!! Wayyo!!! Allah zan mutu ai min gafara.*

Nan da nan Alhaji ya fito, domin gaba xaya ta tashi hankalin mutan har masu gida da masu aiki, sai da ya fito kuma ta waske da cewa, faxuwa ta yi. Bayan nan, akwai lokacin da ta ce, wai tsoron xakinta take ji, wai idan tana barci sai ta ji ana cewa:

Tsaiba: *Tsaiba! Tsaiba!! Tsaiba!!!, ki tashi, mu ne baqaqaen Aljanu, an turo mu domin ki zama qawarmu*.

Ire-iren waxannan abubuwa Tsaiba ta rinqa yi domin ta hana Alhaji zuwa wurin Jamila, sai dai ita kaxai, duk da cewa haqar ta bai cim ma ruwa ba, amma Jamila ta xanxani bakin ciki da vacin rai.

Kishi dai ba tsakanin kishiyoyi ya tsaya ba, domin kuwa wata uwar daji surukarta take kishi, wanda hakan kan jefa gaba xayansu cikin takaici.

### 3. 5. 2. 2. Kishin Uwar Miji

Wani nau'in ganin qyashi da rashin jituwa ne da ke faruwa tsakanin mahaifiyar maigida da matarsa a sakamakon rashin fahimta. A wasu gidajen matsalar daga wajen matar ne dangane da irin riqon da ta yi wa uwar mijin nata, ma'ana irin halayyar da take nuna wa uwar mijin ko 'yan'uwansa shi zai sa uwar mijin ta qi ta. A wasu lokuta za a tarar matar da iyayenta da qanne har ma da qawayenta suna samun taimako da girmamawa daga wajen mijin 'yarsu, 'yar'uwarsu kuma qawarsu, amma nasa iyayen da dangin ba sa samun wani taimako ko sakewa a gidan. Idan uwar ta buqaci wani abu daga wajen xanta, sai matarsa ta yarda uwar za ta samu, in ba ta yarda ba, ba za [illegible] ba. A wasu gidajen kuma, duk irin qoqarin da matar za ta yi don ta wa uwar mijin da samun karvuwa a wajen dangin miji, sai su qi ba ta kai, rikicin yau daban na gobe daban. Wata ma daga aljihunta take yi uwar mijin duk wani abin bajinta in ya taso, amma a banza ba za ta ba, sai zagi da tsana da tsinuwa da baqaqen maganganu tsakaninsu matar, saboda qyashi da hassada da kishi, har wasu lokutan ma ka ji cewa, 'ai ni na san na haifa wa wata xa, kuma idan ya zo zan ba shi xauke ni ko matarsa'. Sannan ga yin katsalandan da sa ido kan duk

xansu yake yi wa matarsa. Wasu iyayen mijin har lave suke yi a qofar xansu da daddare, idan gidansu xaya ko kuma idan uwar ta kai kwana gidan xanta.

Ko kuma duk lokacin da matar xan za ta yi magana da shi, sai kawai uwar ta zo gun ta zauna. Irin waxannan halaye da makamantansu, su ke haifar da rashin jituwa a tsakanin matar xa da uwar miji (Bakura, 2003 : 48-49).

Babu shakka, idan al'amura suka kasance haka, babu maganar zaman lafiya da kwanciyar hankali tsakanin matar xa da uwar miji. Matar xa za ta kasance cikin baqin ciki da takaicin abin da uwar mijin ke yi mata, idan mai kunya ce, idan kuwa marar kunya ce, to sai ta dinga ramawa, daga nan kuma mutunci ya zube, shi kuwa mutunci madara ne idan ya zube ba ya kwasuwa, don haka zama ba zai yi daxi ba, daga qarshe sai dai a rabu. Haka ita ma uwar mijin idan Allah ya jarrabe ta da matar xa marar kunya mara mutunci, to dole za ta kasance cikin baqin ciki da takaici [illegible] abin da zai yi mata.

An fito da [illegible] a cikin fim xin *Daqasi* (2010, na Digital Sound, Jos), tsakanin Hajiya mahaifiyar Balarabe mijin Bilkisu, domin kuwa Hajiya ta kasance mai sa ido da jin haushi a kan abin da

da matarsa Bilkisu ke gudanarwa, kuma ba ta jin shayi ko nauyin ta yi magana a kan komai.

Ko zuwa gidan ta yi, ta tarar da su a xaki, musamman idan ta ga qofa a rufe, sai ta kama buga qofar, tana faxa, tana faxin:

Hajiya: *Wai wane irin barci kuke yi tun safe har Azahar.*

Idan kuwa ta bushi iska, sai ta tafi gidan xan nata, ta shiga madafi ta kama buxe-buxen kwanuka, wai tana neman abinci. Akwai ranar da Hajiya ta je ta kama Bilkisu da faxa tana faxin:

Hajiya: *Ba ni kuxin da xana ya ba ki ki ba ni*.

Bilkisu: *Ni fa bai ba ni kuxi ba*.

Hajiya: *Abin da mutane suke faxa gaskiya ne, 'yar matsiyata, mun auro irin varayi, komai a sace a kai gida, shinkafa a sace a kai gida, kuxin ma kin kai gida ke nan?*

Haka dai zama tsakanin Bilkisu da Hajiya ya kasance cikin rashin jin daxi, ita Hajiya tana jin haushin Bilkisu, gani take yi kamar duk abin da Balarabe ya samo ita yake kai wa, don haka ta kafa mata karan-tsana. Ita kuma Bilkisu na jin haushin abin da Hajiya ke yi mata a matsayinta na uwar mijinta, haka kowacce ta sha fama da takaici da vacin ran abin da ke faruwa.

Hakanan ma a fim xin *Uwar Miji* (2009, No Limit Concept, Jos) Sayyada matar Sarki ta xauki Mama mahaifiyar Sarki da daraja da kima, ba rashin kunya da tsiwa, amma ita kuma Mama kullum burinta ta jefa Sayyada cikin qunci da takaici, musamman tsakaninta da mijinta. Mama da Sayyada suna zaune a gida xaya ne, wannan ya ba Mama damar fito da kishinta qarara a kan Sayyada, domin Mama kishi take sosai da Sayyada, abin har ya kai idan Sayyada ta yi abinci sai Mama ta faki idonta ta qara mata gishiri a cikin abincin, idan kuma da safe ne sai ta zuba gishiri a cikin shayi. Mama dai ta zame wa Sayyada kamar kishiya, burinta kullum ta ji Sayyada da xanta Sarki na faxa. Duk da ta ga wannan bai yi mata ba, sai ta fara yi wa Sayyada gorin haihuwa saboda ta ga ta daxe ba ta haihu ba. Amma duk wannan bai sa Sayyada ta nuna damuwarta a fili ba, haka shi ma Sarki. Har cewa ta yi Sayyada ta yi cikin shege tun tana budurwa, amma Sayyada ba ta tanka mata ba, duk da cewa abin ya yi mata ciwo. Kullum Mama cikin shirya wa Sayyada makirci take, wata rana Mama ta ce, sai Sayyada ta fita ta nemo mata magani, amma da Sarki ya dawo ya tambayi Mama ina Sayyada sai ta gaya masa cewa, tun safe ta fita wajen samarinta, to amma saboda Sarki ya san halin Mama sai bai damu ba.

Da abin ya ci tura sai Mama ta ce, dole sai Sarki ya saki Sayyada, ko kuma ta tsine masa, don haka ba a san ransa ba ya sake ta, saki xaya. Mama ta auro masa wata matar. Amma zamansu bai daxe ba ya sake ta. Kasancewar Sarki yana mutuwar son Sayyada ya shawo kan Mama da qyar ta yarda ya dawo da Sayyada, duk da haka Mama ba ta daina kishinta ba. Al'amarin Allah Sayyada na dawowa ta sami juna biyu, amma Mama ba ta nuna farin cikinta ba, duk da irin gorin da take yi mata na rashin haihuwa, sai ta nuna jika kawai take buqata ba Sayyada ba. Dubi yadda Mama ta nuna tsantsar qiyayya da kishinta, a lokacin da aka kai Sayyada asibiti.

Mama: *Ni a fito min da jikana Sayyada kuwa Allah ya jiqanta*.

Haka dai Sayyada ta sha fama da takaici da kishin uwar miji, amma duk abin da take yi mata ba ta tava gaya mata magana marar daxi ba, sai duk wani vacin rai ta haxiye.

*Umarnin Uwa* (2011,T.M.A. Kano) shi ma fim ne da ya nuna uwar miji ke quntata wa matar xanta , inda Hajiya mahaifiyar Ibrahim kafa wa Madina karan-tsana ta kuma ce lallai sai Ibrahim ya saki ba laifin tsaye babu na zaune. Madina na yi wa mijinta biyayya yadda kamata, tana kuma yi wa ita ma Hajiya biyayya tana kyautata mata,

ta girmanta.  Amma Hajiya ta takura xan nata kan cewa, lallai sai ya matar tasa. Wata rana da tsakar dare ta buga musu qofa, cikin faxa faxin:

Hajiya: *Ina Madinan to ki fito ki bar gidan nan, munafuka, to Allah Ya kama ki Ya nuna min abin da kike nufin yi min a mafarki.*

Da qyar xan ya ba ta haquri ta bari gari ya waye. Da Ibrahim ya ga Hajiya ta matsa, sai ya ce da Madina ta tafi gida, amma ba sakinta ya yi ba. Da Hajiya ta fahimci ba sakinta ya yi ba, sai ta saka qanwarsa ta rubuta mata takardar saki, ta tafi gidan su Madina da kanta ta sami mahaifiyarta ta ba ta, ta ce, a madadin xanta. Ita kuwa mahaifiyar Madina ta ce:

*Na rabu irin tsananin kishin da kike da 'yata irin na jahilan iyayen mijin nan, don haka wannan takarda, takardar tsire ta fi ta daraja, har sai na tambayi Ibrahim idan shi ya saki matarsa.*

Da abin ya ci tura sai Ibrahim ya kama wa Madina gidan haya a voye, ba tare da sanin Hajiya ba. Amma sai da Hajiya ta bi diddigin da ta gane cewa suna tare, ta kuma yi yadda ta san gidan. Ranar nan suna zaune kawai sai Hajiya ta shigo ko sallama babu, ta yi sa'a kuwa Ibrahim ya sayo wa Madina kaya, nan fa ta kama faxa da zage-zage, tana faxin:

Hajiya: *Ibrahim ka raina ni, ka tare gindin matarka, ka bar ni can. To wannan kayan ba za ta saka ko xaya ba, tafiya zan yi da su. Ke kuma tsinanniya, kwaxayayya, jarababbiya, ba ki isa ki raba ni da xana ba mayya, zo ki fice ki tafi gidanku.*

Ta kuma ce idan Ibrahim ya bi ta za ta tsine masa. Da Ibrahim ya yasda zai vullo wa abin sai ya kai qarar Hajiya wajen mahaifiyarta kakarsa. Tawadda same ta ta yi mata magana, ta ce kuma lallai idan son xanta tarbi maganarta, to lallai ita ma ta bi maganarta,. Babu Hajiya za ta yadda don haka ta bi umarnin uwarta. Amma ta ce, tun da son ya zauna yarda wadda yake so, to ita ma sai ta auro masa wadda Don haka dole sai. dai ya yi wa Madina kishiya, ba za ta zauna ita ba, Ibrahim kawai saboda tsananin son da yake yi wa Madina ya ce, amince. ya

Madina kam ta gamu da takaicin uwar miji. Hajiya ta zava wa Ibrahim mata ya aura, ai kuwa amarya na zuwa ta kan Hajiya ta fara gwada tsiyar ta, don har sai da ta kai amarya ta yi wa Hajiya duka, Madina da qyar ta qwace Hajiya a hannun amarya.

Fim xin *Aljannar Mace* (2000, na kamfanin Tumbin Giwa, Kano) ma ya nuna iyayen miji masu nuna qiyayya da musgunawa da takura

matan ‘ya’yansu. An nuna halayen surukai marasa kyau da suke qwazzaba da matsi ga matan ‘ya’ya. Hajiya ita ce mahaifiyar Ishaq, kuma da matarsa Salma. Ishaq yana son matarsa matuqa, ita ma sosai da sosai. Suna zaune cikin so da qauna, har ya kasance yakan yi aikin gida ita kuma ya ce ta huta, musammam lokacin da ta laulayin ciki. Amma Hajiya ta xauki qiyayyar duniya ta xora wa Salma. hana ta sakat a rayuwarta ta aure. Takan zo gidan ta ci mutuncin hana su sakewa, kullum tana tafe. Girki sai ta ga dama za a yi a kai ma har ta kulle xakin girki da ma’ajiyar abincin gidan, wai ta rinqa musu da abinci daga gidanta. Duk irin abin da Hajiya ke yi wa Salma zagi da cin mutunci ba ta tava xaga kai ta kalle ta ba, ballantana ta daxi, sai dai abin yana damun ta, haquri kawai take yi. Har abin ya Salma jiki.

Duk irin waxannan abubuwa ba su ishi Hajiya ba sai da ta Ishaq yarinya wai sai ya qara aure. Don tana zargin ma wai ko maza take yi a waje idan ta fita aiki. A sanadiyyar wannan magana, hawan jini ya kama ta, ta kwanta a asibiti na tsawon watanni tana Amma kafin ta fito, sai da Hajiya ta saka Ishaq ya auri ‘yar qawarta, dai ya wulaqanta Salma. Amma ko da amarya Fati ta zo, sai ta riqe

da xanta Mujahid wanda Hajiya ta tsana, hannu biyu-biyu, kamar ita shi, komai ita take yi masa. Hajiya ta hana ta, amma ta qi ji, ta ce, ai xaya ne. Da ta ga haka, sai ta tafi gidan su Fati, take gaya wa su tashi a tsaye wai Salma ta mallake miji ta kuma mallake musu 'ya, abin da take so ake yi a gidan, don haka su nemi magani. Duk da ta wannan bai yi mata ba sai kuma ta faxa neman magani, har ta ci Salma, inda ta rinqa zuba wa Salma magani a abinci, amma daga da ta so ya faru ga Salma sai ya faxa kanta, ta ximauce, daga qarshe ita ma Fatima ta ci maganin da Hajiya ta zuba wa Salma a abinci, ta

Wani lokacin irin wannan qiyayya kan faxaxa har dangin miji, wato yayye ko qanne su ma su rinqa nuna wa matar xan'uwansu tsana da qiyayya da gaya mata baqaqen maganganu, musamman idan sun ga xan 'uwan nasu yana da abin hannu, kuma suna zaune da matar lafiya, sai su riqa qyashin ganin matar na cin arzikin xan fim xin. Hin hakan ta faru. umarsu. *Hannuka Mai Sanda, 2* (2010, T. M. A, Kano) inda Yaya Humaira da Khadija suka takura wa matarsa Xayyaba, ko tana xaki sai sun yi kiran ta sun ci mata mutunci, sun yi mata gori cewa ita kaxai a danginsu ta auri mai hali, ta zo za ta mallake musu dukiyar xan'uwa; akwai ranar da suka a gaba, suna dugure kai suna faxin:

Khadija da Humaira: *Kin bi malamai, kin bi bokaye, wake xaya ke kaxai a tarihin gidanku, kin zo ki mallake mana dukiyar xan'uwa, to yadda kika zo haka za ki koma.*

Yana kan gadon ciwo ma haka suka qare mata, sai dai ita ta mutu ta bar shi, mayya za ta cinye shi. Bayan da Allah ya yi wa Alhaji rasuwa ma ba su bar ta ba, ga irin abin da suke gaya mata:

> *Munafuka, kininbibiya, kin kashe mana xan'uwa, mayya sai a yi gaba, a koma qauye*.

**3. 5. 2. 3. Kishin Sauri / Faccala**

Wani nau'in kishin kuma, shi ne wanda ke faruwa tsakanin da ta qani, wato faccala. Shi wannan nau'i na hamayya na aukuwa tsakanin matan 'yan'uwa, wato matar wa da ta qani, irin wannan tana aukuwa ne idan xaya daga cikin mazajen ya xara xaya hali, shi yake taimakon xayan. Amma sai wanda ake taimakon ya fi zuciyar wa matarsa ta fuskar sutura da abinci; saboda irin waxannan abubuwa sai ka ga matar mai sukunin ta shiga jin haushi da qyashin matar xan'uwan, daga nan sai ta shiga neman yadda za ta toshe qofar taimakon da suke samu daga maigidanta, ko kuma ta quntata wa matar.

Irin wannan ya faru a cikin fim xin *Faccala* (2010, Unique Entertainment, Kano). Yaya da Auwalu wa ne da qani, Ita Salame matar Yaya na ganin cewar mijinta shi ne babba, don haka dole Jummala matar Auwalu ta ba ta girma. Ita kuma Jummala na ganin cewa mijinta shi ke yin duk wasu al'amura na gidan, don haka take qoqarin ta quntata wa Salame. Don haka sai ta rinqa gaya wa Salame maganganu da nuna mata qyashi kan abin da mijinta yake kawowa gidan, har ta kai tsakaninsu an fara samun gore-gore.

Jummala: *Mijinki ai yaron mijina ne*.

Salame: *Shi hatsin ai gonar mijina ake samo shi*.

Ko naman miya Auwalu ya sayo, sai Jummala ta xauke tana faxin; "Ai mijina ne ya sayo, in kin yi zuciya mijinki ya sayo miki mana". Ko da kuwa kuxi Salame ta ce Auwalu ya taimaka mata da su, sai Jummala ta yi baqin ciki. Jummala dai ta yi matuqar raina Salame, ganin cewa mijinta shi ke yin komai a gidan. Ko da sharar tsakar gida sai Jummala ta ce ba za ta yi ba, sai dai Salame ta yi, ai ita ba baiwarta ba ce, haka ma wanke-wanke da sauran aikace-aikacen gida. Jummala dai ta mayar da Salame tamkar yarinyar gida. Har abin ya kai ga Jummala na zargin Salame da cewa:

Jummala: *Mu'ujiza, kanin bizar, Allah ya kama ki, waki bi shi banxaki.*

Salame: *Sharrin ya tashi daga kaina ya koma kan mijinki, lallai tusa ba ta hura wuta.*

Shi kuwa Auwalu yana fitowa daga banxaki ya lulluve Jummala da faxa:

Auwalu: *Don kin ga ina rangwanta miki shi ne, har za ki yi zargin ina neman matar yayana, ba ki da amfani a wajena.*

Jummala: *Na ji ba ni da amfani a wajenka, in dai wannan ce za ka gane sharrin ha'inci da ta'addanci, ke kuma da sannu za ki gane shayi ruwa ne; da sannu za ki san sharrin xan shaixan.*

Irin rigingimun da suka yi ta faruwa tsakanin Jummala da Salame, ba su misaltuwa, har sai da ta kai ko magana ba su yi a tsakaninsu. Don haka sai maqwabta suka dinga shigowa ana haxa munafunci, aka yi ta gulmace-gulmace, har ta kai Jummala ba ta zuba wa Salame abinci. Salame ta shiga halin qaqa-nika-yi, babu abinci, ga shi mijinta ba ya gani, ya yi tafiya.

Haka shi ma shirin *Auwalu Sani Salisu* (2004, I. U. I. Electronic, Kano) masu shirya shirin sun fito da yadda irin wannan nau'i na kishi aukuwa tsakanin faccaloli. Auwalu da Sani da Salisu su ma 'yan'uwa mahaifansu xaya. A'isha ita ce matar Auwalu, Ridayya matar Sani, kuma matar Salisu, suna kuma zaune a gida xaya, kafin zuwan da A'isha da Ridayya na zaune lafiya har girki ma haxawa suke yi, wannan ta yi, gobe waccan ta yi, amma tun da Fadila ta zo gidan, sai ya qi daxi, duk gida ya rikice, domin ta shigo da rashin kunya da

mutunci da kishi da ganin qyashi. Kullum cikin fushi take ba ta yi wa magana. Ba ta da wani buri illa ta ga ta haddasa fitina a gidan, yawa takan sa Salisu a xaki ta rinqa nuna masa cewa, matan munafukai ne, ita kuma ba za ta yarda da munafunci ba. Wata rana da Ridayya suna zaune suna hira, amma sai Fadila ta yi zargin har take faxin:

Fadila: *Gulmata ake yi, ba fa tsoron ku nake yi ba , banzaye jakai, dabbobi ku je makaranta ku ilimantu.*

Ga shi ba ta son ta ga Salisu ya yi wa matan yayyensa ko 'ya'yansu alhairi, ko da qofar xakinta 'ya'yan su A'isha suka je sai ta doko su, wai za su vata mata waje. Idan kuwa ta ga su A'isha da sabon abu sai baqin ciki. Fadila dai ba ta raga wa kowa a gidan, kuma ba ta ganin kowa da kima da mutunci, ba babba ba yaro.

Don haka tun shigowar Fadila gidan sai A'isha da Ridayya wani hali na rashin jin daxi. Domin duk abin da suka yi, sai Fadila ta ita suke, daga nan kuma idan ba a yi sa'a ba, sai a kama faxa. Don jin kunyar kowa, ba ta kuma tsoron kowa. Haka Fadila ta takura su da Ridayya ko hirar ma da suke yi suka daina, don gudun kar ta gan

ta ce ana gulmar ta. Su kuma mazan da wani abu ya faru, sai su ce su ne manya, dole su dinga haquri da ita.

Fim xin *Hannunka Mai Sanda 1* (2011,T. M. A. Production, Kano), shi ma an gina shi ne kan wannan nau'i na kishi. Khadija da Ruqayya matan yayyen Adam ne mijin Kubra. Kuma suna zaune ne gida xaya har da iyayen mijinsu. Khadija da Ruqayya sai suka haxe wa Kubra kai, kwata-kwata ba sa harka da ita, ba su yi mata ko da magana. Sai dai su biyu su yi hirarsu, idan ma ta zo wajen sai su fashe da dariya, su dinga yi mata habaici. Don haka sai ta fara shiga damuwa, ta fara wuni a xaki ko waje za ta fito sai ta leqo idan ta ga ba sa kusa, sannan ta fito. Duk wannan bai yi musu ba, sai kuma suka fara gulmar cewa, Hajiya uwar mijnsu ta fi son Kubra, ana nuna musu bambanci don haka su ba za su yarda da wannan ba. Wannan dalili ya sa suka qara muzguna wa Kubra, suka kuma takura mata, suka hana ta fitowa ko da tsakar gida, suka hana ta sakat a gidan. Madafinsu xaya, amma sun hana ta shiga, ko da shayi ba ta da ikon ta dafa a madafi, domin idan suka gani sai su zubar.

Da Kubra kuma ta samu juna biyu, sai likita ya ce ta daina aikin nan fa kishi da baqin ciki suka kuma qaruwa, domin su suna ganin daxewarsu a xakin miji, babu wadda ta tava yin ko da vari, amma ita

zuwa ta sami ciki. Don haka sai suka fara shawarwarin yadda za su cikin. Wata rana Kubra ta fito tsakar gida sai Ruqayya ta kawo kai za wuce, Kubra ta kauce mata amma sai da Ruqayya ta matsa kusa da bangaje ta, da Kubra ta yi magana ta tsinka mata mari, ta kama ta da ta naushe ta a cikin, nan da nan jini ya tsinke mata, cikin ya zube, haka suke so. Don haka sai suka kama shewa da tafi.

Duk da suka ga wannan ba ta yi musu, sai kuma suka fara shigar mata xaki suna yi mata sata. Ba ta da sakat, ko da banxaki ta shiga, sai Ruqayya ta lallavo ta shigo mata xaki, ta yi mata sata. Wata rana Adam mijin Kubra ya ajiye abinsa a xakin, sai Ruqayya ta shiga ta xauke, nan fa ya dinga yi wa Kubra faxa, ta ce ita ba ta xauka ba, ya qi yarda. Haka suka yi ta tashin hankali har ya ce ta tafi gida. Su kuwa matan sun sami abin da suke so, sai murna. Kubra ta sha fama da takaici da vacin ran abin da su Ruqayya suke yi mata.

Daga qarshe saboda irin halin takurar da take ciki, sun matsa mata, shi kuma Adam baqin cikin an zubar masa da ciki, sai suka yi ta rigima da Kubra, har dai auren ya mutu ta tafi gidansu.

### 3. 6. Rashin Haihuwa

Yayin da wasu matan ke fama da kishi a qoqon ransu, wasu kuwa haihuwa suke nema ido rufe, don ko sa kuvuta daga habaice-habaice da gori daga wajen dangin miji.

Haihuwa hanya ce muhimmiya wajen yaxa zuriya da yawaita jama'a. Ta hanyar haihuwa ce al'umma ke bunqasa. Hausawa mutane ne masu son haihuwa kuma ba sa gajiya da ita komai yawan 'ya'yan da suka samu, har sai ta tsaya da kanta. A wurinsu, duk arziki ko sarauta ko muqamin da mutum  yake da shi idan ba shi da 'ya'ya banza ne. Kuma irin waxannan mutane sukan yi duk qoqarin da za su iya don su sami haihuwa domin samun magada, saboda haka ne ake yi wa haihuwa kirari da 'maganin mutuwa'(Ibrahim,  82:129).

Yawan jama'a a cikin al'umma  abin tutiya ne ga tattalin arziki da siyasa, musamman ga Bahaushe mai tsarin iyali 'mai yaxo'. Yara a jama'a martaba ne ga maigida domin taimakawar yaran ga harkokin musamman wajen aikin noma. Wata fa'idar ta haihuwa ita ce, adon ce mai bai wa mutum damar jin ya ci ribar zamansa na duniya. Tana xan'Adam  farin ciki a rayuwa da kuma gamsuwa. Hausawa kan ce ya 'shuri arewa amma ya bar 'ya'ya rasuwa ya yi ba mutuwa ba', akwai waxanda za su gaje shi. Haka kuma haihuwa tana kafa tushen

zumunta da qarfafa wanda ke tsakani da kuma kyautata soyayya da danqon aure tsakanin ma’aurata.

Don haka babban burin ma’aurata samun zuriya, wato su sami ‘ya’yansu nasu na kansu. Sanin kowa ne Allah ne mai bayar da haihuwa ga wanda Ya so, Ya kuma hana wanda Ya so, ba domin ya yi masa wani laifi ba, amma duk da haka, a al’adar Hausawa, al’amarin na xaukan wani salon jefa matar da ba ta haihu ba cikin takaici da bakin ciki.

Wani lokacin kuma ba rashin haihuwar ne ke vata wa mace rai ba, sai dai yadda ake tsangwamar da munanan kalamai da kuma yi mata habaice-habaice da kuma gori. Irin waxannan mata kan fuskanci matsi daga wajen iyayen miji da ‘yan’uwansa da kishiyoyi, wani lokaci ma har da maigida. Idan kuwa ita kaxai ce matarsa, akan matsa masa ya qara aure, wanda idan har kishiyar ta zo ta haihu, ai shi ke nan, sai abin da ya yi gaba dangane da tsana da habaici da gori. Ana yi wa macen da ba ta tava haihuwa ba, habaici iri-iri, wani lokaci sai ka ji an ce, “ai wance babu katavus, sai dai cika shadda (masai) da kashi”, ko kuma ka ji an ce, “a, to, idan fitsari banza ne, kaza tayi magani mana”.

Irin hakan ce ta faru ga Humaira a cikin fim xin *Manda* (2005, Dararrafe, Kano). Hajiya ita ce mahaifiyar Mukhtar mijin Humaira, sun

kasance suna zaune cikin kwanciyar hankali da nuna wa juna ma Hajiya tana son surukar tata, amma da ta fahimci cewa Humaira lokaci mai tsawo ba tare da ta haihu ba, sai ta fara nuna damuwarta, tsanar ta da tsangwamar ta. Da abin ya yi tsanani ma, sai Hajiya ta qauye ta biya kuxin sadaki ta auro wa Mukhtar mata, ba tare da ta yi amfani da damarta ta uwa, ta kuma ce an yi an gama.

Dubi lokacin da Hajiya ta shigo, Humaira ta tashi da gudu ta tare ta kamar yadda ta saba, tana da faxin:

Humaira: *Mama oyoyo! Mama oyoyo!!*

Hajiya: *(ta hantare ta ta ture ta) Mama ta qare daga yau, shekara da shekaru kina gidan nan ba abin da kika sani, sai dai ki ci, ki yi bayan gida.*

Humaira: *(ta durqusa) Mama yau lafiya, me na yi miki* ?

Mama: *(ta ture ta) Kullum sai dai in shigo gidan nan ki zo kina damu na da Mama, Mama, ba haihuwa, to kin gan ta nan, ita na auro ta zo ta haifo min jikoki in dunga zuwa da ledar goba ina rarraba masu. (Ta ci gaba da cewa,) Sadiya tashi ki zauna nan gidanki ne domin gidan mijinki ne*

Duk da cewa, Mukhtar ba ya son Sadiya, amma haka ya ci gaba da zama da ita a gidan, don ba yadda zai yi. Sadiya da Hajiya kuwa, suka ci gaba da yi wa Humaira wulaqanci da habaice-habaice, har ta kai ga ko abinci ba sa ba ta.

Haka Humaira ta ci gaba da fuskantar qunci da habaice-habaice daga wajen Mama da Sadiya, inda har Mama ta sha alwashin sai ta raba Humaira da gidan Mukhtar. Duk ranar da vacin rai ya tasar wa Humaira, qanwarta Nafisa ke qoqarin kwantar mata da hankali da yi mata nasiha da cewa, komai ya yi zafi maganinsa Allah. Daga qarshe dai sai da Hajiya ta kori Humaira daga gidan kan ba ta haihuwa ba.

Haka ma Maryam ta haxu da irin wannan takaici daga wajen Umma (uwar mijnta) a cikin fim xin *Kumallon Mata* ( 2010, 3star Movie Jos), domin kuwa, Umma ta kasa yarda da qaddarar da Allah Ya xora wa Maryam  na rashin haihuwa. Ga irin abin da take faxi:

Umma: *Yau ka ji suna gidan wannan, gobe ka ji gidan wancan, amma ban da gidan xana don haka, lallai Maryam ta je gida iyayenta su nema mata maganin haihuwa, idan ba haka ba kuwa ka qara aure, don so nake yadda na haife ka, kai ma ka haifa.*

Tun daga wannan rana Maryam ta shiga cikin takaici da tashin hankali, marar misali, domin ta san idan har aka auro wata ta zo ta haihu, to fa kashinta ya bushe, musamman a wurin Umma. Hakan kuwa aka yi, ya auro Zainab, watanni kaxan ta sami juna biyu, Umma da xanta sai farin ciki suke yi, za su sami qaruwa. Daga maigida har mahaifiyarsa suka jaya wa Maryam baya. Maryam kuwa hankalinta ya daxa tashi, saboda irin matsin da take fuskanta tun ma kafin Zainab ta juye, idan kuma Zainb ta juye abin da ke cikinta, sai Allah ke nan. Don haka sai zuciya ta xebe Maryam ta yi qoqarin kashe kanta, inda ta sha guba. Amma Allah Ya kiyaye ba ta mutu ba.

Wani lokacin kuma miji ko xan'uwa kan xauki xaya daga cikin 'ya'yansa, ya ba matar da ba ta haihuwa riqo, a nan ma ba ta tsira ba, domin za a riqa cewa za ta raba xan da mahaifiyarsa, ko ma rana tsaka a zo a qwace shi, bayan sun shaqu.

Irin haka ce kuwa ta faru a Fim xin *Laifin Daxi* (2011, G.Top, fim ne mai cike da ban tausayi kan abin da Anti Zainab ta yi wa sanadiyyar rashin haihuwa. Anti Zainab da Samira matar wa da qani Zainab Allah Ya ba ta 'ya'ya har biyu, ita kuwa Samira ba ta haihu ba, ma ya tabbatar mata da cewa ba za ta haihu ba, saboda wasu dalilai.

Zamansu gwanin sha'awa cikin jin daxi, don haka sai Anti Zainab ta 'yarta mai suna Zainab, tun yarinyar tana da kwana takwas da mallaka wa Samira ta ce, ta ba ta har abada Allah Shi ne shaida, don ma ta ba ta ita tun tana jaririya, domin ko ta girma ta xauka cewa, mahaifiyarta. Samira ta kama murna, ta rasa irin godiyar da za ta yi Zainab. Samira da mijinta suka ci gaba da rainon yarinya kamar su haife ta, har ta isa makaranta suka saka ta, ta taso da basira, ta riqa kyaututtuka na yabo da qwazo.

Har zuwa wannan lokaci Zainab (suna kiranta Anti) ba ta san Samira ba ita ta haife ta ba. Sun yi matuqar shaquwa da juna. Amma sami wata mata daga cikin 'ya'uwan Anti Zainab ta zo mata da tsiya cewa, wai yarinyar da suka ba  Samira, ga shi tun da suka ba arzikinsu ya ja baya, su kuwa su Samira sai samun alheri suke yi. maza su karvo 'yarsu ko arzikinsu ya dawo kamar da. Da farko duk waxannan maganganu Anti Zainab ba ta yarda da su ba, amma daga ta fara ganin cewa, ai kuwa  haka ne. Saboda da mijinta yana aiki amma yanzu babu. Sannan shi kuma mijin Samira wato qanin mijinta ya sami aiki babba, da kuwa ba shi da aiki, kuma 'yarta Anti ta ciwo miliyan xaya. Don haka  sai ta yarda da wannan magana. Rana a

sai Anti Zainab ta je gidan su Samira, ta ce, za ta tafi da ‘yar ta yi mamaki, suka ce mata bari a yi hutu sai a kawo ta, ta ce a’a ai ita ta xau ‘yarta gaba xaya. Ai kuwa da jin waxannan kalamai sai faxi sumammiya, ba ta farka ba sai bayan kwana biyu ta farka, ta gadon asibiti.

Takaicin mace a al’ummar Hausawa bai tsaya kan rashin haihuwa ba kawai, domin mai haihuwar ‘ya’ya mata ma ba a qyale ta ba, wannan shi ne “gaba kura baya sayaki”.

### 3. 7. Haihuwar ‘Ya’ya Mata

Kamar yadda aka bayyana a baya, rashin haihuwa ga mace a Hausawa sabodar kan jefa ta cikin takaici da vacin rai, saboda irin habaice-da tsangwama da za ta fuskanta daga wajen al’umma, musamman miji. To ashe ba a nan matsalar ta tsaya ba, domin kuwa ko da mace haihuwar idan ta cika haihuwar ‘ya’ya mata, shi ma an gudu ne, ba a domin za a riqa kyarar ta a cikin al’umma. A tunanin Bahaushe ‘ya’ya sun fi ‘ya’ya mata, domin yana ganin xa namiji shi ne zai gaje shi, ita ‘ya mace ‘yar gidan wani ce, domin duk daxewar ‘ya’ya mata a gidan iyayensu, wata rana za a aurar da su. Wasu kuwa ba sa son ‘ya’ya

saboda irin tsarabe-tsaraben da ke tattare da su, tun suna yara, har lokacin aurensu, irin kuxin da za a riqa kashe mata na kayan qyale-lokacin da ta zama budurwa, da na kayan xaki a lokacin aurenta. aurar da ita hidima ba ta qare ba, domin kuwa duk lokacin da ta ma sai an yi mata hidima, ba kuma a haihuwar farko abin zai tsaya lokacin da ta haihu sai an yi mata hidimomi. Bayan wannan wasu na cewa 'ya mace na iya jawo musu abin kunya, idan ba mai kamun kai

Waxannan wasu ne daga cikin dalilan da suka sa mazan Hausawa ba su son haihuwar 'ya'ya mata. Masu iya magana na cewa, "inda baki ya karkata, nan miyau kan zuba", haka yake domin ganin yadda mazan Hausawa suka fi son haihuwar 'ya'ya maza, sai su ma matan suka fi son haihuwar 'ya'ya maza maimakon mata, don ko sa sami qarin so daga wajen mazajensu. Kuma idan mijin mai muqamin sarauta ne, tana tunanin nan gaba xanta zai gaji sarauta. Haka kuma duk matar da ke haihuwar 'ya'ya maza, ita ke da gida, domin sai ta fi sauran matan samun karvuwa a wajen maigida, ita ce, "rijiya da duwatsu fasa gugar mahassada", wato ta gagari kowa, domin ta sami karvuwa ga mijinta.

Dubi irin abin da ya faru a fim xin *Tagwayen Gida* ( 2010, Global Concept, Kano) wanda ya nuna yadda Fulani matar Sarki ta fi

haihuwar xa namiji, domin Fulani  ta rufe idonta kan cewa, lallai ita ta haifa  ba mace ba.  Fulani dai sun haihu da Baraka (matar talakan rana xaya a asibiti xaya, kuma lokaci xaya. Fulani ta haifi 'ya mace, kuma Baraka ta haifi xa namiji. Sai aka kai jariran xakin raino,  kafin a da jariran, sai da  aka nuna wa kowace abin da ta haifa ta gani, kuma shaida. Amma daga bisani sai Fulani ta ce, ita lallai xa namiji ta haifa mace ba. Don haka aka ce a kai jaririn a gwada su, don a raba gama gwajin Fulani ta rinqa damun Sarki kan lallai ita ta haifi namiji, baki a karvo mata xanta don kada talaka ya shayar mata da xa, ya tarbiyantar da shi. Har idan an je yi mata barka, takan ce:

Fulani: *Jaje za a yi min ba barka ba, saboda na haifi namiji, amma an musanya min an ba ni mace.*

Alhali kuwa ita kanta ta san mace ta haifa, amma ta rufe idonta saboda kwaxayin ya gaji sarauta ta ce, namiji ta haifa. Inda har ta dinga tayar da hankalinta kan cewa za a musanya mata xa.

Saboda yadda mazan Hausawa suke gudun a haifa musu ya sa suke da wata karin magana mai cewa, "an dava mace, ta haifi wato suna nufin an qara samun wata  wahalar da ba sa so. Akan jituwa da tsangwama daga miji idan har mace tana haihuwar 'ya'ya

kuma ta sake xaukar wani cikin. A tunaninsa haihuwar ‘ya’ya mata jininta yake, don yana ganin wannan cikin ma macen za ta haifa.

Fim xin *Mujiya* (2004, Madobi Enterprises, Kano) ya fito da yadda haihuwar ‘ya’ya mata kan jefa mata cikin vacin-rai a wajen wasu mazajen. Saboda an nuna irin halin vacin-rai da takaicin da matar Ibro ta shiga ciki. Ibro ya nuna wa matarsa tsantsar wulaqanci da tsana da qiyayya saboda tana haifa masa ‘ya’ya mata, da ta kuma samun wani cikin, sai fa ya matsa mata, ya takura ta kan cewa lallai kar ta yadda ta kuma haifo masa mace, sai dai ta haifi xa namiji. Har yake gaya mata cewa, in dai har ta sake ta kuma haihuwar mace, to tana haihuwa ta zauna a kanta, shi ba ya so. Haka ya ci gaba da matsa mata, duk sanda ya shigo gidan sai ya yi mata gargaxi da cewa:

Ibro: *Na gaya miki kar ki yarda ki haifo mace, idan kuwa kika haifo mace ni da ke ne, kuma idan har kin ga mace ce ki zauna a kanta, na fa gaya miki, a yi qoqari fa, a haifo min xa namiji.*

Wannan abu na Ibro na xaga wa matar hankali, yana jefa ta cikin takaici, ga nauyin ciki ga matsawa, da wanne za ta ji? Tana qoqarin fahimtar da shi cewa, haihuwar ‘ya’ya matan ba fa daga gare ta ba Allah ne, kuma wannan karon ma ba ta da ikon canza abin da Allah

nufi, amma ko sauraron ta ba ya yi, shi dai kawai a haifa masa xa Wannan ba qaramin jahilci ba ne, domin dai ba ita take ba kanta ba, ma ba ta san abin da ke cikin nata ba. Har sai da ta kai ya canza wa suna yana kiran ta da 'mujiya, mai baqin jini', saboda baqin jinin da ta wurinsa na haihuwar 'ya'ya mata, wani lokacin har waqa yakan yi mujiya mai baqin jini, mai idanuwa a loko. Mutanan gari ma har sun shi cewa, ba ya son 'ya'ya mata don haka duk inda ya shiga sai ka ji cewa:

*Mutane:* *Allah Ya ba ka xa namiji*.

Ibro: *Ko tsinanne ne, ko shege ne*.

Haka matar nan ta sha fama da baqin-ciki da takaici, daga qarshe ta haifi xa namijin da bai amfane shi ba.

Akwai kirarin da ake yi wa 'ya'ya mata a al'ummar Hausawa, "gwamma da ku da rashin ku 'ya'ya mata", wato sun fi babu. Wannan kirari na nuna qasqancin 'ya'ya mata kan 'ya'ya maza.

Matar da ke haihuwar 'ya'ya mata har ila yau, kan fuskanci tsana da tsangwama daga wajen dangin miji, musamma uwar miji, wani lokacin ma har a buqaci maigida ya qara aure, ba don komai ba, sai don matarsa na haihuwar 'ya'ya mata, a ganinsu wata za ta zo ta haifa musu xa namiji.

Irin haka ta faru a cikin fim xin *Jari* (2009, na H. R. B. Kaduna), inda Fatima ta fuskanci irin wannan vacin rai da tsana da tsangwama daga wajen uwar mijnta Baba mai aya, saboda ta haifi 'ya'ya mata har shida ba ta tava haihuwar xa namiji ba. Nan fa Baba ta ce, ina wutar saka Fatima, tun da ta tara wa xanta taron tsintsiya ba shara, kullum maganar Baba ba ta wuce Ali ya qara aure, ya auro mai haihuwar 'ya'ya maza, tun da ita mata take haifa. Wata rana Baba ta kai ziyara gidan xan nata, sai Fatima ta karve ta da murna tana faxin:

Fatima: *Sannu da zuwa Baba, shigo, shigo mana Baba*.

Baba: *(ta tsaya a waje) Ai idan kin gan ni a lahira kai ni akai, ai xakinki yadda kika san jahannama haka nake ganin sa, tun da ke kin hana xana aure, ke kuma kin qi ki haifo xa namiji. Gara ki bar shi ya yi aure, tun da qwayayenki na haifo'ya'ya mata ne.*

Akwai ranar da Baba ta je ta tarar da Fatima da yaran a tsakar gida suna cin abinci, duk ta sa 'ya'yanta a gaba, amma me zai fito daga bakin

Baba: *Ke 'ya'ya matan har wani tutiya kike da 'ya'ya mata, to ki haifo namiji mana, qaryar banza.*

Yaran kuwa da Baba ta yi sallama a gidan za su tafi da gudu, suna mata sannu da zuwa, amma sai ta ture su tana faxin:

Baba: *Ku matsa ku ba ni guri, tarkacen kawai, aikin banza kana ta fama da wahalarsu , kana kashe musu kuxinka a banza kan waxannan da sun yi aure shi kenan.*

Haka Baba ta ci gaba ta matsa wa Fatima, da sa ta takaici, shi kuwa Ali duk wannan abu da Baba ke yi ba ya so, domin kuwa yana son matarsa, yana kuma son 'ya'ya matan da Allah Ya ba shi, yana kuma kyautata musu. Rannan da abin ya ciwo Baba, sai ta je ta sami Fatima ta ce mata:

Baba: *Yau na zo xaukar mataki na qarshe idan ba zai sake ki ba to ni na sake ki, xana ne, na kuma isa.*

Haka Fatima ta tattara kayanta da 'ya'yanta mata ta bar gida, shi kansa Ali ba a son ransa ba, don ba yadda zai yi ne. Wani abin mamaki shi ne yadda Baba ta manta da cewa, ita ma fa mace ce, kuma haifo ta aka yi, sannan kuma Allah Shi ke bayar da haihuwa, kuma Ya ba ka mace ko namiji, ba tare da Ya yi shawara da kai ba.

**3. 8. Kammalawa**

Wannan babi shi ne wanda ya fara fexe ginshiqin abin da wannan nazari ya fuskanta. An yi nazarin irin takaicin da ke ci wa matan Hausawa tuwo a qwarya a zamantakewar iyali ta yau da kullum. An yi amfani da fina-finan Hausa a matsayin madubin da ya fito da irin takaicin da mata ke ciki a  wannan rayuwa. An dubi matsaloli waxanda ke aukuwa a zamantakewar iyali da suka haxa da yanayin zamantakewar miji da mata da kishi, sannan an  kuma yi nazarin yadda a al'adar Bahaushe, akan xauka kuma a yafa, kan abin da Allah ne kaxai ke da iko kansa. Ba wani abu ba ne illa takaicin da matan da ba su haihu ba suke ji da kuma masu haihuwar 'ya'ya mata. An riqa kawo fina-finan Hausa iri daban-daban, masu fito da irin takaicin da ake nazari, don hujjar hakan.

# BABI NA HUXU : TAKAICIN YARAN MATA

## 4. 0. Gabatarwa

A babin da ya gabata an yi tsokaci ne kan matsayin mace a wajen wasu al'ummu da addinai, an nuna yadda wasu al'ummu suka qasqantar da mata, ba su xauke su da muhimmanci ba. Har sai da addinin Musulunci ya zo sannan Allah (S.W.T.) ya yi umarni dangane da matsayin mace a cikin Alqur'ani mai girma. Sannan aka dubi matsayinta a wannan zamani, da kuma irin matsayin da mata kan fito a fina-finan Hausa . Sannan aka dubi irin takaicin da ke ci wa manyan mata tuwo a qwarya a zamantakewar iyali ta yau da kullum , a wannan babi kuma za a dubi irin takaicin da yaran mata ke fama da shi. Ba wai manyan mata masu aure ne kaxai ke fama da takaici ba a wannan rayuwar, su ma yaran mata akwai ire-iren abubuwan da ke damun su. Wasu daga cikin waxannan abubuwa, yaran mata su ke ja wa kansu da kansu, wato su ne silar haddasa takaicin ga kawunansu, waxansu kuma wasu kan ja musu. Daga cikin abubuwan da za a duba akwai kwaxayi da son abin duniya da quntatawar matar uba ga 'ya'yan miji da auren dole da kuma yaudarar samari ga 'yammata.

## 4.1. Kwaxayi Da Son Abin Duniya

Masu iya magana na cewa,

"kwaxayi mabuxin wahala".

Qamusun Hausa (2006 : 260) ya ba da ma'anar kwaxayi da tsananin son wani abu, musamman abin da za a ci ko za a sha, wanda mutum bai mallaka ba. Ko kuma son karvar wani abu cikin sauqi a wajen mutane. Kwaxayi abu ne da yake shiga zuciya musamman dangane da nama, kuxi da mata (Bargery, 1934 : 667).

Tsananin nuna sha'awa game da wani abu (na duniya) shi ne kwaxayi. Nuna sha'awa a nan ba irin wanda mutum zai ga abu ya ba shi sha'awa ya bar shi yadda ya gan shi hankali kwance ba ne, a'a sha'awa wadda mutum kan nuna maitarsa a fili har sai ya ga ya kasance da abin da yake da sha'awa ko yake so (Mohammed, 2011: 127). Kwaxayi da son sai an sami abin duniya a lokaci guda, ba xabi'a ba ce domin akwai illolin da suke haifarwa. Hausawa ma na da karin magana, "in da kwaxayi da wulaqanci", ma'ana wanda ke da to fa zai haxu da wulaqanci da takaici, wani lokacin ma har ya yi rabuwarsa da duniya. Mafi yawan mata suna da kwaxayi da son abin

ko dai don su yi takara da tsararsu, ko don a ce sun fi wance, ko kuma don son su tara abin duniya. A wajen aure ma, mafi yawan lokaci, mata za su so mutum ne, idan yana da abin hannunsa, kamar yadda Hausawa ke cewa, 'hannu mai masqi shi ake bi da lasa'. Wani lokaci wannan halayya ta mata ta kwaxayi kan haddasa musu rashin samun mazan aure da wuri ko kuma ma ta sa su shiga cikin karuwanci, ko kuma ta jefa su halin qaqa-ni ka- yi.

Fim xin *Tsautsayin Takaba* (1999, Dukku Production,Kano) fim ne da ya nuna Bebi sun daxe da saurayinta, kuma masoyinta Abdul suna soyayya, amma lokaci guda saboda kwaxayi da son abin duniya ta rabu da shi, saboda ta sami wanda ya fi shi hali, wato wani Bature Mr. Kent. Hakan ya kai ta ya baro ta. Ganin kitsen da Bebi ta yi wa rogo ya ja mata faxawa halin qaqa-nika-yi. Mr. Kent ya xauke mata komai, don haka Bebi ta qi tsayawa ta kula da karatunta, har aka kora ta daga makaranta. Ta koma gida ga mahaifinta ya kore ta. Sai Mr. Kent ya kama mata gida suka ci gaba da holewarsu. Babu abin da ba ya yi mata. Bebi da Mr. Kent sun daxe a wannan hali.

Daga qarshe dai ya gudu ya bar Bebi, abin duk da ya mallaka jami'an tsaro suka qwace, ga shi ya saka mata cutar qanjamau. Haka

cikin damuwa da takaici, ga rashin abin hannu, ga cuta, ga shi kuma kowa ya guje ta, haka Bebi ta zauna har ta mutu.

Shi ma fim xin *'Yanmata* (1999, na Fine Focus Video Production, Kano), ya fito da yadda kwaxayi kan jefa mata cikin quncin rayuwa da takaici. Amina tana da saurayinta Kabir wanda suka yi alqawarin aure. Amma lokaci guda wata qawarta Ummi ta hilace ta, ta sauya mata ra'ayi ta haxa ta da Alhaji Abba saurayin Maikuxi, ta rinqa kushe Kabir kamar haka:

Ummi: *Yanzu ke Amina Kabir za ki aura, Amina wallahi kina ba ni mamaki, yanzu wa ke yin soyayya da samari irin su Kabir, ai ba a soyayya sai da mai mota da kuma wanda ya mallaki sama da miliyan xaya.*

Alhaji Abba ya fara xaukar Amina a mota suna fita yawon shaqatawa, sayayya a kan kari, xinkuna iri-iri. Da Amina ta ga kuxi nan fa ta juya wa Kabir baya, ta rinqa wulaqanta shi, tana gaya masa maganganu, shi kuwa da ya ga haka sai ya ja jikinsa ya rabu da ita. Amina ta ci gaba da fantamawarta da Alhaji Abba. Da mahaifin Amina ya lura da irin abin da ke faruwa, sai ya kira mahaifiyarta, yake gaya mata cewa:

Alhaji: *Yanzu Hajiya kina kallon yarinyar nan, yawan fitar nan da take yi ba na so.*

Hajiya: *Haba Alhaji, to sai ta zauna a gida, budurwa ai sai da yawo.*

Alhaji: *To ni dai ba ruwana*

Hajiya: *Ka ce man ba ruwanka, za a kulle ta a gida ne a hana ta fita* ?

Hajiya dai ta mara wa Amina baya, saboda tana kawo mata kuxi. Don haka Amina ta ci gaba da harkarta da Alhaji Abba. Bayan sun xau tsawon lokaci, yana yi mata hidimomi, ita kuma ta mallaka masa kanta, a qarshe dai ya yi mata ciki. Bayan ta sanar da shi kuma ya ce shi ba ruwansa ta tafi ta ba shi wuri, ta kuma san yadda za ta yi da cikin don ba nasa ba ne. Haka Amina ta gamu da wannan abin takaici, saboda kwaxayin abin duniya.

Fim xin *Butulci* (1999, Xanfodiyo Production, Sokoto) ya nuna Maryam ta shiga halin qunci tun tana qaramarta, domin kuwa sun birni ita da iyayenta da qannenta, za su qauye, sai varayi suka tare suka kashe duk wanda yake cikin motar, sai ita kaxai ta tsira. gudu cikin daji ta zauna, inda Allah Ya haxa ta da Sadiq wanda ya ta ya kai ta gidansu wajen mahaifiyarsa. Bayan ta huta ne ta ba su yadda aka yi ta zo daji. Sadik ya ce, ta zauna tare da su, amma rasu shi kuma lebura ne don haka zai iya qoqarinsa ya riqe ta. Suna

haka, har soyayya ta qullu tsakanin Maryam da Sadik, har ma da alqawarin aure. Kwatsam sai Maryam ta haxu da Alhaji Kabir ya hure mata kunne, inda har ta nemi ta manta da abin kirkin da Sadik ya yi mata. Sai ta fara yin abubuwa na rashin xa'a, ta qi jin maganar kowa, sai abin da ta sa kanta. Har ma Sadik yana yi wa Mama magana a kai;

Sadik: *Yanzu Mama daidai ne a ce wai Maryam tana fita a motar Alhaji Kabir, abokaina har sun fara yin Magana* ?

Maryam: *Wai ni magana ake yi ne?*

Sadik: *I, maganarki ake yi, me ye tsakaninki da Alhaji Kabir?*

Maryam: *Wannan bai shafe ka ba.*

Mama: *Ni ba wannan ne yake damu na ba, yawace-yawacen da take yi safe da yamma.*

Maryam: *Ni ba inda nake zuwa.*

Sadik: *Wato Mama ta yi miki qarya ko?*

Maryam: *I, qarya ake yi mini, tun da ban yi ba, zan tafi gidan Alhaji Kabir da yamma, zan turo a kwasar mini kayana, saura kuma a yi mini sata*.

Kwaxayi mabuxin wahala, Maryam dai kwaxayin abin duniya ya ruxe ta har ta vata da iyayen da ta samu suka rufa mata asiri, bayan ta rasa iyayenta na asali. Bayan ta koma gidan Alhaji Kabir ba daxewa, sai ‘yansanda suka zo gidan bincike, ashe Alhaji Kabir shugaban ‘yan fashi ne, yaransa ne ma suka kashe mata iyaye ba ta sani ba, don haka aka yi gaba da shi da duk abin da ya mallaka. Nan fa Maryam ido ya raina fata, ta rasa wajen zuwa, ta dawo gidan su Sadik, amma suka ce a’a.

**4. 2. Quntatawar Matar Uba ga ‘Ya’Yan Miji**

Wani nau’in quntatawa ne da ganin qyashi da qyama da matar gida kan nuna ga ‘ya’yan mijinta musamman ma waxanda mahaifiyarsu ta rasu ko kuma ta fita daga gidan. Irin waxannan mata quntata wa ‘ya’yan miji ta hanyoyi da dama. Ko ta hanyar hana su duka ko faxa ko zagi ko kuma saka su aikin wahala. Wani lokacin ma matar gida ta fahimci akwai kyakkyawar dangantaka a tsakanin ‘ya’yansa wato yana kula da su yadda ya kamata, sai ta fara qulle-makirci yadda za a sami rashin jituwa tsakanin maigida da ‘ya’yansa. wasu lokutan kuma matan kan yi qoqarin dakushe duk wani abin

zai faru ga ‘ya’yan maigidan, musamman ma ta fuskar aure wanda ake ganin yarinyar za ta huta, sai a yi qoqarin kawo cikas tare da nuna cewa auren ba zai zama alheri ga yarinyar ba. Haka shi ma maigidan za a hure masa kunne domin ya nuna rashin amincewarsa da wanda ke neman ‘yarsa da auren. Idan kuwa ya qi yarda ya mara wa matar gidan baya, sai ta shiga neman bokaye don ganin auren bai yiwu ba.

Irin haka ne ya faru ga Alawiyya a cikin fim xin *Adabiyya* (2010, na Nasara Global Concept Ltd, Kano). Mahaifiyar Alawiyya dai ta rasu, tana hannun matar babanta ne Iya, ita ma kuma tana da ‘ya Adabiyya. Amma tana nuna bambanci a tsakaninsu, duk wani aike da aiki na wahala ita ke yi a gidan. Komai dare haka za ta tura Alawiyya daji samo itacen girki, ita kuwa Adabiyya tana gida a zaune. Shi kuwa mahaifin su Alawiyya sai abin da matarsa Iya ta ce masa, domin ba ya ganin laifinta ko kaxan, kuma duk irin azabar da take ganawa Alawiyya ba ya magana.

Ana cikin haka, Allah Ya fito wa da Alawiyya saurayi, kuma mai xan mutunci, amma ita Adabiyya babu wanda ke sallama da ita, nan ta fara nuna hassada da baqin ciki. Duk lokacin da Ahlan ya zo zance

Alawiyya, sai a turo Adabiyya, ko kuma a ce Alawiyyar ba ta nan, ko a ce tana aiki. Wata rana Ahlan ya zo zance wajen Alawiyya suna tsaye, sai ga Adabiyya ta zo shiga gida, nan fa ta buga uban tsaki haxi da harara, tana faxin:

Adabiyya: *Amma abin ko tsari babu, ko da yake ba wani abu ba ne, shi ma mai neman bai san abin da ya dace da shi ba.*

Dubi inda kishin Iya ya fito qarara, lokacin da Alawiyya take gaya mata cewa Ahlan ya ce zai turo iyayensa, amma don baqin ciki sai ta kama ta da faxa, ta qwallawa Mahaifinta kira:

Iya: *Malam ! Malam !! Sai ka fito, wai wannan yarinyar ce har ta iya buxar bakinta take gaya min wai Ahlan zai turo, sai ki yi masa bayani, (ta ci gaba da cewa,) don rashin kunya shi ne, ta tare ni da maganar aure, don kin raina ni, ni ban isa ba, mahaifinki ma bai isa ba. To shi ke nan ba aure ba, sai ki tattara ki tafi, miji ko!? To ya xauke ki, ku tafi, ki ji in gaya miki da aurenki ko cokali ban saya ba, da sunan aurenki.*

Tun daga wannan rana aka qara quntata wa Alawiyya, a kan abin da ake mata da, ba su yi mata ko da magana, sai dai harara.

Fim xin *Murjanatu Yar Baba* (2009, Nagoma Production, Kano) shi ma ya nuna yadda matar uba ke nuna tsana da qiyayya ga 'yar miji, kamar yadda ya faru ga Murjanatu 'yar Asma'u. Tun Murjantu na jaririya Magajiya ke faman nuna mata tsana. Wata rana Magajiya ta fito da barkono za ta zuba a hancin Murjanatu, sai Malam ya gan ta. Ana cikin wannan hali ne Allah ya yi wa Asma'u rasuwa, Murjanatu na da wata biyu a duniya. Bayan sadakar bakwai sai Magajiya ta ce Malam ya xauki Murjanatu ya kai ta gidan raino domin tana damun su da kuka. Murjantu na da shekara tara ne, shi ma Malam ya rasu, don haka sai ya kasance gida daga Magajiya sai Murjanatu, nan fa Magajiya ta dinga cin karenta ba babbaka da azabtar da Murajanatu azaba iri-iri, da tsana har ma da baqin ciki kan abin da Murjanatu ta gada. Da ta ga wannan bai yi mata ba sai kuma ta koma xora mata tallar goro, makaranta kuwa ta hana ta zuwa. Dubi wajen da ta ba ta kai niqa, Murjanatu ta yi tuntuve niqan ya xan zube, jikin Murjanatu na rawa tana kuka ta shigo gidan amma duk da haka, sai da ta zage ta tsab, ta yi mata dukan tsiya, tana faxin:

Magajiya: *Shegiya mucuciya, munafuka, da ni kike wasa, za ki ga abin da zai same ki idan ba ki qwarara jikinki, kin yi biyayya a wajena ba, wallahi za ki sha wahala, 'yar banza jiki duk qashi.*

Saboda irin quntatawar da Magajiya ke yi wa Murjanatu, har sai da ta sa ta gudu ta bar gidan. Allah Ya haxa ta da wasu Fulani a dajin wani qauye mai suna Kurkujal, ta sami lokaci mai xan tsawo tare da su, har suka fara sabawa, amma daga baya aka sami akasi, yayin da suka tashi suka neme ta suka rasa. Hakan shi ya sa Murjanatu ta ci gaba, inda ta je wani qauye mai suna 'Gargaje' a galabaice, tana gararamba a titi. Ta shiga matsanancin hali na tausayi da rashin sanin inda za ta, ana haka Allah ya haxa ta da Murjanatu yar mai shayi take gaya mata cewa,

Maryam ta: *Ni [illegible] je in ci abinci.*

A nan ne Maryam ta kai ta gidansu, Baban Maryam ya tambayi Murjanatu daga ina ta fito, take yawo haka, sai ta ba shi amsa da cewa;

Murjanatu: *Ni uwata ta mutu, ubana ya mutu, ba na jin daxin zama a gidanmu saboda duka na da kishiyar Babata take yi.*

Haka dai Magajiya ta yi sanadiyyar shigar Murjanatu duniya, sauran kayan gadon nata ta qarasa cinye su.

Fim xin *Qarshen Makirci* (2000, Ibrahimawa Production, Kano), shi ma fim ne da ya nuna irin wannan nau'i na hassada da matan uba kan yi ga 'ya'yan mijinsu, domin Sadiya ta sha wahala wajen matar babanta Hajiya Asma'u, bayan ta sa Alhaji ya saki mahaifiyarta Hajiya Zainab. Hajiya Asma'u ta dinga azabtar da Sadiya ta hana ta sakewa, inda ta mai da ita tamkar baiwa a cikin gidan, domin duk wani aikin wahala Sadiya ke yin sa a gidan. Sadiya ke wanke kwanukan abinci, ita take wankin kayan su Hajiya da Zara'u, ita ce goge-gogen teburin cin abinci, da wankin banxaki. Haka sharar gida baki xaya ita ce. Ga masu aiki amma ba za a sa su ba, sai dai Sadiya. Kullum Sadiya a tsaye take tana aiki babu hutu. Domin ko yaya ta tsaya za ta ji mari a fuskarta. Ita kuwa Zara'u 'yarta tana zaune cikin gida ba ta yin komai. Sannan zagi da duka da cin mutunci, da yankan qauna ba su bar ta ba. Tsangwama dai iri-iri Sadiya na shan ta. Ko makaranta Sadiya ba ta zuwa, sai dai 'yar lelen gidan Zara'u ita ke zuwa makaranta. Abinci kuwa qarshen kwasa ne rabonta, kuma ba za a ba wanda za ta qoshi ba, kamar yadda masu iya magana ke cewa, "rabon akuya tsari, farau-farau sai mai gata".

Duk da wannan azabar kuma Hajiya Asma'u ba ta daina neman magani kan ta raba Sadiya da mahaifinta ba. Kullum mahaifiyar Hajiya Asma'u na hanyar gidan boka karvo guru da layu da yin yanke-yanke, don a raba Sadiya da Alhaji. Ta hana Alhaji ya yi wa Sadiya abin arziki. Har ya zamanto ko kallon Sadiya Alhaji ba ya yi.

## 4. 3. Auren Dole

A addinin Musulunci, aure na nufin xaura aure tsakanin mace da namiji, ta yadda zai halatta gare su, su kaxaice da juna, su biya buqatar jin daxi na mutuntaka a tsakaninsu, ta hanyar da shari'a ta tsara musu. Sannan aure na nufin zama tare tsakanin mace da namiji wanda akan yi tare da yarjejeniyar ma'aurata da waliyansu da shaidu namiji yakan biya wata dukiyar aure kafin auren ya tabbata (Ibrahim, 1982 :162). Haka kuma aure na nufin wata yarjejeniya da ake cim ma tsakanin mace da namiji, wadda bayan waliyai sun amince kuma shaidu sun shaida take bai wa macen da namijin damar zama miji da mata, bisa wasu sharuxxa zayyanannu waxanda addinin Musulunci ya sharaxa su, waxanda suka haxa da sadaki da waliyai da shaidu, kafin tabbatar da aure.

Auren dole shi ne auren da yaro yakan ga yarinya ya ce yana son ta da aure, watau ko tana so ko ba ta so. Ko kuma a ba da yarinya ga wanda yake sa'an babanta ko kakanta, alhali kuma ita ba ta so. Ko a nema wa yaro yarinya da ba son ta yake ba saboda alaqa ta iyaye. Shi irin wannan auren ana yin sa ba da son ran xaya daga cikin ko duka ma'auratan ba, ana tilasta musu ne. Sai dai fa an fi yi wa mata. A al'adar Bahaushe iyaye suna aurar da 'ya'yansu da wuri. Su ne kan zava wa 'ya'yansu 'yan mata mazajen da suke son su aura. Wani Iokacin iyaye kan hango wata fa'ida wajen aurar da 'ya'yansu ga wanda suke ganin yana da kyakkyawan hali ko yana da gaskiya da riqon amana ko riqon addini da sauran halayen kirki. Wasu iyayen kuma, kan yi la'akari da mai hannu da shuni, ba tare da duba ko yana da halaye na kirki da zai iya riqe musu 'yar ba, abin da kawai suke duba shi ne abin hannunsa. Akasari irin wannan aure bai cika yin auren ba.

Duk auren da aka gina shi ta hanyar soyayya ya fi qarko da domin a nan ne za a fahimci wata magana da Hausawa kan ce, "so ganin laifi", idan kana son abu to komai muninsa, kyawunsa kake a harkar aure masoya biyu masu son junansu ba su cika ganin laifin junansu ba, ballatana aure ya gutsure. Amma idan akwai tabo game

da soyayyarsu ko ma babu soyayyar ma gaba xaya, auren kan iya samun tangarxa, wanda hakan kan sa yarinyar ta shiga wani hali na vacin rai da takaici da ban tausayi da aikata aikin da na sani, idan ma ba a yi sa a ba sai ya yi sanadiyyar fanxarewar yarinyar ta shiga uwa duniya, ita ba ga miji ba, ita kuma ba ga iyayenta ba. Wannan shi ne, "ba a ga tsuntsu, ba a ga tarko", "ina amfanin baxi ba rai".

Dubi iri abin da ya faru a fim xin *Gyale* (2004, Dararrafe Kano,) Tanko da Marka sun kasance masoyan juna, amma saboda da ke tsakanin iyayensu, Malam Jatau, mariqin Marka ya ce, ba zai Marka Tanko ba, maimakon haka ya yi iqirarin haxa ta aure da ma san ko waye ba. Wannan dalili na yunqurin yi wa Marka auren ta gudu ta bar gida. Tana ta gudu a daji ita kaxai, har ta gaji ta faxi a daji, ta kurkurje fuska, ga yunwa, da qishin ruwa, sai ta faxi ta kama cikin ciyayi. Tana cikin barcin ne, Allah ya kawo wani Malami ya zo wucewa ya gan ta, ya tashe ta ya ba ta ruwa, ta sha, ya kai ta sami kwanaki, ya yi mata nasiha ya ce, ta koma wajen iyayenta, kuma nausawa daji. Haka Marka ta ci gaba da rayuwa a dokar daji ga ga iska, ga namun daji ga qwari iri-iri, idan qwarin sun dame ta, sai ta sake waje. Tana cikin wannan hali ne, Allah ya kuma haxa ta da wani

saurayi, shi ma ya xauke ta ya kai ta gidansu, amma mahaifiyarsa ta qi yarda Marka ta zauna a gidan. Domin korar kare ta yi mata, har da duka da bulala.

Ka ga a nan "qilu ta ja bau" an hana ta auren wanda take so, ga shi ta bar gidan ta shiga duniya, ba a ma san inda take ba, ita kuma ta shiga wahala da takaici.

Mace a Musulunci na da 'yancin zaven mijin aure, musamman idan ta balaga. Yin auren dole ga mace bai dace da sunnar Manzon Allah (S.A.W.) ba, kamar yadda Hadisin Manzon Allah (S.A.W.) ya nuna:

> "Daga Abu Huraira (R.A.) daga Annabi (S.A.W.) ya ce, " Ba a aurar da bazawara har sai an nemi umarninta, kuma ba a aurar da budurwa, har sai an nemi izininta. Sai sahabbai suka ce, "ya Manzon Allah, yaya izininta yake"? Sai ya ce: "ta yi shiru" . Buhari da Muslimu suka ruwaito (Albassam 2003:849).

Lallai ne basar ma'aurata su ga juna kuma su amince da juna lokacin akan samu yarinya ta haqura ta auri wanda iyaye suka zava Amma kuma irin wannan auren gara babu da shi, domin yarinyar za qoqarin ganin ta yi duk wani abu da za ta vata wa mijin rai. Ba za ta kyautata masa ba, saboda a ganinta shi ma bai kyautata mata ba, tun

da ya aure ta ba tare da yardarta ba. Ita kuwa kyautatawa a aure na da muhimmancin gaske, saboda aure hanya ce ta samun Aljanna, ba za a sami Aljannar ba kuwa, sai an kyautata. Sakamakon rashin kyautata wa mijin matar kan haxu da fushin Ubangiji, da zai jefa ta cikin quncin rayuwa a nan duniya har ma da kiyama.

Don haka an yin tsokaci kan wannan matsala a fim xin *Ban Sani Ba* (2011,T.M.A. Production). Duk da cewa Rahma ta yi biyayya ga mahaifiyarta, ta yarda an yi aurensu da Alhaji Umar, ubangidan mahaifiyarta, kuma mutumin da Rahma ba ta so ko kaxan a rayuwarta, wannan bai hana Rahma ci masa mutunci da wulaqanta shi ba. Domin kuwa tun ranar da aka kai Rahma gidan Alhaji Umar take gwada masa rashin mutunci da wulaqanci da baqaqen maganganu, duk kuwa da irin kyautatawar da soyayyar da Alhaji Umar xin ke nuna mata. Sau da yawa takan gaya masa cewa, ita fa tana zaune don bin umarni mahaifiyarta, amma ba aure take ba. Sannan duk lokacin da ta ga dama kawai za ta fita ba tare da ta tambaye shi ba, idan ya tambaye ta ina ta je, sai ta ce ba a sani ba. Duk da cewa tana gidan Alhaji, amma ba ta fasa yi wa tsohon saurayinta Usman waya ba, kuma wani lokaci har sukan tsai da inda za su haxu don su yi hira, dubi irin abin da Rahma ke gaya wa Usman:

Rahma: *Ina da tabbabcin auren da na yi ba aure ba ne, kuma yana kan mutuwa, kuma ina da tabbabcin tsare maka kaina, har yanzu ba wani abin da ya canja daga yadda nake, kuma wallahi a budurwa zan fito.*

An xau tsawon wata biyu da auren Alhaji Umar da Rahma, amma har wannan lokaci Alhaji bai san ya yi amarya ba, har duqusawa Alhaji ya yi, ya roqi Rahma ta ba shi haxin kai, zai yi mata duk abin da take so amma ga abin da ta ce:

Rahma: *Tun da ka aure ni ba na son ka, saboda ka isa da mahaifiyata, zaluncinka ya sa ka kau da kai daga quncin da zan shiga, don kawai ka biya buqatarka, ai auren dole ba daidai ba ne wajen Ubangiji, don haka duk wanda ya yi shi, dole ya ga ba daidai ba. Ba abin da zai sa na haxa jikina da naka har abada.*

Alhaji: *Rahma ni abin da nake so ki ba ni haxin kai, na san yau na yi amarya, ni kuma na yi miki alqawarin duk abin da kike so zan yi miki, don Allah Rahma, kar na zautu.*

Rahma: *Da za ka zautu, farin ciki zan yi wallahi, kai kana can gidan mahaukata, ni kuma na tafi na auri wanda nake so. Wallahi*

*babu wani hali da za ka shiga na tausaya maka, ka sake ni kawai shi ne za ka sami kwanciyar hankali*

Wannan dalili na aura wa Rahma Alhaji Umar ba tare da tana son sa ba, ya jefa ta cikin fushin Ubangiji, saboda ta kasa yi masa biyayya yadda Ubangiji Ya yi umarni. Kullum tana cikin la'antar mala'iku da tsinuwarsu, hakan kuma ba zai sa ta yi farin ciki a rayuwarta ba.

Fim xin *Ladidin Baba* ( 2010, U.K. Entertainment, Kano) shi ma ya fito da irin wannan matsala ta auren dole. Ladidi ta kasance tana soyayya da saurayinta Xanladi, amma mahaifinta ya ce ba zai aura mata shi ba, saboda ba shi da qwaqqwarar sana'a, don haka ya aurar da ita ga wanda ba ta so, wato Bala. Tun da aka yi auren Ladidi da Bala, kullum tsakaninta da shi sai faxa da tashin hankali, dabi wata rana da rigima ta kaure tsakaninsu.

Bala *Ladidi [illegible] a gidan nan ba, idan har ba za ki biya min buqatata ba.*

Ladidi *Ni Ladidi babu wanda ya isa ya sami biyan buqata a wajena sai masoyina Xanladi, wa ya ce ka je ka auro wacce ta sallama zuciyarta ga waninka.*

Bala *Ladidi tafi gida*.

Ladidi *Ba zan tafi ba sai ka sake ni, don kuwa masoyina na nan na jiran dawowata.*

Bala dai ya saki Ladidi ta dawo gida, mahaifinta ya ce ta kuma fid da miji, amma ta kuma cewa ita idan ana so ta yi aure ta zauna sai dai a aura mata Xanladi, amma mahaifinta ya kuma cewa, shi ba zai aura mata Xanladi ba. Nan fa Ladidi ta kuma shiga wani qangi, kullum ba ta da aiki sai na kuka. Shi ma kuma Xanladi haka, don haka sai Ladidi da Xanladi suka haxa baki suka yanke shawarar su gudu su bar garin, haka kuwa aka yi, suka gudu birni, suka kama aiki gidan wani Alhaji mai kuxi. Ladidi tana ta aiki gidan Alhaji, har aka samu wata rana Alhaji ya haike wa Ladidi, tun daga lokacin ta fara laulayin ciki, daga qarshe dai ciki ya bayyana. Nan fa Ladidi da Xanladi sai kuka da kuka. Duk abin takaicin da ya faru a wannan fim xin auren dole shi ne ya haddasa shi.

**4. 4. Yaudarar Samari Ga 'Yammata**

Yaudara na nufin a cuci ko a ha'inci ko a zambaci wani. Hali na voye gaskiya da niyyar cuta ko zambatar wani (Qamusun Hausa 2006 : 480). Bargery, (1934) cewa ya yi yaudara na nufin, shammata ko zambata.

Wani lokacin akan sami saurayi ya yaudari budurwa. Saurayin kan zo da maganar aure ne, amma kuma a haqiqanin gaskiya ba auren ta zai yi ba. Irin waxannan samari sun fi iya maganganu irin na qarya da yaudara, waxanda kan ja hankalin ‘yammata, sai mutum ya natsu zai gane cewa duk yaudara ce. Saboda daxaxan zantukansu na yaudara sukan sami karvuwa gun ‘yammatan, idan akwai wasu samari sai yarinya duk ta kore su, ta kama shi. Sai tafiya ta yi nisa, yarinya ta sakankance zai aure ta, sai ya fara nuna mata wasu halaye na daban, waxanda idan auren ta zai yi da gaske, bai kamata ya nuna mata su ba, idan yarinya kintsattsiya ce mai kamun kai tun a wannan lokacin za su rabu, shi ke nan ya cuce ta ya yaudare ta ya raba ta da samarinta masu yi mata son gaskiya. Idan kuma aka samu ballagaza sai ta biye masa ya kai ta ya baro, idan abin ya yi muni har ya yi mata ciki. Idan kuma aka ce ya fito a yi aure ya ce bai san zancen ba. Wasu kuma auren za su yi amma sai su dinga yin qarya, ba za su faxi gaskiya a abin da ganin ya wadata su da shi, sai mata sa je gidan wata tarar zaman aka ba yaudari ‘yammata, da daxin zance da har su kai su su baro. Irin haka ta faru ga Jamila, inda Faruk ya Jamila na da saurayinta xan mutunci ta kore shi, ta kama Faruk, ashe

Fim xin *Walaski* (2009, Na Allah Motion Pictures, Kano) ya nuna ta je gidan wanan tarar zaman aka ba ya.

xan yaudara ne, ba aure zai yi ba. Sai dai ya zo ya xauke ta su tafi suna gidan fati gobe suna gidan rawa. Haka suka sha holewarsu, har yi mata ciki. Amma da Jamila ta sami Faruk ta gaya masa ga halin da ciki,. Nan da nan ya murtuke fuska:

Faruk: *Ni ba ruwana, ciki ai naki ne, tun da a jikinki yake, kuma ni yanzu lokacin da za mu yi hannun riga ya zo, tun da abin karva ya qare, kar ki kuma yi min ko da waya, daga yau ma zan canza layi, babu ni babu ke, (ya yi ficewarsa ya bar ta nan)*

Jamila ta fashe da kuka, ta rasa yadda za ta yi da ciki. Ta shiga gida, da ma tuni matar yayanta ta fahimci halin da take ciki, tun da ta ga tana ta amaye-amaye. Don haka ta sanar da yayanta abin da ga Jamila ya faru Shi kuma da jin wannan zance bai yi wata-wata ba, ya samobulala ya fara zabgar ta, yana faxin, ta janyo musu abin kunya, faxi wanda sai ta yai mata. Ta faxa, amma ko da aka je neman Faruk tuni ya bar garin. Haka rayuwar Jamila ta yi mata qunci.

*Gaskiya ta yi Halinta* (1999, Xandago Production,Kano), an nuna Hamisu ya yaudari Ramatu. Duk da cewa shi auren ta zai yi, amma yi mata qaryar cewa, shi mai hali ne. Alhali ba haka ba ne. Tun farko Ramatu na da saurayinta wanda suka daxe tare, sun shaqu da juna.

rana tsaka Hamisu xan qarya ya yi kutu-kutun da ya raba su. Hamisu dinga shirya wa Ramatu qarya, da cewa shi mai hali ne. Yana da Idan kuwa za shi zance haka zai cava kwalliya, ya sami kaya masu saka, ya saka takalma masu tsada, agogonsa ma abin kallo ne. turaren da zai fesa, ko ya bar wurin da awa xaya qanshin turaren ba ba. Har akwai ranar da ya yi shigar kayan satauta. Idan kuwa zai yi kyauta, sai ya nuna bajinta, yadda kowa zai yaba kyautar. Haka dai tsakanin Hamisu da Ramatu suke ta tafiya, har magana ta yi girma. aure.

Da Ramatu ta je gidan sai ta sami savanin abin da ya gaya mata kafin auren. Gidan da suke ciki ma na haya ne, ga bashi ya kanannaxe shi iya wuya, ga babu abinci. Ashe ma ba shi da aikin yi. Duk hidimar da dinga yi mata bashi yake karvowa. Kayan da yake zuwa zance ma da su na aro ne. Duk dai al'amarin nasa qarya ce da yaudara. Ita kuwa Ramatu ta ce, ai ba haka ya gaya mata ba, don haka ba ta san wannan zance ba. Aure bai daxe ba aka yi ta tafka rigima. Yau idan ta yi yaji an mai da ita, gobe ma kuma fitowa za ta yi. Babu abinci, haka Ramatu ta sha fama da qunci ta takaici, daga qarshe auren bai daxe ba suka rabu. Ya mai da ita qaramar bazawara.

*Fim xin Safara 2* (2010, Asfam Investment Ltd, Kano), fim ne da ya fito da yadda ake yaudara qarara. Yaudara ta taka muhimmiyar rawa, domin duk abin da ya faru a fim xin ya wanzu ne ta sanadiyyar yaudara. Khalisa tana da saurayinta da suka yi alqawarin yin aure idan ya kammala karatunsa na likita, amma lokaci xaya Jawal ya zo ya yaudare ta da abin duniya da qarya, na cewa idan suka yi aure za su Dubai, za su zaga qasashen duniya. Sannan da abokinsa Ahmad shi ma yana da budurwarsa Indo, suna son yin aure, domin suna son juna matuqa. Amma kuma shi ba shi da halin yin aure saboda ba shi da aikin yi. Ita ma kuma Indo mahaifinta ya rasu, mahaifiyarta kuma tsohuwa ce, ba ta da kuxin kayan xaki. Saboda wannan dalili Jawal ya ce da Ahmad zai biya masa kuxin jirgi su tafi Dubai, idan sun je zai samar masa aiki, don ya sami kuxin da zai yi aure. Har ya qara da cewa, ita ma Indo idan mahaifiyarta za ta yarda sai su tafi tare ta sami kuxin kayan gado. Ahmad ya yarda da wannan shawara, suka je suka sami mahaifiyar Indo, ita ma ta amince, ta ba su amanar Indo. Ta vangaren Khalisa ma Jawal ya kashe mata kuxi aka yi aure, ta tare Amma da suka isa Dubai sai Jawal ya xauki Khalisa matarsa ya ce, zai kai su gidan sarauta aiki. Shi kuwa Ahmad kullum yana

ya yi masa maganar aiki sai ya ce yana bincikawa. Idan kuma ya shi ina su Indo sai ya ce suna gidan aiki, ya qi kuma ya kai shi gidan ba a zuwa gidan sarauta. Ashe dai ba gidan aiki ya kai su ba, ya otel ne inda maza za su dinga zuwa ana lalata da su, shi kuma ana kuxin. Tun ranar da suka sauka a gidan wata mata ta karve su ta abinci mai kyau, ta shirya su, jimawa kaxan sai ga maza sun zo ce su shiga. Da suka ga suna neman tava su, sai suka fara kuka yarda. Nan fa matar ta yi wa Jawal waya, ya zo ya kama su da zagi duka, kan cewa ai shi don abin da ya kawo su ke nan ba don komai Kowace ta fashe da kuka, Khalisa matarsa na faxin:

Khalisa: *Da ma don ka yi amfani da ni ka sami kuxi ka aure ni, don ka haxi ni da mazan banza, ina matarka ta sunna, wallahi ka cuce ni, da ma ba son gasikya kake mini ba.*

Amma duk da haka, bai fasa ba sai ma ya kama dariya yana dai neman kuxi yake yi duk dukiyar da ya kashe mata ai ba a banza don ya san zai mai da kuxinsa ne. Shi kuwa Ahmad hankalinsa ya yi matuqar xagawa domin ya fara fahimtar cewa, lallai Jawal ba shi da Shi kullum sai ya kulle shi a gida shi kuma ya fice , sannan ya qi ya gun su Indo. Suna cikin wannan halin ne wata rana Ahmad ya gaya

cewa, zai haxa shi da hukuma idan har bai nuna masa inda su Indo Sai da ya kai shi gun hukuma sannan aka fito da su, aka dawo da su Nijeriya suna cike da baqin-ciki da takaicin abin da Jawal ya aikata

**4. 5. Kammalawa**

Kamar yadda aka gani a wannan babi, an yi tsokaci ne kan abubuwan da kan haddasa wa yaran mata shiga qunci da takaici a rayuwa. An yi nazari kan muhimman abubuwa guda huxu da suka haxa da yadda mata kan jefa kansu cikin takaici saboda kwaxayi da son abin duniya, da kuma irin yadda matan uba kan addabi 'ya'yan da ba nasu ba, sai kuma irin halin da yaran matan kan shiga a sakamakon auren dole da, kuma yadda maza kan yaudari mata su jefa su cikin halin qaqa-nika-yi.

## BABI NA BIYAR : NAXEWA

### 5. 0. Gabatarwa

A babin da ya gabata an ga abubuwan da ke jefa yaran mata cikin qunci har ya sa su takaici. Wannan babi wanda kuma shi ne na qarshe na wannan aiki, ya qunshi kammalawa wato taqaitaccen bayanin abubuwan da binciken ya gano da shawarwari da suka danganci masu kallon fina-finan da kuma masu shirya su. Sai manazartar da wannan bincike ya harhaxo bayanansa, har ya cim ma manufarsa. Sai kuma sunayen fina-finan da binciken ya yi aiki a kansu. A qarshe kuma aka kawo ratayen wasu kamfanonin fina-finan Hausa.

### 5.1. Kammalawa

Bahaushe kan ce 'komai nisan dare, gari zai waye'. Da wannan bincike mai suna 'Takaicin Mata a Fina-Finan Hausa' ya An dai gudanar da wannan bincike ne kan abubuwan da ke sa mata takaici da jefa su cikin quncin rayuwa. Binciken ya waiwayi ayyukan da suka gabata a kan fina-finan Hausa da kuma waxanda suka shafi rayuwar mata, wato ayyukan da aka yi a kansu ko waxanda suka yi.

A nan binciken ya gano cewa ayyukan da aka yi na binciken-bincike da nazarce-nazarce a waxannan fannoni ba su da yawa. Har ma a iya bugar qirji a ce babu wani takamaiman aikin da aka gudanar wanda ya xauki fina-finan Hausa ya fito da takaicin mata daga cikinsu. Don haka, wannan aiki shi ne irinsa na farko a wannan fanni. Sai dai ko a ce aikin Nafisa (2002) da ta yi a a kan mata a fina-finan Hausa, wanda shi ma ba abin da ya dami mata ta nazarta ba, ta nazarci rayuwar matan fina-finan Hausa ne, irin su Hauwa Ali Dodo Halima Adam da Amina Garba da kuma irin fina-finan da suka fito

Duk dai a wannan babi an kalli irin yadda marubuta daba-daban suka bayyana matsayin mata a lokutan tarihi masu tsawo. Marubuta irin su Mary Wallstonecraft da Simone De Beauvior da Virginia Woolf sun fito da yadda matsayin mace yake a wancan kokacin. Don qara tabbatar da hakan, sai aka dubi matsayin mace a wajen al’ummu da addinai daban-daban kafin zuwan addinin Musulunci wato lokacin jahiliyya, inda a qasashen Larabawa da addinin Hindu ake binne mace da ranta, da kuma qona ta idan mijinta ya mutu, saboda al’ada da kuma jahilci. Da kuma yadda sauran al’ummu na duniya suka xauki mace da qasqanci. Addinin Musulunci

wanda shi ne ya fara ceto mata daga qangin da suke ciki, ya xaga darajarsu a idon duniya, ya nuna cewa, su ma mutane ne kamar takwarorinsu maza, sannan ya ba su damar a dama da su a fagen ilimi da cinikayya da siyasa da sauran mu'amaloli. Haka kuma an dubi matsayin mata a fagen ilimi da siyasa da tattalin arziki da zamantakewa a wannan zamani. Da kuma irin matsayin da masu shirya fim suka ba mata tun a farkon lokaci zuwa yau, inda za a iya cewa da-dama-dama sarki a kan jaki, domin kuwa duk da irin da matan ke bayarwa wajen shirin fina-finai, a mafi yawancin lokuta a fito da su a matsayin qasqantattu, tare da bayyana su da munanan suka haxa da bin bokaye da malaman tsibbu da kishi da rashin kunya da sauransu. Alhali kuwa ba matan ne kaxai ke da waxannan xabi'u ba.

Kafin nan, sai da aka yi xan tsokaci kan al'amarin jinsi, wanda yanzu shi yake tashe a ko'ina cikin duniya, tashen kuwa ya haxa da siyasa da na tattalin arziki da na yanayin zamantakewa da ilimi da Inda aka bayyana cewa, matsalar wariyar jinsi ta wanzu ne a sanadiyyar ra'ayi ko aqidar nan ta cewa, akwai bambancin fifiko tsakanin namiji da mace a cikin al'umma. Sannan aka kawo tarihin

gwagwarmayar mata masu neman dai-daiton ‘yanci tsakanin maza da mata, wato  mata masu ra’in matantaka. Aka kuma kawo tarihin samuwar fina-finan Hausa.

A cikin aikin an kawo taqaitaccen bayani dangane da ma’anar takaici da kuma nau’o’insa. Sannan aka zo da bayani kan abubuwan da ke haddasa wa mata takaici. An kasa abubuwan gida biyu don sauqin bayani, inda aka fara kawo na vangaren manyan mata a zamantakewar iyali, wanda ya haxa da zamantakewar miji da mata da kishi tsakanin kishiyoyi da  tsakanin  uwar miji da suruka da kuma tsakanin faccaloli. Sai kuma aka nuna yadda rashin haihuwa da haihuwar ‘ya’ya mata kan sa mata takaici, sannan a qarqashin kowane batu aka kawo misalan fina-finai aqalla uku-uku.  Daga xaya vangaren  kuma an xauki  batutuwa guda huxu, kamar yadda aka yi a farko, domin samun daidaito, waxanda suka haxa da kwaxayi da son abin duniya da quncin rayuwa daga matan uba da auren dole da kuma yadda ake haxar ga ‘ya’yan mata. Bayan an harhaxa bayanan, bincike ya gano cewa a yanzu haka, nasarori fiye da yadda ake tsammani ta fuskar fina-finai. Kowa ya san vangare mafi wahalarwa da aka fi samun matsala shi ne zamantakewa, musamman ma a tsakanin iyali. To a yau an sami

tallafi daga fina-finai daban-dabam da suka sa mutane da dama suka gyara kuskurensu, wasu kuma suka fahimci abubuwa da yawa suka kuma yi nadama. Misali fim xin *Adabiyya* da *Murjanatu 'yar Baba* da *Kishiya ta* da sauransu, sun taimaka gaya a wannan vangare.

Za a iya fahimtar taimako da tallafi da fina-finan Hausa suka bayar musamman ta irin yadda mutane musamman maza suke yabawa da wasu fina-finan. Wasu sukan ce fim kaza ya sa na fahimci yadda zan zauna da matata da kyautata mata, kamar irin su *Jan hali* da *Adabiyya* da *Aure Dodon mata*. Haka kuma matsalar uwar miji tana nan tana wanzuwa a tsakanin al'umma ba ma ta Hausawa kawai ba, fina-finan sun yi qoqari wajen nuna wa mutane wannan babbar matsala domin a sami mafita ta hanyar yin taka tsantsan da iyayen miji. Fina-finai irin su *Uwar miji* da *Darasi* da *Aljannar Mace* da sauransu sun fito da hakan. Kuma ta vangaren yadda shi kansa miji zai tarairayi uwarsa, ya yi haquri da duk irin abin da za ta yi masa shi da matarsa mai kyau da marar kyau , kamar *Umarnin Uwa*. Haka kuma wasu matan sukan koyi yadda za su zauna da kishiya da yin haquri da duk irin makirce-makircen ta saboda ganin waxannan fina-finai, kamar yadda ya faru a fim xin *Mace ta gari* .

Haka kuma an gano cewa fina-finai kan fito da abubuwa tamkar a rayuwa ta zahiri suna kwaikwayon masu irin waxannan halaye, wasu a zahiri al'amarin ya tava faruwa, amma wani qirqirar matsalar kawai ake yi domin a nusar da masu irinta. Kuma a haqiqa sai a ci nasarar manufar da ta sa aka yi wannan shiri. Misali, fim xin *Kishiyata*, duk abin da aka bayyana a fim xin ya faru da gaske, domin matar da ta fito a matsayin Talatu ita ta je wajen malami don neman fatawa kan cewa, ta ziyarci Xakin Allah, amma ta kasa ganin Ka'aba, an nuna mata, an xora hannunta a kan Xakin, amma ba ta ji shi ba. Don haka sai ya tambaye ta cewa, ko ta tava aikata wani savo ne? Shi ne take bayar da labarinta, sai masu shirin fim suka shirya fim a kansa.

Haka kuma idan muka xauki fim xin *Mata Ko Baiwa*, za mu ga cewa, matar da ta fito a Aisha ta jure wasu wahalhalu da wulaqace-wulaqance na namiji da kishiya, amma daga qarshe ta sami nasara a rayuwa. Haka kuma akwai matsaloli kan auren dole da iyaye ke yi wa 'ya'yansu ga Alhazan birni kamar yadda ya faru a fim xin *Ban Sani Ba*, waxanda 'ya'ya ba sa so. Wanda haka kan haifar da gagarumar Waxannan suna cikin matsalolin da suke addabar al'ummar

Hausawa. Kuma fina-fina nan suna bin diddigi domin gano da kuma fito da yadda za a magance irin waxannan matsaloli da kuma abubuwan da suke haddasa su domin nuna wa jama'a kuma suna iya qoqarinsu wajen cim ma manufarsu da kuma isar da saqon da suke nufi ga jama'a. Kuma Alhamdu lillah ana samun waraka da dama ta fuskar fina-finan. Sannan kuma sun fito a daidai lokacin da jama'a suke buqatarsu.

Akasin yadda mafi yawancin mutane ke kallon fina-finan Hausa a matsayin ba su xauke da komai sai al'amuran soyayya da gurvata rayuwar matasa, binciken ya gano fina-finan Hausa kamar sauran sassan adabin Hausa, su ma suna taimakawa wajen faxakarwa da son ci gaban al'umma, domin sun kasance suna yin gargaxi da hannunka-mai-sanda kan wasu al'amuran rayuwa masu muhimmanci, musamman waxanda suka shafi mata. Sannan suna yin abin da Bahaushe ke kira 'gyara kayanka' kan wasu abubuwa ko halaye munana da wasu suke aikatawa, sukan xauke su su yi shirin fim don a nuna wa jama'a, don su farga su san illolinsu su kuma gyara.Wani abin da binciken ya gano kuma shi ne ba fina-finan da bincike ya kawo kaxai ke xauke da muhimman abubuwa na

akwai fina-finai da dama da suke xauke da abubuwa muhimmai da suka shafi rayuwar jama'a.

Har ila yau, an gano cewa, kusan dukkan jigogin da ake iya samu a sauran sassan adabi kamar waqa da zube da wasan kwaikwayo a fina-finan Hausa ma za a iya samun su. Wato kamar jigon siyasa da tarbiyya da faxakarwa da gargaxi da kiwon lafiya da ilimi da sauransu. Don haka ya rage ga manazarta da su shiga kogin fina-finan Hausa don tsamo irin albarkatun da ke ciki.

A nan ne nake fatan manazarta za su ci gaba da yin bincike a kan al'amuran mata domin cikasa givin da wannan bincike ya bari, don amfanin al'umma a yau da gobe. Sannan su ma fina-finan Hausa ba abubuwan yasarwa ba ne, akwai manufa, akwai darasi a cikinsu, Hausawa dai na cewa, 'sai an gwada akan san na qwarai'.

## 5. 2. Shawarwari

Da farko zan fara ba masu shirya fina-finan Hausa shawara qara yin hovvasa kan qara shirya fina-finai masa ma'ana waxanda za amfani wannan al'umma da ma masu zuwa nan gaba, sannan su zama masu kishin kai da kishin al'adun Hausawa. Haka kuma ga su

masu kallon fina-finan ya kamata su rinqa amfani da irin gargaxin da suke gani a fina-finan ba wai kawai su xauke su a matsayin abububwan nishaxi ba da xebe kewa.

Qalubale gare ku mata, duk fa irin waxannan abubuwa da aka nuna a fina-finanan haka fa suke kasancewa a rayuwa ta zahiri. Don haka fina-finan su zame mana madubi na cewa duk abin da muke gudanarwa tsakaninmu da abokan zamanmu ko kishiya ko uwar miji ko suruka ko faccala ko 'ya'yan miji da sauransu, al'umma fa na kallon mu, kuma tun daga nan duniya asirin mutum zai fara tonuwa kafin a je ga Ubangijin halitta, kamar yadda muka gani a wasu fina-finan. Don haka mata mu gyara halayyarmu, mu tausaya wa duk wanda Allah Ya haxa mu zama da shi, mu riqe shi da amana. Domin sai ka tausaya wa wani Allah zai tausaya maka, kuma Hausawa na cewa, 'alhaki kwikwiyo', kuma 'abin da ka shuka shi za ka girba'.

Haka su ma maza magidanta, waxanda aka tavo irin halayyarsu a cikin waxannan fina-finai, ina ba su shawara da su ji tsoron Allah su gyara, su ba mata duk haqqin da shari'a ta ce a ba su. Su girmama su domin su ma 'yan'Adam ne, kuma Allah (S.W.T.) Ya ce a cikin suratu Isra'il aya ta 70:

> “ Kuma lalle ne, Mun girmama ‘yan’Adam, kuma Muka xauke su a cikin qasa da teku, kuma Muka arzurta su daga abubuwa masu daxi, kuma Muka fifita su a kan masu yawa daga waxanda Muka halitta, fifitawa”.

Haka kuma irin amfanin da mace ke da shi wajen miji da al’umma ma gaba xaya, ba zai misaltu ba, don haka ita ma a kyautata mata ko a sami ci gaban al’umma gaba Allah.

Allah Ya sa wa wannan aiki albarka, Ya sa kuma ya zama mai amfani ga al’umma. Amin.

## MANAZARTA


Abbas, A. A. (2008) 'Sassarquwar Adabi Cikin Adabi : Nazarin Adon Harshe a Waqoqin Fina-Finan Hausa'. Kundin Digiri na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

Abdul-Ganiy, A. (2008) 'Muslim Women: The Epitome of Reformation' Muqalar da aka Gabatar a Taron Qungiyar Xalibai Musulmai Mata ta Nijeriya, a Gombe.

Abdullahi, M. (2002) 'Bambance-Bambancen da ke Tsakanin Wasan Kwaikwayo na Gargajiya da Kuma Fina-Finan Zamani: Nazari Kan Jigo'. Kundin Digirin Farko. Kano: Jami'ar Bayero.

Abdulmumini, S. A. (1993) 'Understanding **Violation of Women Human Rights in Selected Hausa Plays:** ***Uwar Gulma and Ai Ga Irinta Nan*'** **by U.D.Katsina'** Muqalar da aka Gabatar a Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya da Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

AbdulWahid, T. F. (1972) 'The Role of Women as Portrayed in Hausa Drama'. Kundin Digirin Farko. Kano: Jami'ar Bayero.

Adamu, A. U. (2004). 'Passage to India, Media and Construction of African Identities'. Essay Report of a Seminar. Nairobi, Kenya.

Adamu, M. T. (1998) *Asalin Magungunan Hausawa da Ire-Irensu*. Kano: Xan Sarkin Kura Publishers Ltd.

Adamu, N. M. (2002) ‘Mata Cikin Fina-Finan Hausa’. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami’ar Bayero.

Ahmad, A. (2003) ‘Fina-Finan Hausa da Matsalolinsu ga Jama’a ta Fuskar Al’ada da Hanyoyin Magance su’. Kundin Digiri na Xaya. Kano: Jami’ar Bayero.

Al bassam, A. (2003) *Bulugul Maram Min Taudihul Ahkam*. Makkah: Maktabul Asad

Alfred, E. O. and Opular, O. E. (1977). *The Development and Growth of the Film Industry in Nigeria*. Lagos: Third Press International.

Aliyu, I. A. (1982) *Matsayin Mata da Rayuwar Aure a Musulunci* Kano: Bureau For Islamic Education.

Al-Kanawy, A. S. (2004). ‘Fina-finan Hausa: Faxakarwa ko Shagaltarwa? ‘Takardar da aka Gabatar a Mujallar Hausa Home Video Technology, Economy and Society. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Al-Sheha, A. (1997) *Women in the Shade of Islam* . Riyadh: Printed in the Expense of As’ad Hashim.

Aminu, H. (1986) ‘Women’s Language in Cultural Context: A Case Study of Hausa Women of Katsina’. Kundin Digirin Farko.

Kano: Jami'ar Bayero.

Ar-razi, M. (ba shekarar bugu) *Muktaru Al-Sihahi*. Syriya: Mu'asasatul Darul-Ulumi Lil Hikhmatu Al-Kitabul Islam.

Badamasiyu, J.B.(1998) *Status and Role of Women under the Shari'ah.* Kaduna: Zakari Publishing Company Ltd.

Balla, Z. Y. (1972). 'Comparing *'Uwar Gulma' with 'Tabarmar Kunya'*. Kundin Digirin Farko. Kano: Jami'ar Bayero.

**Baqo, H. (2003) 'Fina-Finan Hausa na Bidiyo da** Gurbacewar Al'adun **Aure'. Kundin Digiri na Xaya. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello**.

Bakura, A. R. (2003). 'Gurbin Kishi a Adabin Hausa:Tsokaci kan Zube da Waqoqin Baka'. Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Bargery, G.P. (1934) *A Hausa-English Dictionary and English-Hausa Vocabulary.* London: Oxford University Press.

Bugaje, H. M. (2011) 'Wa'azi a Rubutattun Waqoqin Mata na Qarni na Ashirin'. Kundin Digiri na Biyu. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello

Bunza, A. M. (2002) 'Nazarin Al'adun da ke Cikin Kaset-Kaset na Hausa da Littattafan Zamani' Muqalar da aka Gabatar a Taron Qarawa Juna Sani: Sabon Salon Tafiyar Adabin Hausa. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Chamo, I. Y. (2005). 'Saqo a Fina-Finan Hausa: Nazari a kan Jigo da Rabe-Rabensa'. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Chamo, I .Y.(2002) 'Tasirin Al'dun Turawa a Cikin Fina-Finan Hausa'. Kundin Digiri na Xaya. Kano: Jami'ar Bayero.

CSNL (2006) *Qamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Kano: Jami'ar Bayero.

Congleton, F. I. (1988) 'Some Problems of Girls Education in Northern Nigeria'. Oversea Education Communication.

Xangambo, A. (1984) *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmacinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano:Triumph Gidan Sa'adu Zungur.

Xan-Iya, I. A. (1989) *Mata Iyayen Giji*. Kano: Zed Press Nig. Ltd.

De Beauvior, S. *Second Sex* (1949) London: H. M. Parshley New York.

Dzarma, L. (1984) 'Muhimmancin Mata ga Tarbiyyar Yara'. Kundin Difloma. Maiduguri: Jami'ar Maiduguri.

Fafunwa, A.B. (1974) *History of Education in Nigeria*. NPS Education Publishers Ltd.

Galadima, U. S. (2001) 'Waqa a Fina-Finai' Garkuwa, Nuwamaba. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Gandu, I. M. (2006) 'Tasirin Fina-Finan Indiya a kan na Hausa'. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya, Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Garba, R. (1998) 'Nazarin Jinsi a Adabi: Tsokaci kan Matsayin Mace a

Rubututtun Wasannin Kwaikwayo na Hausa'. Kundin Digiri na Biyu. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Garba, R. (2009) 'Hoton Mata Cikin Fina-fFinan Hausa, Gyara Ko Varna?' Muqaklar da aka Gabatar a Taron Qara Wa Juna Sani Kan Fina-Finan Hausa. A Xakin Taro na Kongo, Zariya.

Gidan Dabino da Yakasai, A.A. (2004) 'Matsaloli da Nasarorin Masu Shirya Fina-Finan Hausa Musamman na Kano', a Cikin Adamu da Wasu. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Gumi, A. M. (1982) *Alqur'ani Mai Girma.* Tarjamar Ma'anonisa. Beirut, London: Dar al Arabiya.

**Gusau, S.M. (1991) ' Tsokaci kan Tushen Kalmar Adabi'. a Cikin Mujallar Bagaruwa. No 1 Vol 1 Kano: Qungiyar Hausa, Jami'ar Bayero.**

Gusau, S.M. (2011) *Adabin Hausa a Sauqaqe.* Kano: Century Research and Publishing Limited.

Hassan, B.Y. (2012) 'Kwatanta Salon Rubutun Bilkisu Ahmad Funtuwa da Bilkisu Yusuf Ali a Ma'aunin Harshe'. Kundin Digiri na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

Hausawa, M. H. (2010) 'Mutuncin Mata 'Yancinsu: Tsokaci kan Mace a Yau'. Muqalar da aka Gabatar a Taron Qara Wa Juna Sani Karo Na Biyar. Kano: Kwalejin Ililimi ta Tarayya.

Ibrahim, B. (2009) 'Gudummawar Mata ga Havaka Rubutaccen Adabi'. Kundin Digiri na Uku. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Ibrahim, M. S. (1982) 'Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa ta Gargajiya'. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Ibrahim, S. A. (1995) 'The Status of Women in Hausa Literature: A Focus on Hausa Plays'. Kundin Digiri na Biyu. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Ingawa, Z. S. (1994). 'Kishi Kumallon Mata: Nazarin Sigoginsa a Rayuwar Hausawa'. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Inuwa, U. A. (2000) 'Tarbiyya Cikin Fina-Finan Wasan Kwaikwayo na Hausa'. Kundin Digiri na biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Inuwa, U.A. (2008) 'Jigon Tarbiyya a Wasu Fina-Finan Hausa'. Muqalar da ke Cikin *Harsunan Nijeria*,Vol.xxi Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Inuwa, U.A. (2009) 'Kutsen Baqin Al'adu Cikin Fina-Finan Hausa'. Kundin Digiri na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

Jennifer, C. (1985) 'Language and Sexism in English Teaching'. Information Circular No 12.

Krings, M. (2005) ‘ Muslim Matyrs and Pagan Empire: Video Films and the propagation Of Religion In Northern, Nigeria.

Kwantagora, I. A. (1999) ‘Asirran Sammu a Idon Bahaushe’. A cikin Mujallar Hausa Studies, Vol.1 No1.Sakkwato: Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Larkin, B. (1995) ‘Modern Lovers: Indian Films, Hausa Drama and Love Novels Among Hausa Youths in Northern Nigeria’ Paper Presented to the African Association Meeting Orlando Florida.

Larkin, B. (2004) ‘*From Majigi to Hausa Home Video Films: Cinema and Society in Northern Nigeria*’. London: Oxford University Press Ltd.

Lemu, A. B. (2007) *New Junior Islamic Studies Book2.* Minna: IET Publications.

Louse, B. M. (1996) ‘Television Drama in Hausaland: The Search for a New Aesthetic and New Ethic’ .Critical Arts Journal, vol 10 Madison: University of Wisconsm.

Mack, B. B. (1992) ‘Women and Slavery in Northern Nigeria’, A Cikin Journal of Comparative Studies, Vol.No 1 Elizabet Sabage.

Mack, B. B. & Boyd, J. (2000). *One Woman Jihad.Nana Asma’u Scholar and Scribe*. Bloomington & Indianapolis: Indiana University

Press.

Mack, B. B. (2004) . *Muslim Women Sing Hausa Popular Song,* Bloomington and Indianapolis: Indiana University Press,

Mahdi, H. (2006) *Gender and Citizenship: Hausa Women's Political Identity from the Caliphate to the Protectorate*, (Goteborg): Oxford University.

Magaji, A. (1999). 'Kunya da Mutunta Mutane a Al'adar Bahaushe'. Muqalar da ke Cikin Mujallar Hausa Studies, No. 1. Kano: Jami'ar Bayero.

Mainasara, T. (2008) 'Karin Magana a Bakin Mata'. Kundin Digiri na Xaya. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Majma'ul Luggal Arabiyya (ba shekarar bugu) *Al- Mu'ujamul Wasid.* Juzu'i na 1: Al-Maktabatul Ilimiyya.

Mandawari, I. M. (2004) 'Tarihi da Tasirin Waqoqin Fina-Finan Hausa'. Takardar da aka Gabatar a Mujallar Hausa Home Video Technology Economy and Society. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Mohammed, R. (2011) 'Mata a Bakin Mawaqan Baka na Hausa'. Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Muhammad, A. H. (2008). *'Yancin Mata Daga Kitab Da Sunna.* Darul huda For Islamic Research.

Mungadi, A. M. (2000) . 'Bidiyon Kasuwar Kano:Tarsashin Tatsuniyoyin Hausa a Cikin Wasannin Kwaikwayo Na Bidiyo: Nazari Kan *'Daskin Da Rixi' Da 'Kogin Bagaja*' Kundin Digiri na Farko, Sashen Koyar Da Harsuna Nijeriya. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Nawawi, I. (1993) *Fassarar Riyadhus-salihin*. Baitul Hikmah. Kano: Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci Da Tarjama Da Buga Littattafai.

Remi, I. (2003) ' The Burden Of Gender : A Comparative Study of Bauchi Emecheta's Second Class Citizen and Zora Huston's Their Eyes Were Watching God'. Kundin Digiri na Uku. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Riley, N. E. (1997) 'Gender, Power And Population Change'. Population Bulletin, Population Bureau, Inc.

Wollstonecraft, M. (1792) http://www. Marxists. Org/ Reference/Subject/ Ethics/ Wallstonecraft/ Vixdication----.

Woolf, V. (1929) *A Room Of One's Own*. San Diego, New York London: Hoggarth Press.

Yahaya, I. Y. (1973) ' Tarihin Adabin Hausa: Ma'anar Adabi'. Maqala Wadda aka Gabatar. Kano: Jami'ar Bayero.

Yakasai, S. A. (2002) 'Waqoqi Cikin Wasannin Kaset-Kaset na Hausa da Littattafan Zamani, Gyara Ko Varna?' Muqalar da aka

Gabatar a Taron Qara wa Juna Sani. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Yakubu, A. (2006) 'Binciken Kalmomin Soyayya a Cikin Fina-Finan Hausa'. Babbar Difloma ta Gaba da Digirin Farko, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Yakubu, B. R. (2004) 'Gudummawar da Mata ke Bayarwa a Shirin Fina- Finan Hausa'. Muqalar da aka Gabatar a cikin Mujallar Hausa Home Video Technology, Economy and Society. Kano: Gidan Dabino Publishers.

**Hirarraki**

Hira da Hamisu Lamixo Iyan-Tama. Shugaban Kamfanin Iyan- Tama Multi Media. Ranar 30/ 2/2012

Shirin 'Inda Ranka' Gidan Radiyon Freedom, Kano. Ranar 25/6/2012 da qarfe 9. 30 na dare.

Hira da Furofesa Abdulqadir Xangambo. Sashen Nazarin Harsunan Nigeriya da Kimiyyar Harshe. Kano: Jami'ar Bayero. Ranar 15/6/2012.

Hira da Dr. Umma Ado Abbas. Sashen Nazarin Harsunan Nigeriya da Kimiyyar Harshe. Kano: Jami'ar Bayero. Ranar 15/6/2012.

Hira da Dr. Sadik Isa Raxxa, Sashen Ilimin Zamantakewa. Kano: Jami'ar Bayero. Ranar 15/6/2012.

Hira da Dr. Isa. Sashen Babbar Tiyata Kano: Asibitin Qwararru na Murtala Muhammad. Ranar 20/6/2010.

## SUNAYEN FINA-FINAN DA AKA YI AMFANI

| | | | |
|---|---|---|---|
| Aure Dodon Mata | 2009 | Sky Entertainment | Kano |
| Jan Hali | 2011 | Fasaha Media Concept | Kano |
| Adabiyya | 2010 | Nasara Globai Concept | Kano |
| Kishiya Ta | 2011 | 3SP International Ltd | Jos |
| Mata Ko Baiwa | 2011 | Royal Film Production | Kano |
| Mace Ta Gari | 1991 | Tumbin Giwa | Kano |
| Darasi | 2010 | Jhankar Digital Sound | Jos |
| Uwar Miji | 2009 | No Limit Concept | Jos |
| Umarnin Uwa | 2011 | T.M.A. | Kano |
| Aljannar Mace | 2000 | Tumbin Giwa | Kano |
| Faccala | 2010 | Unique Entertainment | Kano |
| Auwalu, Sani, Salisu | 2004 | I. U .I. Electronic | Kano |
| Hannunka Mai Sanda | 2011 | T.M. Production | Kano |
| Manda | 2005 | Dararrafe EnterPrises | Kano |
| Kumallon Mata | 2010 | 3Star Movies | Jos |
| Wakana | 2009 | Nagarta Motion Pictures | Kano |
| Laifin Daxi | 2011 | G.Top | Kano |

| | | | |
|---|---|---|---|
| Tagwayen Gida | 2010 | Nasara Global | Kano |
| Mujiya | 2004 | Madobi EnterPrises | Kano |
| Jari | 2009 | H. R. B. | Kaduna |
| Murjanatu 'Yar Baba | 2009 | Nagoma Production | Kano |
| Qarshen Makirci | 2000 | Ibrahimawa Production | Kano |
| Tsautsayin Takaba | 1999 | Dukku Production | Kano |
| 'Yammata | 1999 | Fine Focus Video Production | Kano |
| Butulci | 1999 | Xanfodio Production | Sokoto |
| Gyale | 2004 | Dararrafe EnterPrises | Kano |
| Ban Sani Ba | 2011 | T. M. A. Production | Kano |
| Ladidin Baba | 2010 | U. K. Entertainment | Kano |
| Zakara | 2008 | U. K. Entertainment | Kano |
| Safara | 2010 | Asfam Investment Ltd. | Kano |

**RATAYEN WASU KAMFANONIN SHIRYA FINA-FINAN HAUSA**

Accut Studio

A.B.U. Films Production

Al- Nasid Production

A.H.I. Entertainment

Auwal Trading Company

Almar Enterprises

Amag Movie Kano

Asfam Investment

Al- Mustapha Production

Always Ventures

Al’umma Production

Al-Bash Production

AMD Film Production

Aimah Production

Al-Rahuz Films

Amir Production

Aisha Film Production

Aisy Digital

Ayagi Production Kano

Amana Film Production Kano

Al’ihsan Film

Ashu Media

Amad Entertainment Maiduguri

A.Slal Film Kano

Asid Entertainment Kano

Aram Film Production

Ali Jita Music Studio Kano

Amge Video

Ammani Film Kano

Annur Film Production

Alfahari Film Production

Abdullahi Ventures

Bushara Production

Bright Star Entertainment

Bash Film Inc.

Boss Film Production Jos

Video Web

B.J. Movies

Basawa Film Kaduna

Bosho Film Production Kano

Boudou Film Production

B.K. Ventures Sudawa

Discovering FilmProduction

Dukku Production

Dararrafe Enterprises

D.Y. Entertainment

Xantata Motion Pictures

Xanfodio Film

Xandago Production

Dambazau E. Kano

Dhases A.S. Ltd

Dandurum M. Film Gombe

D.S.S Production

El-Duniya Production

El-Jamil Production

El-Haj Entertainment Kaduna

El-Hadis Enterprises

F.S.H. Production

FKD Production

F.LL Film Kano

Fatima Film Production Kano

Five Film Productin

Falalu Fim Big Time Kano

Five Star Film Production

Fatima Motion Picture Katsina

Fasaha Media Cocept Kano

Gidaje Film Production

Gamsco Ventures

G.Top Kano

Gwanja Enterprises

Godiya anda XanHassan Production

Gidan Dabino Production

Hasin Enterprises

Happy Entertainment

Hand K. Productin

H.R.M production

Ibrahimawa Production

Jaga World Production

Kajal Prdoductin

Kwabon Masoyi Production

Kainuwa Motion

Lerawa Films Kaduna

Mandawari Enterprises

Makoxa Film

Malam Qato Entertainment

Night Star Entertainment

Nagarta Motion Pictures

Royal Film Production Kano

Sarauniya Film Kano

T.M.A. Production

U.K. Entertainment

Unique Entertainment

3SP Star Pictures Jos

2 Effects Empire

Zik Entertainment

Zazzau Movie